# Kimiyya da Fasahar Auratayya



Muhammad Aminu Ibrahim Daurawa

# TAMBAYA KAN AURE 01

Da sunan Allah mai rahama mai jin ƙai. Salati da ɗaukaka da aminci marasa iyaka su tabbata bisa shugabanmu, jagoran mu Annabi Muhammadu sallallahu alihi wasallama, cikamakin Annabawa shugaban Manzannin wanda Allah ya aiko shi rahama ga talikai.

Haƙiƙa aure ya dace da halitta da ɗabi'a da yanayi na zamantakewar al'umma. Don haka ne za ka ga da addini da al'ada da hankali duka suna tabbatar da aure. Akwai abubuwa da dama waɗanda aure ya ƙunsa. Waɗanda suka ƙunshi rayuwar ɗan'adam da makomarsa, cigabansa, rayuwarsa ta duniya da kuma makomarsa ta lahira. Shi yasa Allah SWT a cikin Al'Kur'ani ya gaya mana cewa Annabawa, waɗanda a cikin sanfurin mutane sun fi kowa daraja, suma suna yin aure. A cikin suratul Ra'adi aya ta 38, Allah ta'ala ya ce…

Allah ta'ala ya ce "Haƙiƙa mun aika da Manzanni gabanin ka, kuma mun sanya musu mateku da zuriya."

Sannan a wata ayar Allah SWT cikin suratun Nur, aya ta 32, yake cewa…

"Ku aurar da waɗanda basu da aure daga cikin ku; zawarawa da 'yan mata, samari da gwagware; da kuma nagartattu daga cikin bayinku maza, da kuyangun ku mata."

A wani gurin, Suratul Nisa'i, aya ta 3, Allah Ta'ala yace…

Allah Ta'ala ya ce "Ku auri abinda ya daɗaɗa muku rai daga mata, biyu-biyu, uku-uku, huɗu-huɗu; idan kun ji tsoron ba za ku yi musu adalci ba (in kun yi biyu ko uku ko huɗu) ku wadatu da guda ɗaya, ko abinda damanku ta mallaka. Wannan shi ya fi kusa da ba za ku yi zalunci ba ko ba za ku iya ajiye iyalan da ba za ku iya ɗaukar nauyinsu ba"

Wani gurin Allah ta'ala ya ce…

"Yana daga cikin ayoyin Allah da ya halicci matanku daga gareku domin ku samu natsuwa da kwanciyar hankali da gamsuwa da su. Sannan ya sanya soyayya da rahama a tsakaninku. Haƙiƙa a cikin wannan akwai ayoyi tuli ga waɗanda suke da tuntuntuni." Wannan suratu Rum kenan, aya ta 21.

Waɗannan ayoyi 4 na Al-kur'ani da muka kawo suna zaburar da mu cewa aure sananne kuma tabbataccen abu ne mai asali; wanda yake a cikin addinin Musulunci da hankali da kuma al'ada ta zamantakewa.

Anas ɗan Malik (RA) ya rawaito hadisi dangane da ƙissar wasu mutane guda uku da kowannen su ya firgita da razana, yake kuma neman wani aiki da zai kusanta shi ga Allah; ya tsare shi ga barin halaka. Sai suka ce bari mu je mu tambayi matanen Manzon Allah (SAW) su gaya mana yadda yake aiwatar da ayyukan sa na ibada; domin mu yi koyi da shi. Da suka je suka tambaya aka gaya musu yadda Annabi (SAW) ya ke gudanar da ibadar sa, sai suka ga kamar ta yi musu kaɗan. Sai suka ce ina mu ina Manzon Allah (SAW). Shi dan bai yi ibada mai yawa ba ai ba damuwa domin shi an riga an masa gafara. Mu kuwa da ba a yi mana gafara ba bari mu je mu yankowa kanmu wata ibada da za mu riƙa yi domin mu kai lahira lafiya.

Ɗayan ya ce ni zan riƙa yin sallah duk dare har abada. Ma'ana kullum da daddare na daina barci sallah zan ta yi. Ɗayan kuma ya ce ni azumi zan riƙa yi kullu-yaumin, ba zan sha ruwa ba. Shi ibadar da ya ɗorawa kansa yake ga ita ce za ta fidda shi. Sai na uku ya ce ni kuma zan nisanci mata ba zan yi aure ba har abada-Wato yana ga kamar a cikin yin aure akwai koma baya na ɗaukar nauyin macen da kula da ita, shayar da ita, tufatar da ita da, kai ta asibiti, sai mata magani, bata ilmi da sauran su; wannan zai rage masa ƙwazo wajen neman lahira. Don haka shine ya ce shi ba zai yi aure ba.

To waɗannan mutanen 3, sune Annabi (SAW) ya ji labarin shawarar da suka yanke; cewa kowa zai ɗauki wani nau'i na ibada da kuma yadda za su gudanar da su. Sai Annabi (SAW) ya kira su, ya ce masu "kune kuka ce kaza da kaza?" Suka ce "eh", ya ce "to amma ina muku rantsuwa da Allah, nine na fi ku tsoron Allah, nine na fi ku kiyaye dokokin Allah na a yi ko a bari. Tare da haka ina yin azumi, wata rana ina shan ruwa, ina Sallah, ina yin barci, kuma ina auren mata na. Wanda ya ƙyamaci sunna ta ba ya tare da ni."

Wannan karantarwa ta Annabi (SAW) ta haɗa da barci, sallah, azumi, shan ruwa, sannan ta haɗa da aure, wacce itace cikakkiyar kamala ta ɗan'adam. Kin yin wani abu ko barin wani abu ba shi ne ya ke nuna cewa mutum yana da kamala ko bashi da ita ba. Haɗa taura goma a baki shine na miji. Saboda haka Annabi (SAW) ya ce musu "ni ina sallah ɗin da kai za ka yi, kuma ina barci. Sannan ina azumi ina shan ruwa." Domin idan ka yi sallah ka gyara lahirar ka. Idan kuma ka yi barci ka taimakawa jikin ka. Saboda haka kaga ya haɗa duniya da lahira a cikin yin sallah da barci. Barcin ka zai sa jikina ya huta, ka ga ka gyara duniyar ka. Sannan sallarka za ta sa ka gina lahirarka. Ka ga a cikin yin barci da kuma farkawa a yi sallah ka ga an gina duniya da lahira.

Hakanan Anabi (SAW) ya ce ina azumi kuma ina shan ruwa. Ka ga idan an yi azumi an gina lahira; idan an sha ruwa kuma an gina jiki. Ka ga anan ma ya haɗa

duniya da lahira. Kuma ya ce ina auren mata na, ka ga a cikin aure ma akwai buƙatar duniya da ta lahira a ciki. Domin idan mutum ya yi aure, ta hanyar auren nan mutum zai samun lada mai tarin yawa wanda ba zai same shi a wata ibada ba. In dai har ka kula da haƙƙoƙin sa, ka bawa mata haƙƙinta wanda ya wajaba, to za ka yi ibada da yawa a cikin sa. Sannan kuma ya ce wanda duk ya ƙyamaci sunnata to ba ya tare da ni, ko ba ya cikin al'ummata, ko baya kan tafarkina. Wannan hadisin Imamul BuKhari ne ya rawaito shi a hadisi mai lamba ta 5063, haka kuma Muslim ya rawaito shi, mai lamba ta 1401.

Sannan an rawaito wani hadisin daga Maƙal bin Yasar; ya ke cewa Mazon Allah (SAW) ya ce "ku auri mata waɗanda suke ƙaunar ku kuma waɗanda suke haihuwa." Kalmar ƙauna da haihuwa abune da yake da muhimmanci ga mai aure ya lura da su. Kada mutum ya kuskura ya auri matar da ba ta son shi, ko mace ta auri mijin da ba ta so. Ko iyaye su takurawa namiji sai ya auri matar da ba ya so. Ko a takurawa mace sai ta auri namijin da ba ta so, kada a yi haka saboda musulunci ya hana. Manzon Allah ya ce "tazawwajul wadudul waluda. Alwadud minal wadud, alwalud kuma mminal walud; ana nufin wato mai haihuwa kenan, kuma mai soyayya. Ita soyayyar nan itace take riƙe aure. Ita ke jawo gamsuwa, hakuri da abubuwa da dama. Auren soyayya ya fi kowane aure daɗi musamman in an kula da ƙa'idojin abinda zai riƙe, ya dawwamar da kuma zaunar da soyayyar.

Sannan idan mace tana haihuwa, ƙara daraja ta ke yi a wajen mijin ta. Domin 'ya'yan da yake haifa ɗinnan da ita zai yi alfahari da jin daɗi da su ne da kuma samun sanyin ido. Don haka Annabi (SAW) ya ce ku auri mace wacce take akwai soyayya da haihuwa tsakanin ku. To waɗannan abubuwa 2 duk ba za a gane su ba sai bayan aure. Wataƙila ma sai an yi shekaru da yin aure. Ba alamomi bane na kusa-kusa wanda da ka ga mace za ka iya gane waɗannan abubuwa a tare da ita. To amma me ake nufi a wannan hadisi? Malamai suka ce idan ɓangaren soyayya ce ka dubi zaman baban ta da babar ta. Idan ka ga da baban ta da babar ta suna zaman lafiya da fahimtar juna, babu rigima da daru da dambe a cikin gidan, to alamace ta cewa itama ba za ta yi maka irin wannan halin ba; domin ba ta ga babanta da babarta suna yi ba. Ka ga kenan za ka iya fahimtar wacce za a yi zaman lafiya da ita, ta hanyar zamantakewar iyayen ta.

Sannan mai haihuwa kuma za ka iya fahimtar haka ta hanyar babarta, ƙannen babarta da yayyen babarta. Idan iri na haihuwa ne za ka ga a gidan su babarta tana da 'ya'ya 5, 7, 8, 9, 10 har sama da haka ma. Itama haka, da za ka binciki ƙanwar babarta ko yar babarta, itama zaka ga ta kwatsa 'ya'yan a wani gidan da yawa. To wannan ya nuna iri ne na haihuwa. Saboda haka ka ga za ka iya kafa hujja da cewa itama za ta biyo wannan layin. Kuma mafi yawa hakan ake samu duk da ana samun kaɗan ɗin amma mafi yawa za ka ga in dai ana haihuwa a gidan su itama

takan biyo irin wannan gidan. To shine Manzon Allah ( SAW) yace zan yi alfahari da taƙama da yawan al'uma ta a ranar ƙiyama. Ka ga yawan al'umma ashe alheri ne. Yawan 'ya'ya alheri ne amma da sharaɗi guda biyu. Na farko a basu ilimi, tarbiya da kuma sana'a. Domin idan mutum bashi da ilimi, wato rabin mutum ne, wani kwatane ma, wani ma bai fi inci ɗaya ba ma a cikin mutane. Dan hakane ma za ka ga wasu mutum dubu idan basu yi karatu ba, dubu basu da sana'a, dubu basu da tarbiya,to  in ka haɗa dubu ukun nan, in ka samu mutum ɗaya mai ilimi da tarbiya da sana'a sai ka ga duk ya fiye maka amfani fiye da wannan dubu ukun baki ɗaya. Domin abunda Bahaushe yake cewa, 'da haihuwar yuyuyu, gara a baka ɗa ɗaya ƙwaƙƙwara'. To wannan magana ce muhimmiya, ba wai kawai a tara 'ya'yan ba. Shin za mu iya ilmantar da su? Shin za mu iya tarbiyantar da su? Za mu koya musu sana'a? In baka yiwa ya'ya'nka haka ba to yawan sa bai yi amfani ba.

Malam Abu Dauda ya rawaito wani Hadisi mai lamba ta  2050, Imam Nisa'i ma ya rawaito shi. Ka ga wannan Hadisi kenan yana karantar da mu cewa, lallai in mutum zai yi aure ya tsaya ya yi bincike ya tabbatar da wannan mata ta samu kyakkyawar tarbiya da  ilimi, da kuma kulawa. Ta zamana wacce iyayenta sun ɗora ta a kan gwadabe mai kyau. Domin kada mutum ya zo ya aurowa kansa rigima, ko ita mace ta aurowa kanta namiji mai rigima, tashin hankali ko fitina.

Haka  Hadisin Abdullahi ɗan Mas'ud yake cewa, Manzon Allah (SAW) ya tara mu (lokacin suna matasa 'yan shekaru 18, 19, 20 zuwa 30, sai Manzon Allah ya tara su ya ce…

"Ya ku dandazon matasa, wanda ya samu ikon ɗaukar nauyin aure, to yayi aure." Wato idan mutum yana da dama; yana da sana'a da gurin da zai ajiye matar, kuma ya shirya ya samu ilimin aure cikakke, to yayi aure. Meye amfanin aure a wannan ɓangare na matasa? Ya ce…

Shi aure ɗinnan shi zai taimakawa mutum wajen runtse idonsa da kuma kiyaye farjin sa. Ku runtse ido ga barin kale-kallen matan mutane, da kuma kare kai daga faɗawa illar zina da ƙawayen zina ɗin. Wanda mun yi bayani cewa, idan mutum ya riga ya faɗa tarkon sheɗan, ya jefa shi cikin manya-manyan laifukan da ake tafkawa, da gaba ko da baya- wato mutum ya shiga harkar luwaɗi, ko ya shiga harkar zina, ko mace ta shi ga harkar maɗigo, ko ya shiga amfani da hannun sa, ko ya dinga amfani da dabba, ko kuma ya dinga amfani da kayayyaki na roba da akeyi, wanda akwai na mata akwai na maza. Ance a wata ƙasa akwai kamfani musamman wanda bashi da wani aiki sai ƙerawa mata da maza wani nau'i na mutummutmi na roba, waɗanda za su riƙa gamsar da su. To ka ga wannan duk fasiƙanci ne, kuma sune wanda Allah ya ce… "Sune waɗanda suke kiyaye

gabansu, in ka gansu da wate mace, matarsu ce ta aure ko abinda suka mallaka na kuyangi da bayi da sa ɗaka. Amma idan ba wannan ba, ba za ka taɓa ganinsu suna aikata irin wannan jara'in ba. To ganin al'umma, matasa sune ginshiƙin bayan al'umma. Idan matasa suka ginu, al'umma ta ginu. Idan matasa suka lalace, to al'umma ta lalace.

To wanda bai samu wannan damar ba to ya shagala da yin azumi. Domin azumi ɗinnan shine zai zame masa abin da zai yanke masa sha'awa. Kamar ya yi wa kansa gyaɗar dogo ko kariya, ko ya sa wani katanga, ko shamaki tsakanin sa da faɗawa cikin zina. Wanda in ya fara ta yana yaro, shi yasa za ka ga da yawa mutane suna da aure amma suna fasiƙanci. Dalilin, wasu sun fara yin fasiƙancin ne kafin su yi auren. Shi auren ya biyo layi ya taras da mutum yana fasiƙanci, to ka ga tunda da fasiƙanci ya fara gamsar da rayuwar sa, to ko ya yi auren ba zai iya gamsuwa da iyalisa ba sai ya je yayi fasiƙancin. Wani ma inda yake zuwa ya yi fasiƙancin, in ka duba wacce yake fasiƙancin da ita, matarsa ta fi ta kyau, ilimi, iya ado da kwalliya sannan da tsabta. Waccan da ta ke kowa ma ya zo ya yi amfani da itama kamar banɗakin kasuwa. Amma ka ga sai ka ga mutum ya tafi can ya bar iyalan sa waɗanda suke ga tsabta, ga tsaro na lafiyar mutum ma da sauran wasu abubuwa. To amma abinda ke jawo haka dama shine farawa da fasiƙanci. To tunda matasa sune al'umma, sune a tsakiya. Yara suna kallon matsasa, tsofaffi suna kallon matasa, saboda su tsofaffi tasu ta ƙare, sai dai su bada shawara. Su kuma ƙanana tasu bata kawo ba. Don haka matasa sune a tsakiya kuma sune al'umma. Sune idan suka gyaru al'umma ana yi mata fata na gari. Idan kuwa suka taɓarɓare, suka lalace to al'umma ma tana kan taɓarɓarewa da lalacewa.

Ba ana nufin wanda basu isa ba, wato waɗanda sun isan amma ba su yi nisa ba. Za ka ga ai a matasan mu, wani ya kai shekara 35 ko 40 bai yi aureba. To idan ka kai 40 ba ka yi aure ba, yaushe za ka yi? Idan ka yi aure a shekara 40 kana so ka samu ɗa ɗan shekara 20, to fa kai sai ka kai 60 sannan kake da ɗa ɗan shekara 20. Lokacin da kakai shekara 60 ba ka da ɗa ɗan shekara 20 da zai taimaka maka to mutum yana da matsala. Amma idan mutum ya yi aure da wuri, misali yana ɗan shekara 20, ka ga da ya kai 40 yana da ɗa ɗan shekara 20 a ƙasa. Ka ga idan ka samu ɗan shekara 20 a ƙasa ya baka dama ka samu yadda za ka sarrafa shi, kaga kenan ya taimaka maka cikin wasu abubuwan ka kafin ƙarfin ka ya ƙare. Dama babbar matsala ga mutum a ce ya tsufa yana da ƙananan 'ya'ya. Kaga su ƙarfinsu bai kawo ba balle su taimakawa mahaifinsu. Shi kuma ƙarfinsa ya ƙare ba zai iya tallafa musu ba. Sannan ratar da aka samu mai nisa tsakanin mahaifi da 'ya'yan sa, tana sa kowa yana yiwa kowa kallon ba ɗan zamanin kowa bane. Su suna ga baba ya ci zamanin sa ya tsufa bai ma san me ake ciki a wannan duniyar ba, don haka shawarwarinsa suna zuba sune kawai a kwandon shara.

Shi kuma yana ganin waɗannan ‘yan mitsi-mitsin yara ne ‘yan ƙarshen zamani da basu san ƙimar dattijai ba. Amma idan ya zamo tsakanin ku da ‘yar ratar ko da kaɗan ce, to sai ka ga zamaninsa da zamaninka ɗaya ne. Sai ka zama abokin shawararsa shima ya zama abokin shawararka. Idan ma an gan ku ba za a iya cewa ɗa da uba bane, sai dai a ce wa da ƙani ne. To ka ga duk wani tunani da kake so ka ɗura masa, ko wani yanayi da kake so ka saka shi a kai to zai ga babu nisa tsakanin ka da shi kuma zai san baban sa ɗan zamani ne. Idan yaro ya yi yi zamani ɗaya da babansa, wannan ya fi kwantar da hankalinsa, ya karɓi saƙo kai tsaye daga mahaifinsa. To ka ga amfanin yin aure da wuri kenan ga mata da maza da suka kai shekaru a ƙalla a ce dai 20 ko sama da haka kaɗan. Amma idan mutum ya tafi shekaru 30 ko 40 to wannan akwai matsala.

Akwai Hadisi na Abi Zarrin da yake cewa Manzon Allah (SAW) ya ce a cikin saduwa da ɗayanku zai yi da iyalansa akwai ladan sadaka. To wannan abu sai ya jawo hankalin sahabbai suka ce ya Rasulallah, ya ɗayan mu zai jewa sh’awarsa, wato ya biya buƙatarsa sannan lokaci guda kuma a ce yana da lada? Suna ga kamar abun ya yi yawa. Ka biya sha’awar ka, ka ji daɗin rayuwar ka kuma a ce kana da lada. Sai Manzon Allah SAW ya ce ku bani labari, da mutum zai je ya saka ta a cikin haramun, wato ya je ya yi zina, ko ya yi abinda aka haramta, ba zai samu alhaki ba? Suka ce eh yana da alhaki. Sai yace hakanan idan ya je ya sadu da iyalansa na halal yana da lada. Ka ga wannan ƙarfafawa mutane ne cewa su yi aure.  Su ci da iyalai su kuma ɗau nauyin su gaba ɗaya domin akwai lada mai yawa da Allah zai basu.  Imam Muslim ya rawaito wannan Hadisi mai lamba ta 1006, da kuma Abu Dauda ya rawaito shi a Hadisi mai lamba 1286.

Sannan a hadisin Abdullahi bn Amr y ace Manzon Allah (SAW) yake cewa, duniyan nan jin daɗi ce. Mafi alherin jin daɗin duniya shine Allah ya baka nagartacciyar mata. Idan Allah ya azurta ka da mace ta gari, to an baka muhimmin abu a rayuwar ka, kamar yadda ya zo a Hadisin Muslim a hadisi na 1467. Haka ya zo a Hadisin Sahid bn Zubairu yake cewa, Abdullahi dan Abbas ya ce min, shin ka yi aure? Na ce ban yi aure ba. Ya ce to maza ka je ka yi aure domin mafi alherin wannan al’umma shine wanda yake da yawan iyali. Domin shine wanda zai amfanar da al’umma a samu malamai, injiniyoyi, likitoci da sauran su. Idan dai har mutum zai iya tarbiya, to tara iyali ya fi. Idan ko ba za ka iya yi musu tarbiya ba, to ka je ka yi ‘family planning’, domin kar ka haifi ɗan da zai zame maka matsala, ya zamewa kansa matsala ,ya zamewa al’umma matsala, ya zamewa ƙasarsa matsala, kuma a zo ana Allah wadai ko a riƙa cewa da haihuwar sa gwara a ce ma ɓarinsa aka yi.

Shi ‘family planning’ ba matsala ga wacce ba ta da lafiya da kuma wanda ba zai iya ɗaukar nauyin ‘ya’yan sa ya kuma yi musu kyakkyawar tarbiya ba. Shi yasa

wata rana kamar yadda hadisin Sa'ad bn Abi Waƙƙas suke cewa saboda son ibada da kuma ganin cewa aure yana da nauye-nauye waɗanda wani ba zai iya kiyayewa ba, har yake cewa, Manzon Allah (SAW) yake cewa akwai wani sahabi wanda ake ce masa Usman bn Mas'um, ya zo ya sami Manzon Allah (SAW), sai ce ya Manzon Allah ka bani damar na yiwa kaina fiɗiya. Fiɗiya itace irin yadda ake yiwa ɗan taure, wato a yanke masa maraina ta hanyar  zare 'ya'yan marainan nasa. Sai ya ce to nima ka bani dma na yiwa kaina fiɗiya. Manzon Allah (SAW) yake cewa a'a, bai halatta mutum ya je ya fiɗiye kansa ba. To shine Sa'ad bn Abi Waƙƙas yake cewa, da Manzon Allah ya bashi dama ya yi, da muma duk mun je mun yiwa kan mu fiɗiya domin mu ka haƙura da auren gaba ɗaya sai mu je mu yi ta ibada. Wannan Hadisi Imam Buhari ya rawaito shi da Imam Muslim.

TAMBAYA KAN AURE 02

Mun kawo bayani dangane da hukuncin aure wanda shi ya kamata mutum ya fara sani tun kafin ma ya yi auren. Wanda mun kasa malaman duniya kaf zuwa kashi 3 dangane da yadda suke kallon aure. Mun kawo malamai kashi na farko waɗanda suke gani wajibi ne mutum ya yi aure sau 1 a rayuwar sa. In kayi wannan ka sauke nauyin duk waɗannan ayoyi da hadisai da maganganun malamai da suka ce ayi aure. To idan kayi sau ɗaya, duk ka fita daga kowanne irin zargi a rayuwar ka. Sannan kashi na 2, malaman da suka ce an so ka yi aure ne, wato ba wajibi bane. In ka yi aure za ka samu lada. Idan baka yi ba kuma ba ka da alhaki- amma da sharaɗin za ka iya tsare mutuncin kanka. Ba za ka ga matar wani ka yi sha'awa ba, ba za ka yi zina ba, ba za ka yi duk wani laifi wanda yake na 'jara'ilul insiya ba'. Shine kamar a ce mutum yana luwaɗi, mace tana maɗigo ko suna zina tsakanin su ko suna anfani da hannun su, ko da wata roba ko da wani abu wajen biyan buƙatarsu ta sha'awa. Ai ka ga anan ya nuna cewa kenan yana da bukatar yin auren. Saboda haka ya zama auren ba zai zama rashinsa ya halaka shi ko ya ɗora shi a tafarkin halaka ba. To suka ce wanda ya samu kansa a irin wannan yanayi, to auren gabaɗaya mustahabbi ne a gareshi. Kuma a nan ne muka kawo malamai a cikin littafin 'Ulama'u uzza', wanda malam Abu Guzza ya tattara malamai kusan talatin da y'an kai, mazan su da mata, mashahurai, sanannu, gogaggu masu tsoron Allah, waliyan Allah, waɗanda har suka koma ga Allah ba wanda ya yi aure a cikin su. Amma mun yi bayanin cewa ba dan suna ƙyama ko suna ƙi, ko suna gudun aure ba, sai don rayuwarsu ta shagaltu da wani aiki wanda ba su gama shi ba suka koma ga Allah.

Sannan muka ce malamai kashi na 3 suna ganin aure ya sassaɓa kamar ma yadda mutane suka sassaɓa. Don haka ba za a iya cewa wajibi ne ga kowa ba saboda ya zama wajibi ne a kan wasu. Haka kuma suka ce ba za a ce mustahabbi ne ba don a kan wani mustabbine. Wani ma haramun ne ya yi aure in ji waɗannan malamai kashi na 3, waɗanda sune za mu yi bayani akan su yanzu.

Su ka ce aure ya saɓa gwargwadon saɓawar mutane. Wannan shine abinda mazhabarmu ta Malikiyya da wani ɓangare na malaman Shafiʼiyya da na Hanabila suke gani. Suka ce na farko aure ya kan zama wajibi akan wani mutum. To waye wannan wanda wajibi ne ya yi aure? Suka ce mutumin da yake da shaʼawa mai ƙarfi kuma yana da buƙata zuwa ga saduwa da mace. Wanda idan bai yi aure ba, ko idan ba ta yi aure ba akwai tsoron suna iya faɗawa zina. To wannan tsoron za a faɗa zina ɗin, ko ganin alamun haka, to wajibi ne ya yi aure domin ya kare kansa; itama mace wajibi ne ta yi aure domin ta kare mutuncin ta. Abinda wajibi ba ya cika sai da shi to ya zama wajibi. Maʼana tsare kai wajibi ne, to amma sai ya zama hakan nan ba zai yiwu ba sai an yi aure, ka ga aure ya zama wajibi kenan domin a tsare mutuncin kai. Sai malaman suka ce matar da ta samu kanta a irin wannan yanayi, da namijin da ya samu kansa a irin wannan yanayi, wanda in bai yi aure ba zai iya faɗawa halaka, to ko da ya tsare kansa daga halaka ɗin, wajibi ne yayi aure. Wannan shine kaso na farko da suka ce maganar aure.

Na biyu akwai wanda shi kuma an so ya yi aure ne amma ba wajibi bane a kansa. Menene maʼanar an so? Shine abinda idan ya yi akwai lada idan ya bari babu alhaki. Suka ce mutumin da yana da shaʼawa, amma kuma shaʼawar tasa ba ta da ƙarfin da za ta iya jefa shi cikin zina, maʼana yana da kamewa kuma ya shagala da wani aiki na ibada wanda daidai suke da auren. Saboda haka suka ce shi wannan anso ya yi aure domin sai ya ƙarawa kansa ƙarfi a kan ƙarfi. Idan kuma ma bai yi auren ba ya tsaya a haka, to ba za a ce ya ƙi aure ba, kuma ba za a zarge shi ba domin rashin auren ba zai jefa shi cikin wata halaka, ko matsala ko shaʼawa zuwa ga matar wani ba. Don haka suka ce wannan kashi na 2 kenan wanda shi an so ya yi aure.

Suka ce na 3 akwai wanda haramun ne ma ya yi auren. Abin da ake kira haramun shine idan ya yi auren alhaki zai dinga ɗauka. Idan ya yi aure laifi za a dinga rubuta masa. Idan ya yi auren wata kila ya zama dalilin halakarsa duniya da lahira. Ka ga wannan shi auren haramun ne a kansa. To wanene wannan mutumin ko

wacece wanan matar? shi ne mutumin da ba zai iya ɗaukar nauyin iyalin ba. Ba zai iya ɗaukar nauyin matar da kula da haƙƙin ta ba. Zai dinga cutar da ita ta hanyar rashin ci, sha, sutura, lafiya  da sauaran su. Wanda a cikin littafin Iziyya ya gaya mana, akwai malaman da suka ga cewa idan mutum ya ga zai halaka zai iya yin aure ko da bai samu halal ɗin da zai iya ci da matar ba. Idan dai an samu kuɗi na shubuha- wato abinda ba haram kai tsaye ba, ba kuma hahal kai tsaye ba. Akwai kama da halal ta wata fuska da kuma kama da haram ta wata fuska. To idan ya ga zai halaka ya na iya auren mace ya ci da ita da irin wannan dukiyar. Domin shubuha ɗin ta fi sauƙi akan faɗawa cikin zina ko cikin haramun. Don haka ka ga kenan wanda duk ya ga ba zai iya wannan ba, to yayi auren haramun ne domin zai yi ta ɗaukar alhaki da zaluntar mace. Sannan kuma ya zo ya haifo ʻyaʼya bai sa su a makaranta ba, bai kuma basu tarbiya ba, sai ʻyaʼyan su zama balaʼi ga alʼumma, shi ma ya zama balaʼi ga alʼumma. To ka ga wannan auren bashi da anfani. Kuma auren da ya yi alhaki kawai ya ɗauka tsagwaron sa.

To sai suka ce shi haramun ne ya yi aure. Waɗanda ba su da lafiya da ba za su iya kulawa da haƙƙoƙin iyalan su ba ta wurin saduwa duk sun shiga ciki. Sai dai idan matar ce ta ce ta yarda cewa mijin ya biya mata buƙata ta wata hanyar ba ta saduwa ba. To idan hanyar an yarda da ita, to ana iya yin auren. Dama abinda aka haramtawa namiji ga matarsa abu 2 ne kawai. Kada ya sadu da ita tana alʼada sai kuma kada ya sadu da ita ta dubura. Amma idan ta san bashi da lafiya kuma bashi da ƙarfin da zai iya gamsar da ita, amma ta ce ta yarda ta aureshi sai ta riƙa amfani da wasu ɓangarori na jikinsa domin ta gamsar da kanta, ko da hannun sa ne zai riƙa saka mata a gabanta ya gamsar da ita, in dai ita ta yarda da hakan, to malamai suna ga babu laifi. Domin abinda ba a so ita ɗin kada ta je ta faɗa cikin halaka saboda ita mijinta bashi da lafiiya. Shi kuma ana tsoron kada ya auro mace ɗin ya kasa gamsar da ita, kuma ya  je ya faɗa cikin halaka. Don haka wannan shine kashi na 3 kenan.

Kashi na 4 na malaman suka ce akwai wanda shi makaruhi ne ya yi aure. Wato shi wanda aka ce makaruhi ne ya yi aure, shine wanda shi bashi da shaʼawa, ko kuma yana da shaʼawar amma ba ta ɗaɗa shi da ƙasa ba. Ko da bai yi aure ba wannan shaʼawa tasa ba za ta jawo masa rigima ko ta jefa shi cikin halaka ba. Kuma sannan ya shagala da ibada, neman ilimi da karatu, kuma yana gane karatun. Kuma idan ya tafi a haka zaʼa amfana da shi. Amma idan ya yi aure, to zai shagala da zuwa

kasuwa da nemar mata abinci da sutura da zai sa harkar ilimin da karatun ta yi rauni. To wannan aka ce shi ba a so ya yi aure ba. Domin auren bai zame masa alheri ba domin zai hana shi yin wani abin da ya fi auren alheri a rayuwar sa ta farko. Suka ce wannan zai iya zama cewa shi makaruhi ne ya yi aure. To wannan shine kashi na 4. Akwai wanda suke gani ma 'mubahi' ne. 'Mubahi' shine wanda da yin auren da barin sa duk ɗaya ne a gurinsa. Auren bai ƙara masa wani abu na musamman ba, ko kuma bai rage masa wani abu daga cikin abubuwan sa na rayuwa da ya ke yi ba. To wannan shine maganganun malamai dangane da abinda ya shafi aure ta ɓangaren hukunce-hukunce.

To akwai wata matsala da take tasowa. Shin wajibine ita mace ta yi aure? Ko ita a kan kanta, shin wajibi ne ta nemi miji ta yi aure? To anan ne malamai suke ganin cewa hukuncin su ɗaya da namiji. Ita ma ta kasu wannan kasha 5 ɗin. Akwai wacce idan ta yi auren gaskiya zaluntar mijin kawai za ta riƙa yi. Akwai wacce itama gaskiya idan ba ta yi auren ba za ta halaka. Yadda mazan nan suka kasu 5 haka suma matan suka kasu 5. To amma malamai sukan kafa hujja da hadisin Imam Abu Sa'idul Khudri. Wata yarinya ta zo wajen Manzon Allah (SAW) tare da mahaifinta. Mahaifin ne yazo ya kawo ƙpararta wajen Annabi. Ya ce ya rasulallah wannan 'yar tawa ta ƙi ta yi aure. Sai Manzon Allah ya ce da yarinyar, ke ki je ki yiwa baban ki biyayya ki yi aure. Ta ce a'a ya rasulallah ba zan yi ba har sai ka bani labarin haƙƙin da miji yake da shi a kan matarsa. Idan na ji zan iya sai na yi. Ta sake maimaitawa Annabi ya maimaita mata, ta sake maimaitawa. Sai ya ce, to haƙƙin da miji yake da shi akan matarsa shine, da za a ce miji yana da gulando, ko maruru, ko kaluluwa, a ce ciwon ya fashe yana fitar da mugunya, ko yana zubar da jinni. Ko kuma a ce hancinsa ya fashe yana zubar da mugunya ko yana zubar da jini, mace ta zo ta sa harshenta tana lashe wannan jinin, ko wannan mugunya da ke fita daga wannan ciwo ko gyambo, ko gulando, ko maruru ko, kaluluwa, to ba za ta iya biyan haƙƙin mijinta ba. Sai ta ce "wai wai wai, na rantse da Allah da ya aiko ka, bazan yi aure ba har abada.  Ba zan iya wannan ba."

To shi ne sai Manzon Allah (SAW) ya ce kada ku aure su sai da izinin iyayensu. To ka ga wannan mata Manzon Allah ya ƙyale ta da ta ji cewa ita ba za ta iya ba. Ita ba za ta yi zina ba, amma wannan haƙƙoƙin da aka faɗa na miji ita ba za ta iya karewa ba. Saboda haka aka ƙyale ta. Don haka malamai suka ce wannan hadisi ya nuna cewa akwai uzuri kenan ga wacce ba za ta iya kula da auren ba, sannan ba za

ta iya biyan haƙƙin mijin ba duk da cewa ba za ta yi zina ko ta jawo wa babanta zagi ba. Idan za ta jawowa babanta zagi ai ka ga dole ta yi aure tunda za a iya cewa ya bar ʻyarsa ta gandame a gida. To ka ga dole ya aurar da ita. Itama kai ba za ta ji daɗin rayuwar ba idan tayi irin wannan gandamewar. Dole sai ta yi auren za ta sanmu nutsuwa domin idan ba haka ba sai a yi ta zarginta cewa ko wani fasiƙanci take yi. Ka ga kenan abinda za mu ce a ƙarshe, ko da ba kya jin daɗin yin auren ki yi ɗin, ki haƙura da duk wata damuwa saboda auren zai kare miki mutunci ya kuma ƙara miki daraja.

Su kuma matan da suka tsufa ko mazajensu suka rasu, to ai irin waɗannan suma zaka iya kasa su kashi 3. 1- Akwai wanɗanda har yanzu suna da shaʼawa, ka ga waɗannan su yi auren ya fi. Kuma a nan matsalar da ake samu itace ta ʻyaʻya. Da yawa idan mace tana da ʻyaʼya manya sai su mayar da mijinta abokin gabarsu. Da ka zo ka ce kana son babar su sai ka ga duk sun canza maka fuska. Da yawa iyaye mata waɗanda suka kai wannan matsayin suna kawo mana ƙarar ʻyaʼyansu cewa sun hana su yin aure. Akwai wanda ya ce ma shi idan babarshi ta yi aure da wuƙa zai riƙa yawo sai ya kashe mijin da ta aura. Ita kuma uwar tana da buƙatar yin auren amma ɗanta yana barazanar zai kashe mijin da za ta aura. To ka ga wannan ai matsala ce.

2- Akwai wacce ta ke da ʻyaʼya kuma ga shekaru. Irin waɗannan matan ko mutum ya aure su to sai dai ya tashi ya dawo gidansu da zama a cikin ʻyaʼyan su. To irin wannan shima akwai matsala. Matsalar itace, ka zauna musu a gidan gado idan ba biya kake ba akwai matsala tunda ba gidanta bane na ʼyaʼyanta ne. Idan ta ce ka zo ka zauna dole ne a yanka maka abinda za ka riƙa biya na haya. Saboda idan ka zauna a gidan sai ka riƙa biya idan ba yaʼyaʼn nan ne suka yafe maka ba. Sannan na biyu ƙimarka ba ta da yawa domin duk sanda kuka samu matsala kaine za ka kwashe kayanka ka san inda dare ya yi maka. Sannan ʻyaʼyan ba lallaine su baka haɗin kai ba, maʼana, su kalle ka a matsayin yadda suke kallon mahaifinsu ba. Ko su mutunta ka yadda suke mutunta mahaifinsu ba. To irin wannan shima mata masu ʻyaʼya da shekaru suna samun matsala irin wannan.

3- Akwai wacce dama ita shaʼawarta ma ta ɗauke. Jinin alʼadar da take yi ma ya ɗauke. Ba ta shaʼawar namiji ma kwatakwata saboda shekarun ta sun yi nisa ga kuma ʻyaʼya ta hayayyafa. To ka ga irin wannan abinda ya kamata shine ta shagala

da tarbiya da kula da ʼyaʼyan ta. Shine ya fiye mata fiye ma da ace za ta yi aure da ba ta buƙatar sa.  To wannan shine kashe-kashen mata waɗanda suka yi shekaru suka samu kansu a irin wannan yanayi.

To, shin karatu uzuri ne na rashin yin aure da wuri? Za ka ga a matasa mutum ya ce ai shi digiri yake yi, sai ya gama. Bayan ya gama digiri sai ya yi bautar ƙasa inda daga nan kuma sai ya ɗauki takardun sa ya je neman aiki. Bayan ya samu aiki ɗin, zai ce sai ya fara aikin ya ga nawa ya tara. Bayan ya tara abinda ya tara a aikin kuma sai ya sayi fili. Bayan ya sayi filin sai ya gina gida. Bayan gina gidan ya gama komai da komai kuma sai ya sayi mota. Bayan ya sayi motar ma sai ya samu wani canji mai ɗan nauyi sannan zai yi aure. To wannan lissafe-lissafen sai ka ga sun ɗauki mutum ya kai har shekaru 35 ko 40 ko ƙasa da haka kaɗan sannan ne za ka ga cewa ya kai inda yake so ya kai. To lokacin da zai yi aure daga 40 ko ƙasa da haka, dama rayuwar ta yiwo ƙasa. Wataƙila kuma ya auri ʼyar shekara 20 ko 15. Wannan zai sa lokacin da shi ya kai ƙarshe a rayuwarsa ita kuma lokacin take tasowa. Lokacin da take buƙatarsa a lokacin shi kuma ya gaji. Kaga dole a samu rigima da matsaloli. Dan wannan yana cikin matsaloli.

Haka kuma akwai wacce za ta ce ita ba za ta yi aure ba sai ta gama karatu. To ita kuma mace ƙarin shekaru a gareta raguwar daraja ne. Shi namiji shine wanda in yana ƙara shekaru yake ƙara daraja. Yanzu in aka ce da mace, wance ai tsohuwa ce, ba ta jin daɗi kamar yadda shima namiji in aka ce wane yaro ne ba ya jin daɗi. Da yake shi namiji baya son yarinta, ya fi so a ce shi babba ne. Ita kuma mace ta fi so a ce mata ƙarama. In ka cewa mace tafi can tsohuwa to ita tana ga ba daidai bane. Shi ko namiji in ka ce da shi tafi can tsoho za ka ga bai damu ba saboda dama can an sa shi da son shekaru. To wannan abubuwan guda biyu suma matsala ne na cewa ba zan yi aure ba sai na gama karatu. To lokacin da wataƙila za ta gama karatu ɗinnan ta kai 30, ko 25 ko kusa da haka. Akwai wacce ma za ka ga ta yi 35 budurwa ce a gidan su. Kai akwai wacce ma ta gaya mini shekararta 41 amma bata taɓa yin aure ba.

Saboda haka wanda take hari ta aura saboda tana ganin  ta yi karatu, ta yi ilimi tana aiki to shi kuma yana ga ta yi masa tsufa. Shi kuma wanda yake harin ya auren ta shi kuma yana jin tsoron ta yi mishi girma. To saboda haka sai mace ta wayi gari na ƙasa da ita yana tsoron ta, na sama da ita kuma yana gudun ta. Ita kuma ba ta son na ƙasa da ita saboda ta yi karatu, ta yi ilimi tana aiki. Don haka daga ka ce wa

wani babban ɗan boko da ke sama da ita da ya kai matsayin dakta ko farfesa, sai ka ji yana cewa nemo min ʻyar sakandare wacce bata yi nisa a karatu ba kuma kanta bai waye ba. Sai ka ga su masu ilimin wasu, suna gudun auren mata masu ilimi. Su kuma matan sai ka ga suna gudun auren waɗanda basu da ilimi. To sai ka ga mace a wannan tsakanin take gamuwa da matsaloli da yawa a rayuwar ta.

To sannan kuma aure da banbancin shekaru mai yawa shi ma wataran yana da matsala. Matsalar itace; misali mutum ya kai shekara 50 sai ya je ya nemi ʻyar shekara 15 ya aura. Ka ga akwai zalunci a nan ta wata fuska. Ta fuskar shine lokacin dai zai kai shekara 70, ita kuma lokacin ne fa ta kai shekara 30 ko 25. Lokacin da mace ta kai shekara 25 ko 30 a nan ne ƙarfin shaʼawarta da buƙatarta ga ɗa namiji yake. To shi kuma ƙarfinsa ya ƙare ita kuma nata ya kawo. To a nan ne idan ba a samu kulawa sosai ba sai ka ga da aurenta kuma tana zina saboda mijin ta ƙarfin shi ya ƙare ba zai iya gamsar da ita ba. Shi kuma ya ɗauko ta tana ƙarama. To wannan shima akwai matsala.

Sannan kuma wani sai ya je ya auro wacce ta grime shi a shekaru. Duk wannan abin da muke faɗa ba wai haramun bane a shariʼa amma yana da matsaloli. Ace ta auri wanda ta fishi shekaru. Shi ma kuma ba za ta kalle shi da ƙima yadda ya kamata ba. Ko ita ma a rika zarginta cewa ta auri yaro shi kuma ana zarginsa cewa ya auri tsohuwa. To wannan a cikin duka abubuwan da muka faɗa matsaloli suna faruwa. Ya kamata mutane su riƙa lissafi na wacCe irin mace ce za a aura, ko kuma banbancin arziƙi da wAdata. Ko banbancin launin fata, da yanayin ɗabiʼu. Ko banbancin alʼada da ƙabila. Wannan duk bashi da wani muhimmanci da tasiri a addini. Mutum ya ji cewa shi ɗan ƙabila kaza ne ya auri ʻyar ƙabila kaza.Wani ma zai ce ya shi yana ɗan ƙabila kaza zai auro ʻyar ƙabila kaza. Kamar shi Bahaushe da Bafulatani shi yake ganin kowa ma a duniya ƙabila ne. Sai a ce ya je ya auro ƙabila. Kabilar bahaushe da ƙabilar bafulatani amma sai ya riƙa kallon wasu mutane a matsayin ƙabilu. Ko kuma mace ta Musulunta wani ya aure ta sai kaga har ana mata gori da cewa "ai tubabbiya ce". Koma babanta ne ya Musulunta aka aure ta sai ka ga ana mata gori da cewa tubabbiya ce. To ka ga wannan shima matsala ne, Musulunci bai yarda a riƙa kiran wani tubabbe ba. In ka duba ai sahabban Annabi Muhammad (SAW) gaba ɗaya in ka ɗauke annabawa da manzanni babu mai darajar sahabban Muhammadu (SAW) amma duk manyansu ai musulunta suka yi. Saboda haka tunda musulunta sukayi ai shikenan wanda ya

musulunta bai kamata a cewa wani tubabbe ba.  Idan har za ka cewa wani tubabbe, Abubakar da Umar da Usman da Ali ma za ka ce musu tubabbu. Kuma ma ai ba abin zargi bane a soki mutum da ya tuba. Idan ya ƙi tuba shine abin zargi.

Saboda haka wannan alʼada tamu da muke sukan waɗanda suka musulunta; ko mu soki iyayen waɗanda suka musulunta da cewa su tubabbu ne, da kuma alʼadar mu ta kallon waɗanda ba mu ba a matsayin ƙabila ne komai musuluncin su, to waɗannan alʼadu guda biyu musulunci bai yarda da su ba. Kamar yadda ka ga ana ware masu wata sanaʼa ana ƙyamar su, wato masu sanaʼar fawa. Da masu saʼar wanzanci da wasu abubuwa da ake gani kamar masu irn wannan ba za a auri ʻyaʼyan su ba, shi ma duk shiririta ce. Saboda haka a Musulunci, matuƙar mutum ya yiwa ʻyarsa kyakkyawar tarbiya , Musulmi ne shi mai kula da tarbiya, ko wane ƙabila ne ko wane yare ne, ko wacce irin sanaʼa ya ke yi ba za a ƙi auren ʻyarsa saboda wannan ba.

Idan mace tana aikata laifuka ai kashi biyu ne. Kamar a ce abinda ya shafi matantakarta, wato tana  zina ko maɗigo. Rannan wani ya rubuto tambaya cewa zai auri wata yarinya amma ya samu labari tun a makarantar sakandire suna yin maɗigo ita da ƙawarta. To shine ake bashi shawara kada ya aure ta. Ita kuma ta zo tana tabbatar masa da ta tuba ta daina, to shine ya ke tambaya. To sai muka ce idan dai har ya tabbata ta tuba ta kuma gayara to ba matsala. Shi tuba ai tsakanin Allah ne da bawansa. Wata kuma za a ce zina take, to ka ga shima akwai matsala. Idan har mace tana zina to ba za a aure ta ba sai an samu sharaɗi guda biyu.

i- A samu inganntaccen tuba na zaran bunu wanda babu alamar komawa daga gareta sannan a samu nadama.

ii- A yi mata istibraʼi da sikanin (scanning)- shine a tabbatar da cewa bata da ciki kuma zina da ta keyi bai sa ta yayimo cutar ƙanjamau ko wasu cututtuka da ke iya yaɗuwa ta hanyar  jimaʼi wanda za ta iya sawa mijin ta da ta aura ba. Idan an tabbatar da lafiyarta kuma bata da juna biyu sannan ta tuba, to mutum yana iya aurenta in yana buƙata. Saboda haka waɗannan abubuwa suna nan.

Haƙiƙa matsalar karatu, aiki da kasuwanci na daga cikin abubuwa da ake samun matsala a cikin zamantakewa ta aure. Akwai mata ʻyan kasuwa attajirai waɗanda suke tafiye-tafiye zuwa Indiya, Dubai,  Saudiya da sauran su domin yin kasuwanci. Ta zama hamshaƙiyar mai kuɗi. Wata kuma tana kasuwancin ta a cikin gida na sayar da man gyaɗa da man ƙuli-ƙuli da sauran su. Akwai wacce tana zuwa kasuwa ta sayo kayayyaki.

Sannan akwai matar da take karatu ko za ta sharɗantawa mijinta karatu take yi ko za ta yi karatu. Watama kuma karatun ƙila tana matakin NCE ne ko na Difloma, daga nan sai ta wuce digiri ko na ɗaya ko na biyu ko na uku.

Sannan akwai matar da ta gama karatu, ko tana tsakar karatun amma za ta kama aiki.

To waɗannan abubuwa guda uku na daga cikin abin da yake kawo matsala a cikin harkar aure. To ya zaʼa yi mata su yi sanaʼarsu ko su yi karatunsu, ko su yi aikinsu ba tare da hakan ya dagula rayuwar su ta aure ko ta zamantakewa ba? Kuma ba tare da miji yana ganin yin kasuwancin matarsa, ko yin aikinta, ko kuma yin karatunta zai iya kawo masa cikas, ko kuma zai buɗe ƙofar wata ɓarna ta shigo masa cikin gida ba?

Mata tun a zamanin Annabi (SAW) suna kasuwanci, suna aiki, suna karatu. Amma ba irin sanaʼarmu da kasuwancinmu ba. Akwai bambanci tsakanin waɗannan abubuwa guda uku. Nana Khadija ai attajira ce. Idan ma a istilahin wannan zamanin namu ne ka iya kiran ta biloniya ce. Dalilin haɗuwarsu da Manzo (SAW) ai kasuwanci ne. Manzon Allah (SAW) ai ɗan kasuwa ne. Saboda abinda ake buƙata gun ɗan kasuwa sune riƙe amana da gaskiya. Shi kuma ya fi kowa amana da gaskiya. Ya gaya mana ya yi sanaʼar kiwo kuma ya yi kasuwanci. Saboda haka Nana Khadija da ta ji labarinsa yana da amana, yana da kwaliti da ake nema ga ɗan kasuwa, sai ta neme shi ta danƙa masa maƙudan dukiyar ta. Ya kuma je ya yi kasuwanci aka samu riba mai yawa; wanda wannan shine ma dalilin aure tsakanin su. Ka ga ashe kenan akwai mata ʻyan kasuwa tun a zamanin Manzon Allah (SAW).

Ta ɓangaren ilimi akwai mata malamai, irin su Ummi Yaʼaƙub, irin su Nana Aʼisha, irin su Nana Ummu Salama. Sun yi karatu mai yawa kuma sun rawaito hadisai tuli daga manzon Allah (SAW) wanda ke ƙunshe da karatun kowane babi.

Ka ga kuma amma tarbiyarsu tana nan. Sannan na uku akwai mata masu yin aiki irin su Ummu Mubashshir, wacce take aikin gona. Irin su wata mata mai sana'ar saƙa da ƙira. An samu ma mai sana'ar ɗinki da mai saida abinci kamar Ummu Sharikin, da masu sana'o'i daban-daban  duk a zamanin Annabi (SAW). Duka waɗannan mata ya tabbata suna da ayyukan yi a zamanin Annabi (SAW) kamar yadda ya tabbata a hadisai ingantattu.

To banbancin aikinmu na wannan zamanin da wancan aikin, da banbancin karatunmu da wancan aikin shine, mafi yawa mata ba sa bin ƙa'idojin da addini ya tanada musu na kamun kai da shiga ta addini a lokacin da suke gudanar da kasuwancin su. Haka kuma ba'a samun cikakken kamun kai da cikakken kula da mutunci, da shiga mai kyau ta addini a lokacin da suke karatu. Haka ba a samun cikakken kamun kai da cikakkiyar shiga ta addinin Musulunci a lokacin da sukeyin sana'a da karantarwa ko ta aikin gwamnati ko kuma nau'in aikin da suke yi. Amma ana samun mata 'yan kaɗan, da suna kasuwancin kuma kamammu ne. Ana samun 'yan kaɗan da suna yin karatun kuma kamammu ne. Ana samun 'yan kaɗan da suna yin aikin kuma kamammu ne. Wataran ɗabi'ar aikin ne yake jawowa mace matsala. Shine idan aikin ta cikin maza take gaba da baya. Dole za ta yi mu'amala da wasu mazaje, wata ƙila rayuwarta ma ta fi yawa tare da su. Domin gwamnati ta ba mutum dama ya yi aiki na awanni 8,  ka ga idan ka ɗauki takwas sau uku shine 24. Ka ga idan za ta yi barcin awanni 8 ta fita aikin  awanni 8, da hidimarta ta gida da rubuce rubucenta na gida da waye da mijinta suna daragowar awanni 8 kenan. Saboda haka ka ga mijinta bai samu cikakken lokaci daga gareta ba. Domin duk mutumin da yaje aikin awanni 8 , daga 8 zuwa 4 ai dole zai buƙaci in ya zo ya huta. Dole zai buƙaci ya yi barci, ya shiga banɗaki. Saboda haka awannin da za ta shirya, da na bayan ta dawo daga aiki, da awannin da za ta ɗauka na hutawa da kuma awannin da za ta ɗauka ta shirya kafin ta tafi aikin sai ka ga wataran an shiga haƙƙin mijin.

To daga nan sai a fara samun matsala. Ba ma haƙƙin ba sai ka ga wasu mutane suna yin mu'amala da matarsa wanda bai dace ba. Kamar yadda wani suka shaƙu da matar wani a wajen aikin sa. Shaƙuwa ta kai har shi yake ɗauko ta a mota ya kawo ta gida kuma shi yake zuwa ya ɗauke ta. Har mijin ya lura cewa shaƙuwa ta kai shaƙuwa tsakanin wancan ma'aikacin da wannan ma'aikaciyar matarsa har ta kai ma a gida ma ta fi tunanin wancan mutumin fiye da mijin nata. Ta fi maganar

wancan. Har yake zargin wasu abubuwa na iya shiga tsakaninsu da wancan mutumin. Saboda haka shi kuma ƙarshe sai ya yanke shawara zai sake ta. Shine aka je kotu. Da aka je kotu sai ya ce zai sake ta amma a saka sharaɗi, ta saka hannu cewa idan ya saketa ba za ta auri wancan mutumin ba. Ba za ta auri wannan mutumin da yake zargin tana soyayya da shi ba. To ka ga irin waɗannan abubuwa sune wasu ba sa jin daɗi. Sannan ana samun wasu mata su yi shekara da shekaru suna aiki ba ka taɓa jin wata matsala ba. Irin waɗannan matan sun kama mutuncinsu kuma suna yin shiga da ta dace da alʼada da addininsu. To ka ga irin waɗannan ba su da matsala, suna aikin amma ba su da matsala.

Wasu suna karatun ba su da matsala. Domin abinda muka yi ta nema  ma a yi doka kenan a cikin jihohin mu da ma alʼummar mu gabaki ɗaya domin ganin cewa duk malamin da ya yi amfani da damarsa ta shi malami ne, ko ya yi amfani da damar sa ta shi shugaba ne a wata makaranta har ya ɓata wata yarinya, to a kore shi daga aiki kwata-kwata. Kuma a haramta masa yin aiki a koʼina a duniya. Saboda wannan zai toshe ƙofar da waɗanda suke fasiƙai a cikin masu koyarwa ko masu aiki a manyan makarantu ko a maʼaikatu wanda za su yi amfani da damar su, su ci mutuncin mace ko su hanata makinta na jarrabawa, ko su hana ta damarta na ƙarin promotion a wajen aiki har sai tukunna ta bada mutuncin ta.

Wata idan ba irin wannan fitsarar take yi a maʼaikata ba sai ka ga damammaki suna ta samun ta ana toshe mata. Ko idan ba wannan fitsarar ta ke yi a makaranta ba sai ka ga bata samun maki na cin jarrabawa. Kuma ana samun irin wannan da yawa. Akwai wanda ya gaya mini wani malami ya riƙe masa sakamakon jarrabawar sa. Yazo yana ta neman ya zai yi sai aka nuna masa akwai wata yarinya a makarantar ya same ta kawai za ta je ta karɓo masa saboda shi malamin yana da alaƙa da wannan yarinyar. Saboda haka da ya je ya same ta ya faɗa mata halin da yake ciki, kawai kafin wasu ʻyan mintuna sai ga sakamakonsa ya fito. To ka ga wannan ai shine dalilin da ya sa wasu suke tsoron tura ʻyaʼyan su cikin irin wannan tsarin.

Dole sai hukuma ta karkaɗe hannun maʼaikata fajirai da fajiran malamai masu karantarwa. Ko kuma ta karkaɗe hannunsu da ga ʻyaʼyan mutane. Duk wanda ya yi ƙoƙari ba ruwanka da yarinyar nan ko tana kula ka ko tana sakar maka fuska ko tana zuwa ofis ɗinka ko kuna muʼamala da  ita. Sai an cire hannun waɗannan daga ʻyaʼyan mutane sannan zaʼa samu ilimi ingantacce kuma nagartacce. To ka ga

wannan shima abin gudu ne kuma abin tsoro ne a wannan zamani. Wata kuma aikin ya zame mata dole ta yi domin wani mijin bashi da ƙarfi. Mata da yawa sun tambaye ni, waɗanda su sun fi mazan tattalin arziƙi. Wata ma kamar itace take ɗaukar nauyin komai saboda mijin bashi da hali. Wataƙila ta yarda an yi auren ne saboda tana da mutunci. Ba ta so a riƙa zarginta da rashin miji. In suka daidaita da mijin in ya ce bashi da hali sai su yi yarjejeniya, ita za ta ɗauki wani ɓangaren. Akwai wacce take gaya min ma in ta ɗauko albashin gaba ɗaya mijin take danƙawa. Sai ya sayo musu kayan abinci, ragowar canjin ya zuba a aljihu yai tafiyar sa waje. To ka ga irim waɗannan matan gaskiya suna shan wahala sosai. Ga shi tana aikin amma mijin ne mai cinye albashin. Kuma ta ce ba cinye kuɗin da yake yi ko bashi ɗin da nakeyi yake damu na ba, duk irin wannan abin da nakeyi amma bani da mutunci a idonsa. Ba ya ganin ƙimata da girmana, to ka ga wannan matsala ce babba.

Dole sai an kalli matsalar aikin mata da kuma matsalar maza da suke da mata masu aiki. TO, yaya aikin yake taimakawa iyalan matan? kuma aikin ma meye amfanin sa ga matar ko ga mijin ko ga ʻyaʼyan matar? Yanzu wata za ka ga mai koyarwa ce kuma kullum sai ta je ta koyar. Amma ba ta da wani extra lesson da take yiwa ʻyaʼyanta a ckin gida. Kaga wannan ya nuna basu amfanu da kasancewar babarsu malama ba, don ba ta da lokacin su. Sai dai ta je ta yi sanaʼa, ita kuma ta ba wata ta kular mata da nata. Wata tana ta sanaʼar tana tara kuɗin amma ba ka ga tasirin kuɗin a jikinta ba. Yau da za a ce ta yi ritaya ba ta da wani abu da ta tanada ko ta ajiye wanda za ta iya dogaro da shi ta ɓangaren tattalin arziƙi, ko da ƙarfinta ya ƙare. Sanaʼa ake ta yi amma ba a ganin abin da aka tara. Duk sun tafi a biki, sayan kayan kwalliya ko wataƙila sun tafi a wajen gazawar mijin ma.

Akwai wacce ta ke gaya mana cewa tana aiki, amma ita take biyawa ʻyaʼyan kuɗin makaranta, shi uban baya yi. To ka ga duka aikin ya tafi kenan a wahalhalun gida, kuma an fita waje an sha wahala an dawo gida ƙara shan wahala. Kaɗan ne za ka ga wacce take aiki za ta gaya maka ba ta da matsala da mijin ko ba ta da matsala a wajen aikin, ko ba ta da matsala da abinda take tarawa idan ta dawo daga aikin, ƙawaye da ʻyanʼuwa da dangi ba su cinye ba. Ita kuma ta tashi da wahalar fita kullum da ƙafe 8 kuma an dawo ƙarfe 4 an gaji kuma a sake fita gobe. Sannan ga ʻyaʼya suna jiranta. Ga ciki, ga haihuwa, ga raino ga sauran abubuwa waɗanda dole

itama sai ta nemi wani ta biya shi ya taimaka mata nata kamar yadda ita ma ake biyanta take taimakawa wani.

To wannan gaskiya abin la'akari ne yadda maza suke zaɓa su darje, suma mata ya kamata su zaɓa su darje. Kuma wataran wajen zaben ya darje sai ga ji namijin ya faɗi a binda shi kansa bashi da shi. Wani ya taɓa gaya mini yace shi yana so ya auri mace fara, doguwa, mai hanci mai ilimi, da na kalle shi ai naga shi ba fari bane, ba dogo bane, ba mai hanci bane kuma ba mai ilimi bane. Sai na ce mishi matsalar shine wannan da kake so ɗin ita ma kuma tana son wani ba kai ba. Domin da wuya ka samu mai wannan suffar da ka faɗa itama ba ta da zaɓi. To ya kai za ka zo ka faɗi abinda kai in ka kalli madubi, ba ka da ko ɗaya daga cikin waɗannan abubuwa da ka lissafa kuma kace mai wannan suffa za ta sauko kai ta ɗauke ka? Idan ka ga ta ɗauke ka sai dai in ta ga kana da wata daraja ta musamman. Kamar kana da mulki ko kana da kuɗi ko kana da ilimi- wataƙila ta haƙura da waɗannan siffofin naka da kai baka da su wanda ita take da su. To ka ga wannan matsala ce.

Sannan ita kuma za ka ga ta sa buri wajen irin mijin da take so wanda wannan ma ya kan kawo jinkirin a daɗe ba a yi aure ba. Wata ƙila ƙawarta ko 'yar'uwarta ta auri wani hamshaƙin mutum ko mai kuɗi ko mai ilimi ko mai mulki. An yi hidima an kashe maƙudan kuɗaɗe, to sai ta dinga jiran irin wannan ya fito domin itama a yi irin wannan auren. Ita kuma ba ta san cewa al'amura a hannun Allah suke ba. Tana iya yiwuwa ta auri talakan ya juye ya koma mai kuɗin. Ko ta auri mai kuɗin ya juye ya koma talaka. Ko ta auri mara darajar ya koma mai daraja. Mun sha gananin mutanen da ba kowa ba amma Allah ya ɗaukaka su ya mayar da su wani abu. Kuma mun sha ganin waɗanda suke jin su wani abune amma sai Allah ya sauke su. To ka ga ashe kenan ba ma'auni bane in za a yi aure kawai a ce lallai sai wanda ya samu wata ɗaukaka ta duniya- domin za a iya samun ɗaukakar daga baya. Kawai abinda ake so tarbiya da kuma zuciya da kuma hali na gari. Wannan shi a ke buƙata a miji in za a aure shi haka matar ma.

To sannan wani za ka ga cewa iyaye su suke haɗa auren irin na zumunta ɗinnan. Shi baya so ko ita ba ta so. Amma kawai sai a nunawa mutum wata a cikin dangi a ce ya aure ta sai kuma a zo a yi ta rigima. Akwai wani ɗalibi a ƙasar waje yake karatu. Sai ya bugo mini waya, har kuka yake yi, cewa an tilasta masa ya auri wata kuma shi ɗin ba ya so. Ita ma ɗin ba ta so amma iyayen sun ce dole sai an yi. To ka ga wannan ba daidai bane. Sai ka zo a jefa ɗanka cikin matsala, ka sa ya riƙa jin

haushin ka. Ya riƙa jin haushin matar, su riƙa yi muku mumunar addu'a suna fatan ku mutu, domin kun kawo musu cikas a rayuwa. Ba laifi ka tallatawa ɗanka 'yar abokin ka, ko ɗan wani mutumin kirki da kake ganin ya dace ɗanka ya aura, sai ka tallata masa in ya gamsu ya aure ta. Amma ka zo kawai kace wai saboda abokinka ne sai kun takurawa 'ya'yan ku sun yi aure, to wannan ba daidai bane. Amma a iya yin kamfen. A sa ta yi kwalliya da ado. Wataran ku je gidan da abokin, ta kawo muku ruwa. Daga haka zai iya cewa "kai wannan 'yar ta ka ai mutuniyar kirki ce, inama ɗa na zai same ta." Shima ya ziga tasa ka ziga naka sai ku haɗa su da dabara. Idan kun basu dama kuka ga suna son juna shi kenan. Idan ɗaya ya kangare shikenan sai a nemar masa wata ita ma a nema mata wani.

Da haka ne malamai suka ce hanyar haɗa aure guda biyar ce:

1- Kai ka ga matar, wato kana binciken matar da za ka aura sai ka ga wata ta yi didai da wacce kake buƙata. To sai ka je ka gabatar da kanka wurrinta ko wurin iyayenta cewa kana so ko kana ciki. Sai ka tambaya cewa "za a bani dama in zo in gwada, in faɗi ni waye in an aminta da ni a aure ni?"

2- Ke kika ga namijin kuma za ki iya jin kin gamsu da shi. To sai ta turo ko ta aiko cewa "wane ina son ka in Allah ya yarda za ka aure ni". Ta bayyanar da kanta cewa "nice wacce, 'yar wane. Shekaruna kaza. Ilimi na a mataki kaza nake da shi." To idan ka gamsu kana son ta shikenan sai ka aure ta. Duka wannan an samu a zamanin sahabbai an yi.

3- Wani mutumin kirki ya gano ka ko ya gano ta, ya zo ya baka labari ko ya ba ta labari. Kamar yadda Haulatu bintu Hakim ta zo ta bawa Manzon Allah (SAW) labarin Nana A'isha da kuma Sauda, cewa bayan rasuwar Khadija wacce shekarun ta 25 da Manzon Allah (SAW) lokacin bai yi aure ba bai kuma yi mata saɗaka ba, sabodab ita Nana Khadija bata da kishiya. To bayan ta rasu sai ya zamo babu kowa a gidan Manzon Allah (SAW) sai 'ya'ya. Ba mace ko ɗaya, ba saɗaka, ba baiwa ba kuma kuyanga. To sai wannan Haulatu bintu Hakim tace "ya rasulallah na gano maka bazawara da budurwa, ko ka auri duka biyun ko ka auri ɗaya. Bazawarar ta yi imani da kai kuma akwai mijinta sunan sa Sakaranu, Allah ya yi masa rasuwa. Idan ka aureta ka ƙimanta ta domin ba za a walaƙanta ta a dangi a ce ta yi imanin banza ba. Gashi yanzu mijinta ya rasu ta tozarta ba. Ita kuma budurwar 'yar

abokin ka ce, wato Abubakar Siddiƙ. Idan ka aure ta zumuntar da ke tsakanin ku da shi za ta ƙara ƙarfi. Domin ga zumunta ta addini ga ta abota kuma ga ta surkuta ta shiga tsakani." Manzon Allah ya ga waɗannan dalilai da Haulatu ta gaya masa duka dalilai ne da ya kamata a dubasu kuma daga bisani ya amince ya auri waɗannan matan guda biyu. Ka ga kenan wani yana iya zuwa ya gabatar da wani.

4- Uba da kansa yana iya zuwa ya samu wani mutumin kirki da ya gamsu da shi ya ce idan kana buƙatar auren 'ya ta wance na baka. Kamar lokacin da Sayyidina Umar, lokacin da Nana Hafsa mijin ta ya rasu, 'yar Sayyidina Umar ce. Sayyidina Umar da kansa ya fito ya samu Sayyidina Usumanu, ya ce masa akwai 'ya ta, mijin ta ya rasu ta gama takaba, idan kana buƙatar aurenta na ba ka ita. Sayyidina Usumanu ya ce to shi a bashi lokaci tukuna ya yi nazari. Bayan 'yan kwanaki da suka haɗu ya cewa sayyidina Abubakar bani da buƙatar yin aure yanzu. Ka ga kenan ya riga ya ba da uzurinsa. Da ya ji haka sai ya tinkari Sayyidina Abubakar, ya ce masa "ga 'ya ta hafsa ta gama takaba bayan rasuwar mijinta. Idan kana buƙatar aure na baka ita." Sai ya yi shiru bai ce eh na karɓa ba, bai ce a'a ban karɓa ba. Sai bayan 'yan kwanaki kaɗan sai Manzon Allah ya turo ya ce yana so zai auri Hafsa. Bayan ya aureta sai suka haɗu da Sayyidina Abubakar da Sayyidina Umar. Sai Sayyidina Abubakar ya ke so ya ba Sayyidina Umar hanzari da uzuri a bisa rashin amsa masa buƙatar da ya kawo na ya auri 'yar sa da eh ko a'a. Ya ce "abinda ya sa ka ga kamar na yi maka shiru ban ce maka eh ba ko a'a lokacin da ka bijiro mini da maganar 'yar ka ba." Sai yace "gaskiya ne kuma ban ji daɗi ba, gara Sayyidina Usumanu shi ya ce mini ba ya buƙata amma kai sai ka yi tsit." To shine ya ce "dalilin da ya sa na yi tsit, a lokacin da ka kira ni kake tambaya ta game da auren, ni kuma mun yi Magana da Manzon Allah (SAW) ya ce mini yana so zai auri 'yarka Hafsat, to shi yasa ka ji na yi shiru.  Idan Annabi (SAW) ya aure ta, to ka gashi kenan buƙata ta biya. Idan ba za ka aure ta ba to ni ina sonta zan aura. To kuma bai kamata in gaya maka sirrin Manzon Allah (SAW) ba kafin ya tabbata." To ka ji a nan uba zai iya zuwa ya bijirar da 'yar sa ga wani. Kuma duka waɗannan abubuwa da muka faɗa babu wani ƙasƙanci a ciki.

5- Ana iya samun mai dalilin aure. Ka san muna da masu dalilin aure wato masu haɗawa. Wanda suma ɗin akwai gyare-gyare a cikin aabubuwan da suke yi amma dai akwai alheri da yawa domin wanin bai san yadda zai samu matar ba. Wata matar ba ta san yadda za ta haɗu da mijin ba. Amma za su karɓi hotunan matan, sai dai basa karɓar na mazan, matsalar su kenan. Ya kamata mazan ma masu neman aure su riƙa basu hotunan su. Yadda kai ya kamata a kawo maka hoton macen ka gani, ya kamata kuma mazan da kuke neman aure kowa ya je ya tsalla wanka ya ɗau hoto ya cakare hula, shi ma ya bayar da nasa hoton. Shima a kai wa matan da suke neman auren idan ta gani ta ce wane ya zo. Amma wannan shine gyaransu guda ɗaya. Gyaransu na 2 shine, wataran wasu mutanen ba auren ne a gaban su ba. To ya kamata su tabbatar cewa duk wanda suka ba shi hoton wata yarrinya to lallai maganar aure ce; ba maganar wasa a ciki. To wannan shine gyaran su guda biyu amma suna taimakawa ƙwarai da gaske wajen yin dalilin aure.

Itama mai neman auren ya kamata ta ga hotunan namijin. Sai a kai mata ta fara gani, idan ta gamsu itama ta je. Amma ba kullum za a riƙa zama matan kawai ake nunawa ba; suma mazan a riƙa nuna su. To wannan shine gyara wanda ya kamata su yi. Da kuma lura da cewa duk wanda suka ba hoto ko suka kai masa sun tabbatar mutumin kirki ne kuma auren zai yi. Domin wataran sun haɗa sun tafi sai kuma ka ga ba auren ne a gaban wanda aka haɗa shi da yarinyar ba kuma yana nema ya sa ta a wata hanya, wanda da yawa sun sha kawo mana irin waɗannan ƙarar. Sai mutum ya zo zance kuma sai ya riƙa miƙa hannu yana so zai taɓa wannan matar. Sai ta ce "a'a to ba aure ka zo ba?" to ka ga wannan ba daidai bane.

Akwai ma wacce aka ce mata wai ta kawo fasfo ɗinta za a fita waje tukunna. Ta ce "mu je waje mu yi me to, me za mu yi a waje ba tare da an yi aure ba?" Ka ga irin waɗannan duka sai an taka musu birki a cikin wannan harka ta haɗa aure. Sannan wani dalili yana iya sawa, kamar haɗuwa a wani wuri. Shima a iya tattauna wa- misali za ka ga wasu sun tura 'ya'yan su cikin dangi, ko idan an yi baƙi sai a sa yaran su kawo ruwa ko su kawo musu abinci. A nan wani yana iya sanin akwai yara a gidan nan da suran su. Idan wani yana buƙata sai yayi Magana. Ko a aiketa wajen dangi ko ta haɗu da wani wanda ko idan ta zauna a gida ba a sani ba.

Wasu kuma sukan ce "to ai malam kuna cewa mu 'yan matako zaurawa mu riƙa sanya hijabi muna rufe jikinmu muna lulluɓi da zai rufe jikinmu gabaki ɗaya. Mu kuma ba za a gane ko a banbanta mu da matan aure da waɗanda ba matan aure ba. Har wata ta taɓa bada shawara duk da ba mu yarda da shawararta ba, cewa me yasa ba za a bambanta hijabi ba ya zama matan aure a yi musu wata kala, zawarawa ma a yi musu wata kala, 'yan mata a yi musu wata kala. Yadda duk wacce ka gani da shiga iri kaza to budurwa ce. Idan ka ga wata da shiga iri kaza to bazawara ce. Idan ka ga wata da shiga iri kaza to matar aure ce. Saboda haka mun duba wannan mun ga yana da illa shi ya sa ba mu gamsu da wannan shawara ba.

Dalili, zai rika nunawa mutane irin rayuwar  da al'umma ke ciki. Ta yiwu wataran aka ga dandazom mata sun taso duk da hijabi irin na zawarawa, ka ga kawai kallon su za a riƙa yi cewa ga dandazon zawarawa nan. Ko kuma a zo taro ga mata da yawa a cakuɗe sai a ga kalar hijabin da ke nuna matan aure ya fi yawa ko wanda ke nuna zaurawa ya fi yawa ko kuma wanda ke nuna 'yan mata ya fi yawa. Sai muka ga dai babu hikima a cikin wannan shawara, shi ya sa ba a ɗauke ta ba, ba a yi aiki da ita ba.

Saboda haka ka ga shawara ce da ba za ta haifar da maslaha ba. Gara dai a ci gaba da bin hanyoyin da ake yi da na nunawa juna ma'aurata. Ko irin ƙungiyoyi haka a wasu ƙasashen za ka ga ana kafa wato wata cibiya ta haɗa aure, wacce gwamnati ta amince da ita, mutane sun amince da ita. Akwai ƙwararrun ma'aikata masu amana waɗanda mace za ta zo ta gabatar da kanta a yi mata intabiyu a tanbaye ta rayuwarta da komai a tabbatar ta cancanci aure. Shima namiji ya zo haka. Waɗannan cibiyoyi su haɗasu su yi magana a gabansu su tabbatar kuma su shaidawa iyayen cewa waɗannan ma'auratan sun cancanta su yi aure.

## Tambaya Kan Aure 04

Mun gabatar da abubuwa 8 zuwa yanzu. Abubuwa 3 matsalolin da suke tasowa mata dangane da aiki ko karatu ko kasuwanci, wanda ko wane a cikin abubuwannan uku muka yi bayanin abin da ke faruwa cewa idan mace tana yin aiki, to wata takan gamu da matsala na shugabanci. Ga shugabanta a gida wato

mijinta akwai ayyukan da yake so ta yi masa. Ga shugabanta a ofis wanda shima akwai ayyukan da yake so ta gabatar na ofis,. Wannan sai ya sa mace ta yi ta ƙoƙarin yadda za ta gamsar da guda biyun ba tare da ta samu matsala a gida da ofis ba. To wata rana sai ka ga abin ya haifar mata da ruɗani, da wahala da sauran su. Wanda muke ganin mata da suke aiki ya kamata su riƙa samun sassauci cikin wasu lamura domin suna da iyali kuma suna da rauni a daina ɗaukan su. Domin wani ya ce mini wai dokar aikin ce ita ba ruwanta da ko namiji ne ko mace ce. Kawai duk wanda ya shiga aiki za a lafta masa aiki kamar yadda ya kamata.

To ka gani, musamman aikin ɗamara da sauran su. To wannan ya sa da yawa matan basu iya yin wasu ayyukan ba da sauransu. Da kuma ya shafi ko ana buƙatar mata suyi. Tunda mun ce aikin nan ya kasu 3.  Akwai aikin mata zalla, su ya kamata a bari su yi. Kamar aikin ungozomanci, da wasu ayyuka da suka shafi tsaraicin mata, da lalurar mata ɗin da ya kamata a ce mata zalla ne suka ƙware a wannan fannin.

Akwai kuma aikin da ya kamata maza kawai su ƙware a ciki. Aikin da ya shafi maza ne kawai da alʼaurarsu da wasu abubuwa da ya shafi ɓangarorin maza kawai.. Sannan akwai aikin da mata suna iyawa maza suna iyawa. Kamar aikin koyarwa da wasu ayyuka waɗanda mata suna buƙata maza ma suna buƙata. Sannan haka wajen aikin akwai wanda ya kamata mace ta yi akwai aikin da bai kamata mace ta yi ba. Akwai kuma aikin da lallai sai mata ne za su yi. Amma kuma yana cin karo da addininsu da alʼadar su, da zamantakewar su. Saboda haka shine muke ganin ba za ka hana aikinsu gabaɗaya ba kuma ba za ka halatta shi bakiɗaya ba. Dole ka halatta shi wanda ya halatta amma da sharuɗɗa da dokoki da ƙaʼidoji na cewa dole a yi shi da kare mutunci da kuma shiga ta addinin Musulunci, da kamewa. Sannan kuma kada wannan aikin ya jawo ayyukan gida na kula da tarbiyar yara da haƙƙoƙin maigida da haƙƙoƙin gida su ruguje sakamakon fitar mace aiki. To wannan shima mun ce in za a auri mace mai yin aiki ana samun irin waɗannan ƙaʼidoji da ya kamata a tsaya a kula da su.

Hakanan mace mai kasuwanci, wacce ta shagala da neman kuɗi, itama wannan ana samun matsala. Idan ba a sa ƙaʼidoji na wane lokaci ya kamata a yi kasuwanci, wane lokacine bai kamata a yi ba kuma da wa za a yi kasunwancin kuma da wa take muʼamala, ina take zuwa kasuwancin, da wa za su tafi in fita waje ne da sauran su, to za a samu matsaloli. Aakwai maganar ʻmahramʼ wanda zai dinga

tafiya da ita. Ya kamata ya kasance yayanta ko ƙaninta ko wani wanda haramun ne ya aure ta; da shi ya kamata su riƙa tafiya yana taimaka mata. Da dai sauran abubuwa irin wannan.

Sai kuma mata masu karatu. Suma da matsalolin da suke fuskanta a wajen karatun, dangane da mu'amalar su ta karatun da ta gida. Da kuma abin da muka yi magana na cewa ya kamata hukumomi su kula da ma'aikata da kuma malamai waɗanda suke amfani da damarsu ta shugabanci ko ta koyarwa, su riƙa cin mutuncin mata ko suna neman mutuncin su ko suna so su ɓata su. In sun ƙi kuma su samu matsala a wajen karatu ko su samu matsala a waje aiki. Ya kamata a yi doka a majalisa wacce za ta kare haƙƙin mata a wajen aiki da kuma wajen karatu.

Sannan muka ce kuma akwai hanyar neman aure wanda mace tana iya gani ta ce tana so. Ana iya ganinta a ce ana son ta. Babanta ko ɗan'uwanta yana iya zuwa ya faɗeta ga wani mutumin kirki. Ko kuma wani shi yana da ɗa ya je ya gayawa wani cewa yana nema masa auren 'yar wane ya ga alamar in sun haɗu za a samu nagarta, sai ya shige gaba ya haɗa su. Ko kuma a ce masu dalilin aure, ko wasu santoci da cibiyoyi, ya zama an kafa wasu cibiyoyi na ilimi. Ba za mu bar ma kawai masu yawo da hotuna a jaka ko a buhu suna bi ofisoshi suna nuna wa maza hotuna mata tare da ba sa nuna wa mata hotunan mazan ba. Ko kuma basu san da wa za su haɗa suba. To wannan akwai buƙatar a kafa santoci masu zaman kansu wanda za su buɗe da ofis da komai da ID card da ɗaukar hoto da bincike a tabbatar ya cancanci ya yi aure, mace ma ta cancanta su haɗa su. To wannan shima duk abin da ya kamata ne, an yi shi da dama a ƙasashen duniya. Wasu ma har site suke da shi in ka shiga internet. Akwai zawaj.com, in ka shiga za ka ga form ɗin da za ka cike, za ka ga mace ta yi bayanin kanta mnamiji ya yi bayanin kansa yana neman aure har da tsawonsa da shekarunsa, da sana'ar sa da nauyinsa in ya hau sikeli. Da irin abinda yake so da wanda ba ya so. Da abinda ya fi so har a kalan abinci da kalar matar da yake so duk zai rubuta ya aika. Kamar yadda mutum yake gabatar da CV a wurin aiki. Hakanan itama mace za ta rubuta wannan. Misali ta ce ni 'yar ƙasa kaza, ƙabila kaza ce kuma ni Musulma ce. Ina neman miji wanda zai zamo tsawonsa bai wuce kaza ba, nauyin shi a silkeli bai wuce kaza ba, ya zamo kuma ba mai shan taba ko giya ba. Kuma ya zamo ba mai faɗa ba saboda ba na son faɗa kuma ya zamo ɗan gaye ba ƙazami ba. Kuma ya zamo albashinsa ya kai kaza. Ya zama yana da gidan kansa ko gidan haya, ko a ƙasa kaza ko a yanki kaza yake.

Duk za ka ga wannan bayanai idan ka shiga internet. Idan aka rubuta www.zawaj.com ko "seeking marriage", suna nan da yawa. To wannan ta ɓangaren abinda ya shafi abinda muka gabatar kenan na waɗannan abubuwa 8 na hanyoyin neman aure ko samun aure guda 5, da kuma matsaloli da mata suke fuskanta lokacin da suke kasuwanci ko suke aiki ko suke yin karatu.

Babu laifi a yi canjin yin aure wanda shi ba laifi bane idan dai za a yi sadaƙi. Kamar mutun ya auri 'yar wani shima kuma ya auri 'yarsa amma ba sharaɗi ba, kowa dai yana so ne. Idan an sa sharaɗi ka ga ya zamo kenan idan ka sako mai tasa sai ya sako ma taka, to kuma wannan ba shi ake buƙata ba. Idan ka ga 'yar mtum kana so kuma shima ya ga 'yarka yana so, kawai za a biya sadaƙin auren 'yarsa kuma a biya sadaƙin auiren 'yarka, babau laifi. Inda aka haramta shi shine 'Nikahus sigar', shine kawai ka ce bani 'yarka in baka 'ya ta babu sadaƙi a tsakani. Wannan suna yi a zamanin jahiliyya; kowa ya riƙe tasa kamar yadda in an ɓata ka sako tasa shima ya sako taka. To wannan shi ba a yarda da shi ba a shri'ar Musulunci domin dole za a cutar da ɗaya. Dole a samu ɗaya mai biyayya ce. Ka ga ta iya yuwa wacce aka bashin ita mai biyayya ce wacce ya bayar kuma bata da biyayya. Ko tasa ce mai biyayya waccan ba ta da biyayya. To ka ga idan sharaɗi ne nan idan an sako maka kaima za ka yi saki, to mai yuwa takar ce bata da kirki shi tasa tana da kirki. To wannan ya sa dole malamai suka ce ba za a yi haka ba domin zai haifar da matsala, kuma zai sa aure ya yi ta mutuwa, sannan kuma a yita walaƙanta na kirki ana ɗaga darajar waɗanda ba na kirki ba.

Malamai sun yi bincike sun gaya mana akwai mata 24 waɗanda haramun ne mutum ya aure su. Don haka idan mutum zai yi aure ta bangaren wannan sai ya bincika ya ga matar nan da zai aura ba ta cikin waɗannan mata 24, wanda asalin wannan aya ce a ciki Al Kur'ani da Allah SWT yake cewa....

Allah ta'ala yace "kada ku auri abinda iyayen ku maza suka aura na daga mata" - baban mutum ya auri mace sun rabu ko ya auri mace ya rasu ta gama takaba, ɗan sa ko jikansa ya fito ya ce yana son ta da aure- wannan an hana, haramun ne. "sai dai abinda ya gabata" wanda aka yi a baya. Allah yayafe wanda aka yi a baya a zamanin jahiliya. Sai ya ce .....

"yin haka alfasha ne, abin ƙi ne, kuma tir da wannan hanya" kenan ya saɓawa hankali, al'ada da addini. Sai Allah yace …..

“an haramta muku ku auri babar ku” ba zai auri babar babarsa ba, ba zai auri babar, babar, babarsa ba. Duka wannan dangi na babar sun haramta ga ɗa ya auri babarsa da babar babar sa. ‘‘an harramtawa mutum ya auri ‘yarsa’’ da ‘yar ‘yarsa, da ‘yar ‘yar ‘yar ‘yarsa har zuwa can ƙasa. Wannan layi gaba ɗaya mutum ba zai auri ko ɗaya daga ciki ba har abada. Domin da ‘yar ‘yarka da ‘yarka duk ‘ya’yanka ne. Don haka jikarka ma ‘yarka ce. Da ‘yar’uwar mutum’’. Idan an ce ‘yar‘uwa, wacce kuke uba ɗaya, uwa kowa da tasa, wacce kuke uwa ɗaya, uba kowa da nasa, ko wacce kuke uwa ɗaya uba ɗaya. To wannan ɗin mutum ba zai aureta ba har Abadan abada.

Ka ga mutum ba za a ce gashi da ƙanwarsa sun yi aure ba. Da ƙanwar uba ko yayar uba wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya da baban mutum, to wannan matar ko mutum ya girmeta ko ta girme shi ba zai aureta ba har abada. Ko shi wanda ya ke so ya aureta ɗin ta haramta a gareshi. Domin wataran sai ka ga ƙanwar baban naka ka girmeta, ka ganta ‘yar ƙarama kai babba, to duk dai ba zai aureta ba har abadan abada. Kenan ka ga ‘yar uwar uba, ƙanwar uba, yayar uba da suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya da baba to ɗan wannan mutumin ba zai aureta ba har abada.

Sai Allah yace da ƙanwar uwa ko yayar uwa wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya da babar mutum, wannan matar babu aure tsakaninsu da ɗan ƙanwarta ɗinnan da ɗan yayarta ɗinnan, wacce suke uba ɗaya ko uwa ɗaya, ko uwa ɗaya uba ɗaya da ita, to ɗanta ba zai aureta ba har abada, ko da kuwa ya girmeta ko ta girmeshi ko kansu ɗaya. Da kuma ‘ya’yan ɗan’uwa; ɗan’uwa iri 3 ne:

i- Akwai ɗan’uwanka wanda babanku ɗaya da shi, uwa kowa da tasa.

ii-Akwai ɗan’uwanka wanda uwarku ɗaya da shi uba kowa da nasa.

iii- Akwai ɗan uwanka wanda uwarku ɗaya ubanku ɗaya.

To wannan ɗan uwan, ‘ya’yansa da ya haifa, da jikokinsa-wato ‘yarsa da ‘yar ‘yarsa da ‘yar ‘yar ‘yarsa ko ‘yar ɗansa, to har abada ba zai auri ‘ya’yan wannan ba. Idan ma an yi auren aka gano to a rushe shi da gaggawa.

Da ‘ya’yan ‘yar uwa. Mutum yana da ƙanwa, ko yana da yaya wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya. Ko wacce suke uwa ɗaya uba ɗaya to wannan matar, kamar

yadda yake haramun ne ya aure ta, haramun nema ya auri to ʻyaʼyanta da jikokin ta, da jikokin jikokinta har abada. Idan ma an yi auren daga baya aka gano to a warware shi- ba za a ce an yishi ya daɗe an hahhaihu ba. Idan ma an yi to a ruguje shi saboda ba aure bane, ya ruguje kansa da kansa. Saboda haka mutum ba zai auri ʻyaʼyan ʻyarʼuwarsa da suke uwa ɗaya ko uba ɗaya, ko uwa ɗaya uba ɗaya ba har abada. To ka ga 7 kenan.

Da kuma iyayenku mata waɗanda suka shayar da ku. Idan aka ɗauki mutum aka kaishi wani gida ya sha nono a gidan, to wannan matar da ya sha nononta, itama da abubuwanta 7 da ya shafi irin wannan, ba zai aure suba har abada. Za mu yi bayanin kasha-kashe na shan nono ɗaya.

Da ʻyarʼuwar mutum ta shayarwa. Ita wannan matar da ta shayar da shi tana da ʻya, to wannan matar da ita da ʻyaʼyanta har abada wannan da ya zo ya sha nonon wannan matar, to ba zai aureta ba ba kuma zai auri ʻyaʼyanta ba waɗanda shayarwa ta haɗa su.

Sai Allah Ya ce da babar matar mutum. Mutum ya auri mace, to ba zai auri babarta ba. Da kuma agololin ku waɗanda suke cikin kulawarku ga matan da kuka tare da su. Mutum ba zai auri ʻyar matarsa ba. Mutum ya auri mace sai ta zo da ʻya sai Allah Ya yi mata rasuwa ko suka rabu, to ba zai auri wannan ʻyar da tazo da ita ba. Amma a nan akwai sharaɗi. Sharaɗin shine idan ya riga ya tare da uwar, to ba zai auri ʻyar ba. Misali uwar ya fara aura, da ya auri uwar suka tare, idan ya ga ʻyar ta ba zai ce yana so ba. Haka nan idan ʻyar ya fara gani ya aura, ba zai sako ta ya auri uwarta ba. Amma idan ya auri uwar, kafin su tare sai ya ga ʻyarta, sai ya ce ko za ta yarda a musanya, tunda bai riga sun tare a matsayin miji da mata ba- wato a musanya zuwa ʻyar, idan uwar ta yarda to za a iya warware auren tunda baʼa tare ba a koma kan ʻyar ta.

Amma da ʻyar aka fara ba za a dawo kan uwar ba. Hakana idan uwar aka fara, amma sai da aka tare da uwar, to ba za a dawo kuma kan ʻyar ta ba. Wannan matar ta riga ta fita daga layin aure a gurinsa har abada. Idan dai har ka auri ʻyar mace to kuma ba za ka dawo daga baya, ko kun rabu ko ta mutu, ka zo ka auri babarta ba; ba a yin haka. Hakama idan ka fara auren babarta har kun tare, to shikenan wannan har abada ba zaka aureta ba. Amma idan ba a tare da uwar ba, mutum ya ga cewa, ko uwar ta ga cewa to ni daman na fi son ʻyata ta samu miji, tunda ni Allah ya sa

na samu, ko zaka haƙura da aurena ka auri ʻyar tawa? Sai ka zo ka neme ta, idan ta amince a ɗaura muku aure sai a yi. To wannan malamai suka ce babu laifi.

Sannan sai Allah ya faɗi matan da suke sun haramta ga mutum ta ɓangaren nasaba; sune waɗannan guda 7. Ta ɓangaren shan nono suma guda 7. Ta ɓangaren surukuta su kuma guda 4. To ya za a yi mutum ya gane waɗanne mata ne suka halatta gareshi cikin matan da suke kusa da shi? ƙaʼida, dukkan matan da suke kusa da mutum, wato ʻyan uwansa kaf, bai halatta ya aure su ba sai ta ɓangare 4 kawai.

- i- ʻYa'yan ƙanwar baban mutum, ko yayar baban mutum wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya. Wannan ɗansa yana iya auren ʻyar ƙanwarsa ko ʻyar yayarsa wacce suke ko uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya. Shi ake kira auren zumunta ko ʻyaʼyan maza zur ko ʻyar namiji da ʻyar mace, wannan ana yi.
- ii- ʻYa ʻyan ƙanwa ko yayar babar mutum. Idan mutum yana da baba, ita kuma tana da ƙanwa ko yaya wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya, to shi wannan yana iya auren ʻyar ƙanwar babar tasa ko ʻyar ya babar tasa da suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya da babarsa. Maʼana dai ga mace da ƙanwarta ko da yayarta, suna iya haɗa ʻyaʼyan su aure. Shi ake kira ʻyn mata zur.
- iii- Ko ga namiji da namiji dukkanin su sun haifi ʻyaʼya, to suna iya haɗa auren ʻyaʼyan su ɗin. Amma su kuwa ba zai auri ʻyar ɗayar ba amma ʻyaʼyan su a junansu suna iya yin aure.
- iv- To haka nan mutum ba zai auri ƙaunwa ko yayar babansa ba amma zai iya auren ʻyar ƙanwa ko yayar babansa. Mutum ba zai auri ƙanwa ko yayar babarsa ba amma zai auri ʻyar ƙanwa ko ʻyar yayar babarsa. Kaga wannan shine auren ʻyan maza zur ko ʻyan mata zur ko ʻɗan namiji da ʻyar mace. To wannan sune waɗanda suka halatta dangane ga makusantan mutum.

To ita ɗin da aka ce ya halatta ya aureta, ko ʻyar ƙanwar baban mutum ko ʻyar ƙanwar babar mutum, ko ʻyar yayar baban mutun ko ʻyar yayar babar mutum. Waɗannan duk dai zai iya auren su. To idan bai aure su ba zai iya auren ʻyaʼyan su kuma. Tunda ita ya halatta ya aure ta, to yana iya auren ʻyar ta? Misali yaya da

ƙani kowa yana da ʻyaʻya, to sai ya zama shi wannan yayan shima ʻyarsa ta haihu, amma shi kuma ƙanin ɗa gare shi, kaga yayan yana da jika kenan, to ɗan wancan ƙanin zai iya auren jikar wannan yayan, ko ʻyar jikansa ma.. Kamar yadda ya halatta ya auri ʻyarsa, yana iya auren jikarsa ma. To wannan shine abinda ya shafi wannan.

To wata tambaya ita ce, mutum ya yi zina da mace ta haihu, wannan ʻyar tunda ba ta halal aka sameta ba shi wanda ya yi zinar matar ta haihu to yana iya auren ʻyarta?

To wannan matsalar a cikin mazhabar mu ta Malik akwai malamin da ke ganin tunda dai ba ʻyarsa ce ta halal a shariʼa ba, to yana iya aurenta. Amma dai mafi yawan malamai sun ce aʼa duk da ba ʻyarsa ce ta halal ɗin ba amma dai ta shiga cikin dandazon ʻwa banatikumʼ, saboda haka ʻyarsa ce dai ta saduwa da ɗaukan ciki amma shariʼa ce ba ta halatta ba. Tunda shariʼa bata halatta ba suka yi zina, to dai ʻyarsa ce sai dai a ce ʻyarsa ce ta zina. Ka ga Kalmar ʻya ɗinnan ba za ta gudu daga kanta ba. Tunda Kalmar ʻya ba za ta gudu daga kanta ba, dole ta shiga. Duk da bata da wasu haƙƙoƙi na shariʼa amma dai tana cikin ʻyaʼya. Suka ce waɗancan malamai da suka halatta wannan suma ba su bi tafarkin da ya kamata ba.

## Tambaya Kan Aure 05

To waɗannan sune ɓangarori guda 4 waɗanda suka haramta ga mutum ya auresu ta ɓangaren abinda ya shafi surukuta. Ka ga in ka faɗi waɗancan huɗun ka faɗi waɗannan ukun sun zama guda 7 kenan.

Guda 4 sune:

1- Matar baban mutum- baban mutum ya auri mace, ya tare da ita ko bai tare da ita ba, haramun ne akan ɗansa har abada ya aure ta.

2- Hakanan idan ɗa ya auri mace, ya tare da ita ko bai tare da ita ba, haramun ne babansa ya aureta har abada.

3- Babar matar mutum, bai halarta ya aureta ba. Da zarar ya auri ʻyar ta, an ɗaura aure, ko ʻyar nan ya tare da ita ko bai tare da ita ba, babarta ba zai aureta ba har abada.

4- Idan mutum ya tareda uwa, to ba zai auri ʻyarta ba har abada. Amma idan mutum ya ɗaura aure da uwa bata tare ba, ko ta rasu bata tare ba, saboda haka mutum zai iya auren ʻyarta. Amma idan ya riga ya sadu da babar to kuma har abada ba zai auri ʻyarta ba. Kaga 4 kenan.

Waɗannan guda 3 da za mu faɗa a kan huɗunnan su haɗa su ne ba a yi. Idan ware su aka yi sun halatta. Idan kuma an haɗa su sun haramta. Haɗa su a nan yana nufin a haɗa su a aure ba wai yana nufin haɗa su a gida ɗaya ba. Su waɗannan guda uku in an haɗasu a aure bai halatta ba. Amma idan aka fara auren ɗaya aka rabu da ita ko ta rasu za a iya auren ɗayar. Sune kamar haka:

1- Mace da ʻyarʼuwarta wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya. Ba za a haɗa su a aure ba. Amma idan ya saki wannan ta gama idda, ko ta rasu ya na iya auren yayarta ko ƙanwarta wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya. Ka ga wannan ana iya aurensu a ware, daban daban a lokaci daban daban amma a haɗa su a aure a igiya ɗaya lokaci guda mijinsu ɗaya, bai halatta ba.

2- Mace da ƙanwar babanta ko yayar baban ta wacce suke uwarsu ɗaya da babanta ko ubansu ɗaya da babanta, ko uwa ɗaya uba ɗaya da babanta. To suma waɗannan ba za a haɗa su a igiyar aure lokaci guda su zama matan mutum ɗaya ba. Amma idan ya saki yayar babanta ko ƙanwar babanta wacce suke uwa ɗaya uba ɗaya, zai iya aurenta idan ta gama idda ko idan ta rasu. Haka idan kuma ya rabu da ƙanwar baban nata ko yayar baban nata da suke uwa ɗaya uba ɗaya ko uwa ɗaya kawai ko uba ɗaya kawai, to zai iya aurenʻyar wannan mutumin da ya rabu da yayarsa ko ƙanwarsa, babu laifi wannan. To ka ga suma ana iya aurensu daban-daban, haɗa su ne ba a yi.

3- Haka kuma ba zai auro mace- yaya ko ƙanwar babarta da suke uwarsu ɗaya ubansu ɗaya ko uwa ɗaya ko uba ɗaya da babarta ba. Wannan ʻyar uwar babar tata, ko yayarta ce, ko ƙanwar ta ce ko uwa ɗaya ne ko uba ɗaya, ko uwa ɗaya uba ɗaya, duk dai ɗaya ne ba zai aure ta ba ya haɗa ta da ʻyar

yayarta ko ʻyar ƙanwarta, wannan ba zai yiwu ba. Amma idan sun rabu da ita ta rasu, to zai iya auren wannan.

Ka ga waɗannan sune guda 3 waɗanda su haɗasu ne ba a yi amma ana iya yin su. To waɗannan sune guda 7 da sun shafi ɓangaren abinda ya shafi surukuta.

To yanzu mun faɗi 7 mun ƙara faɗin wasu 7 ɗin, kaga ya zama 14 kenan a cikin 24 da muka yi bayani a baya. To sai waɗanda suka haramta ta wajen shayarwa, suma guda 7 ne. To  su waɗannan sune wanda ya tabbata a hadisin da Imamul Bukhari ya rawaito, mai lamba ta 5099 da kuma Imamu Muslim mai lamba ta 1444, Manzon Allah (SAW) yace....

"shayarwa ta haramta irin abinda haihuwa ma ta haramta". To wanene ya haramta, shine aka kalli waɗannan, wacce ta shayar da mutum. Idan mace ta shayar da mutum, to wannan mutumin da ya sha nononta, to babarsa ta shayarwa. Yadda ba zai auri babarsa ba, to ita ma wannan matar ba zai aureta ba. Ka ga ta zama babarsa ta shayar wa. Tunda ta zama babarsa ta shayarwa, to ka ga mijinta ma ya zama babansa na shayarwa. To tunda mijinta ya zama babansa na shayarwa, wannan matar ai tana da ƙanne ko yayye, ka ga sunansu ammomin babarsa na shayarwa. Don haka ba zai aure ta ba, ba kuma zai auri babarta ba domin babarta sunanta kakarsa ta shayarwa. Ka ga kakar babarsa ta shayarwa ba zai aureta ba domin ta zama itama a matsayi kakarsa.

To idan tana da yaya ko ƙanwa waccce suke uwa ɗaya kawai ko uba ɗaya kawai. Ko uwa ɗaya uba ɗaya, shi wannan ɗan ba zai je ya auri ƙanwar wannan matar ko yayar wannan matar da ya sha nononta ba domin ta zamo ammarsa ta shayarwa. Wato ta zamo ƙanwar babarsa ko yayar babarsa ta shayarwa.

To haka nan mijin wannan matar idan yana da yaya ko ƙanwa wacce suke uwa ɗaya kawai ko uba ɗaya kawai, ko uwa ɗaya uba ɗaya, wannan yaron da ya sha nonon matarsa, ba zai je ya auri yayar ko ƙanwar matar wannan mutumin ba domin sun zomo ammomin sa. Kamar yadda wancan suka zamo halolin sa, to waɗannan sun zamo halolinsa na shayarwa. Saboda haka ba zai aure su ba.

To idan wannan matar tana da ʻyaʼya ka ga sun zamo ʻyanʼuwansa na shayarwa. Sun zamo ʻyanʼuwansa na shayarwa ne saboda babar waɗannan yaran ta shayar da

shi. Saboda haka ya zama cikin iyalinta tunda ya sha nonon ta. To ʻyaʼyanta sun zamo ʻyanʼuwansa na shayarwa. Don haka ba zai auri ʻyaʼyanta ba. To su waɗannan ʻyaʼyan nata idan tana da su maza da mata, suma ba zaka hana su wata ƙila ko suna da ʻyaʼya ba. To ʻyaʼyan waɗannan ʻyan uwan nasa na shayarwa maza da mata wanda suke uba ɗaya ko uwa ɗaya, ko uwa ɗaya uba ɗaya da wannan matar, to ba zai auri waɗannan ʻyaʼyan ba da ʻyaʼyan su suma. Sun haramta a gare shi har abada.

Ka ga kenan irin abinda ya biyo shi na nasaba shine abinda ya biyo shi anan. To idan wannan matar tana da ʻya, ka ga ba zai aureta ba kuma jikarta ma ba zai aura ba. Ka ga sun zama guda 7 kenan. To duk ɗaya daga cikin waɗannan duk ba zai aure su ba. Ka ga anan kenan ya kamata a lura da hukuncin shayarwa. Mata za a je gidan biki ko a je gidan suna, ko a je wani taro yaro na kuka a ba wata mata ta shayar da shi. Ka ga dole a lura da wannan domin kada ta shayar da shi kuma wata rana aure ya zo ya shiga tsakanin su.

Sannan wannan hukuncin ya shafi shi kankin kansa ne yaron. Yayansa ko ƙaninsa wanda bai je wancan gidan ya sha nono ba, shi duk wanda yake so daga wannan matar - yayarta da ƙanwarta duka kamar sauran matan duniya ne a guruinsa. Kasancewar ɗanʼuwansa ya je gidan ya sha nono, to shi ɗanʼuwan nasa ne kaɗai ya shiga gidan. Amma shi hukuncin kowa bai hau kansa ba. Wansa ko ƙanin sa zai iya auren kowa yake so a cikin gidan. Duk ƙaʼidojin da suke akan wancan, game da bayyana tsaraici a wancan nasabar tasa suna nan a kana wannan. Yadda zai shiga wajen waɗancan haka zai shiga wajen waɗannan.

Shi ya sa kaga matsalar Salim lokacin da matar Abu huzaifa ta riƙe shi yana yaro, kuma bayan ya girma aka ce ba ɗanta bane, ba zai ci gaba da shiga gurinta ba. Sai ta zo ta gayawa Annabi (SAW) cewa gashi ta riƙe yaro, ta sha wahalarsa yana ƙarami, yanzu kuma gashi ya kai lokacin da zai roƙa taimaka mata, amma kuma bata hafe shi ba, ba ta shayar da shi ba. Ka ga kenan ba dalilin da zai shiga wurinta. Kuma wannan shine abinda muke nanatawa gameda abinda ke faruwa a garinnan namu. Za a ɗauko yaro daga ƙauye, ko a kawo shi aikatau gida tun yana ƙarami har ya saba da mutanen gidan. Sai ka ga har ya girma ya yi gemu, har ya yi ʻyaʼya yana cigaba da shiga tsakanin waɗannan matan. Yana ganin kwalliyarsu, wataran ma har da tsaraicinsu. Saboda abin da ake laʼakari ai a gidan ya girma, yaushe

kuma yanzu za a ce masa ya daina shigowa, ko idan zai shigo ya nemi izini a rufe jiki da al'aura, bayan ana ganin an zama ɗaya.?

To wannan ɓarnace. Babbar ɓarna ce kuma dole malamai da masu mulki da masu kuɗi da sauran al'umma duka muna cikin wannan matsala. Ka ɗauko wani, wataƙila ma ɗan yayanka ne ko ɗan ƙaninka ne. Kaga shi ɗan yayanka da ɗan ƙaninka bai halatta ya ga matarka ba saboda idan ka saketa zai iya aurenta. To tunda akwai wannan ka ga kenan bai kamata a saki abin ba ƙaidi ba. Kuma wata rana sai kaga tare da ɗanka suka taso suka girma. Yanzu idan sun taho za su shiga su gaida waccan babar tasu da ta riƙe su wanda shi ta haifi ɗanka ta shayar kuma da ɗanka, amma shi wannan bata haifi ɗan ka ta shayar da shi ba, amma ya girma a hannun ta. To a kaga idan ya zo zai shiga sai aka ce ya dakata, sai yayi mama ki y ace, "ya na girma a gida za a ce in dakata, kuma ya aka bar ɗan gidan ya shiga?" To wannan abun ne ya sa mutane suke bari irin waɗannan yara suna shigar musu tsakanin iyali saboda an riga an zama ɗaya. Kuma ba daidai bane ba, ba a zama ɗaya ba. Domin babu dalilin da zai shiga wurin matarka, alhalin ba ta haifeshi ba, ba ta shayar da shi nono ba kuma bashi da alaƙa da 'yan'uwanta wanda suka haramta ta aura. To wannan shine abinda yake faruwa. Kuma idan ka taka birkin wataran har zumunta sai ya shafa.

To shine matar Abu Huzaifa da ta gayawa Annabi (SAW) sai ya ce ta shayar da shi nono. Gashi kuma ya wuce shan nono har ya girma ya haddace ƙur'ani, ya yi gemu amma haka ta je ta bashi nononta ya sha domin a sauƙaƙa mata a yi mata ruhusa ta samu damar yin mu'amala da shi a matsayin ɗa. Saboda ta sha wahalarsa yana ƙarami kuma ba ta da wani ɗa sai wannan da ta riƙe ɗin. To shi yasa aka yi mata sauƙi. Ka ga kenan ashe hukuncin shayarwa yana bin wannan.

Kuma rashin bincike akan wannan matsalar yana jawo matsala. Akwai wani ango yayi amarya sai wata dattijuwa ta shigo wurinsu. Da ta gan shi sai ta gane wannan yaron ai ta shayar da shi da wannan yarinyar suna yara, kuma gashi sunzo sun yi aure. Ta gaya masa sai ya ƙi yarda. Sai ya taho wurin Manzon Allah (SAW). Sai ya ce, "ya Rasulallah ina zaune da matata, wata dattijuwa ta shigo ta ce wai ta shayar da mu muna yara." Sai Manzon Allah (SAW) ya ce "ya zaka yi tunda an faɗa. Ka je ja sake ta." Ka ga sai da aka yi auren aka gano an sha nono ɗin kuma ka zo aka raba wannan auren.

Sannan akwai wani abu da ake yi a duniya guda 3 wanda sai mun lura da shi. akwai bankin nono, akwai bankin jini, akwai bankin maniyi. Yanzu duniya ta kai sai mutum ya je a ɗebi maniyinsa a ajiye ko da akwai mai buƙata sai a bashi ko a bata. Wani irine sai ace shi iri ne, irin masu ƙarfi ne ko iri kaza ne. Wataƙila wata macen ba ta son haihuwa amma tana son ɗa. Ba ta son aure amma tana son ɗa, wannan ƙasashen kafirai sukeyi mu daman ba mu yarda da wannan ba. Sai kawai ta zo sai a ɗauki maniyin wannan da aka ajiye a bankin maniyi, sai a je a haɗa da maniyin ta sai ta samu ɗa.  To musulunci bai yarda da wannan ba. Akwai kuma bankin nono. Mata da yawa su kuma za su zo a tatsi nonon su a ajiye. Idan wata ta zo tana da buƙatar nono, za a ba ɗanta nono ko kuma ba ta da hali, to akwai banki da ake bada na gudunmawa da na sayarwa. Saboda haka sai ta je a bata nonon da za ta riƙa ba ɗanta anan. To kaga wannan shima akwai matsala ta ɓangaren hukunnce-hukuncen shari'a. Ba laifine a bada nonon ba, amma dole a kiyaye hukuncin bada shi- a asan na waye. Saboda a iyakance nasabar wannan yaro da kuma wacce ya sha wannan nonon nata. Dole a rubuta sunanta da adireshinta da inda take kamin a bawa wannan yaron nonon. Sai a ce wannan mata da ta bada gudunmawar nono aka ajiye ka zo ka sha to yanzu fa ta zama babar ka. Ka nemeta babarka ce ta shayarwa, kada ka aureta, kada kuma ka auri 'yarta da sauran duk abubuwa na hukunce-hukunce. To sai a gaya masa haka.

Sannan akwai bankin jini. To gara shi jini ba matsala tunda idan an ɗurawa mutum jinin mata ba ta haramta a gareshi ba. Yanzu mutum za a iya ɗiban jininsa a zubawa matarsa. Ko a ɗebi na matarsa a zuba masa. Wannan ko ba maganar haramci a ciki. Amma maganar maniyi da nono sune suke da wani hukunci na musamman wanda dole idan har za a yi ɗin to sai an sharɗanta hukunce-hukuncen su. Ka ga wancan daman a maniyi ɗin mu ba mu yarda da shi ba a musulunci domin babu aure tsakanin maniyi damaniyin da aka ɗauko aka haɗa. Kuma duka maniyin da aka haɗasu ba na aure ba aka samar da ɗa, to wannan ɗan bashi da hukunci na shari'ar musulunci.

Haƙiƙa malamai sun tattauna dangane da mas'aloli guda 3 wanda wannan mas'ala tana ciki.

1- Kafin ace mutum ya haramta ga mace saboda ya sha nononta, akwai wani adadi na shayarwa, ko kuwa babu wani adadi? Ko da a ce ɗigo ɗaya ne ya shiga bakinsa ya haɗiye wannan ta zama babarsa ta shayarwa? Ko akwai wani adadi na musamman da sai ya kai sannan ne shayarwa ta tabbata akan mutum?

2- Shayar da babban mutum. Shin idan babban mutum ya sha nonon mace, shima hukuncin yana nan akansa ko baya nan a kansa? Wanda waɗannan mas'aloli guda 2 suna ɗamfare da juna.

3- Idan nonon tatso shi aka yi a cikin kofi, sai kuma aka zo daga baya aka bawa yaro, to shima hukuncin yana nan ko kuwa sai in ya sa bakinsa ya tsotsa da kansa?

Waɗannan sune mas'aloli guda 3 da suke da alaƙa da maganan shayar wa da muka yi.

Dangane da adadin abinda mutum zai sha kafin ya zama matar da ya sha nononta ta haramta a gare shi, malamai sun yi saɓani akan wannan matsalar. Wanda har an samu maganganu da yawa amma maganganun da suka fi rinjaye a ciki ko aka fi faɗa a ciki sune maganganu guda 4

1- Malaman da suke ganin, ko sau 1 mutum ya sha nonon nan, domin akwai banbanci tsakanin tsotso ɗaya da kuma ƙoshi ɗaya. Abinda ake nufi da tsotso ɗaya shine yaro ya kafa kai ya tsotsa kawai sai a fincike shi. Da kuma in ya kafa sai ya ƙoshi ya saki da kansa. Wannan shi ake kira shayarwa. Amma tsotso ɗaya shima hukuncin sa daban wanda za mu ji duk a cikin wannan bayani.

To malaman farko suna ganinn cewa idan mutum ya sha nonon mace sau 1 tak, to wannan matar ta haramta a gare shi. Ta zamo babarsa ta shayar wa. Waɗanda suka tafi akan wannan magana akwai Malam Abu Hanifa, Imamuna Maliku, akwai wata ruwaya daga malam Ahmad ɗan Hambali, da wata Magana daga malam Sa'id bn Musayyib, da wata magana daga malam Hasanul Basari, da malam Zuhri da malam Katada da malam Auza'i da malam Sauri da malam Laisu. Wannan

dandazon tawaga ta malamai wanda sune jamhuru, sun tafi akan cewa idan mutum ya sha nonon mace sau ɗaya to ta haramta a gare shi. Sun kafa hujja da inda Allah ke cewa....

A-Suka ce Allah Ya ce "da babar ku wacce ta shayar da ku da kuma 'yar'uwarku ta shayarwa". Ka ga anan Al ƙr'ani bai faɗi adadin shayarwa ba , kawai sai ya ce wacce ta shayar da ku. Saboda haka komai yawansa, komai ƙarancinsa, shikenan wannan mutumin ta zama babarsa ta shayarwa.

B- Sun kafa hujja da wani hadisi wanda Manzon allah (SAW) ke ce wa, "haƙiƙa shayarwa daga ƙoshi take" wanda Imamul Bukhari ya rawaito shi mai lamba ta 5202, Imam Musli ya rawaito shi a hadisi mai lamba ta 1455... wato sai lokacin da kake bukatar maman, wato idan mutum ya sha shike nan ya shiga cikin haramci. Saboda yana da buƙatarsa sosai. Saboda idan ya sha lokacin da yake ƙarami maman yake buƙata, idan ya sha ya shiga cikin haramci. To ka ga yana yunwar wannan maman kenan.

C- Sun kafa hujja da hadisin da Immul Buhari ya rawaito; wanda yake cewa "ya haramta daga shayarwa abinda yake haramta daga nasaba". Suka ce wannan dalili ya nuna Annabi (SAW) bai bambance ko ya faɗi wani adadi na musamman ba.

D- Sun kafa hujja da hadisin Uƙbatu bn Haris da yake cewa, "na aurii wata mata, sai ga wata mata baƙa ta shigo cikin gidana. Sai tace ai kuna yara ku biyunnan na shayar da ku. Sai na tashi na je na samu Manzo Allah (SAW) na ce masa, na auri wance, 'yar gidan wane amma sai wata mata baƙa ta zo ta ce mana ta shayar damu muna yara, da ni da amaryar tawa. Kuma na san ƙarya take yi." Sai manzon Allah ya kau da kai bai kalleshi ba. Sai ya sake zuwa ta ɗaya fuskar da Manzon Allah (SAW) ya juya fuska, ya je ta can ya ce "ya Rasulallah , matarnan da ta ce ta shayar da mu ni da amarya ta muna yara ƙarya take yi."sai Manzon Allah (SAW) ya ce masa "yaya zaka yi bayan ta riga ta faɗa?" Saboda haka sai ka saki wannan matar. Wannan hadisin Imamaul Buhari ya rawaito shi da Imamu Tirmizi da imamu Nisa'i. Wannan shine hujjarsu ta 4 kan cewa wannan shayarwar ka ga ba a faɗi sau nawa ta shayar da shi ba.

E- Duk wata ruwaya da ta zo da maganar adadi, wanda za ta zo a gaba, akwai saɓani ma a cikin adadin. Wani ya ce kaza, wani ya ce kaza. Don haka idan aka yi saɓani akan adadi sai a koma kan mafi ƙarancin adadi wanda shine ɗaya, tunda daga nan ake fara lissafi.

F- Sun rawaito daga Amru bn Dinar yake cewa ya ji Abdullahi ɗan Umar ya ce wani mutum ya  tambaye shi cewa shi sau 1 ko sau 2 ne yake haramtawa mutum ya auri mace ko kuma mace ta zama babarsa ta shayar wa? Ya ce "ai mu ba mu san 'yar'uwar da kuka sha nono ɗaya da ita ba face haramun. Kawai duk 'yar'uwar da kuka sha nono tare da ita ya zama haram ka aure ta. Ba ruwan mu da cewa sau nawa aka sha. Ya ce wannan shine abinda muka tabbatar da shi. Kuma sai wani yake ce masa to ai na ji Ameerul Muminina, wato yana nufi Abdullahi bn Zubair shi yana cewa ba haramun bane idan mutum ya sha nonon mace, ko yaro ya sha nonon mace, don ya sha sau 1 ko sau 2. Sai Abdullahi bn Umar ya ce hukuncinn Allah ya fi alheri daga hukuncin wannan sarkin naku.

G- Suka ce abinda yasa aka haramatawa mutum macen da ya sha nononta, ai da kaɗan da mai yawa duka ɗaya ne, tunda dai an ce haramci. Saboda haka ba maganar a ce nono sai an sha mai yawa ko an sha kaɗan. To menene babancin mai yawa da kaɗan? wanda ya sha mai yawa da wanda ya sha kaɗan dai duk sun sha nono. Saboda haka asalin matsalar guda ɗaya ce. Yawan nonon da kuma ƙarancinsa abu ne da ba za a iya iyakance shi da wani lokaci ko wuri ba. Don haka wannan shine hujjar malaman da suke ganin idan ma sau 1 yaro aka kaishi ya sha nono a wani gida, to wannan matar duk hukuncin da muka faɗa a baya na cewa ta zama babar a, mijinta ya zama babansa 'ya'yan matar sun zama 'yan'uwansa na shayarwa, 'ya'yan sa sun zama 'ya'yan 'yan'uwansa na shayarwa. Yaya da ƙanwa na wannan matar wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwa ɗaya uba ɗaya sun zamo halolin sa na shayarwa.  Hakanan kuma yaya ko ƙanwa na mijin wannan matar da ya sha nonon su, shaƙiƙiyar a ko liabbiyar sa ko liummiyar sa ta zamo 'ya'uwar babansa na shayarwa. Yadda ya haramta ya auri waɗanda suka haɗa nasaba da shi ta waɗannan ɓangarorin, to waɗanda ya sha nononsu ma ta waɗannan ɓangarorin ba zai aure suba, indai har ya sha wannan nonon.

Malamai na biyu suka ce a'a sai idan shayarwar nan ta kai sau 3. Don mutum ya sha sau 1 ko sau 2 ba za a ce wannan matar ta haramta a gareshi ba. Sai idan an sha nonon wannan matar sau 3 sannan ne wannan hukunci ya tabbata a kan sa. Akwai

wata ruwaya daga Imamu Ahmad da kuma malaman Zahiriyya banda Ibn Hazamin, kuma wannan shine ra'ayin malam Ishaƙu, da malam Abu Ubaida da malam Sauri da malam ibn Munzir. Hujjarsu shine Manzon Allah (SAW) ya faɗa a wani hadisi cewa tsotso 1 ko tsotso 2 ba ya haramtawa mutum wata mace ko ya ci gaba da mu'amala da ita. Wanda wannan hadisin Imam Muslim ya rawaito shi a hadisi mai lamba ta 1450 da malam Abu Dauda a hadisi mai lamba ta 2063 da Tirmizi a hadisi mai lamba ta 1150, da Imamun Nisa'i da ibn Maja a hadisi mai lamba ta 1941. Suka ce wannan shine hujjarsu ta cewa idan mutum ya sha nono sau 1 ba za a yi masa wannan hukuncin ba. Sai an kaishi raino gidan ya sha nonon sosai sannan ne ya shiga ciki. Amma, tsotsa 1 ko tsotsa 2 ba za ta shigar da shi ciki ba. Sai an yi abun da niya kuma an kai mutum shayarwa. Yanzu kaga Annabi (SAW) an kaishi shayarwa wajen Suwaibatul Aslamiya. An kaishi shayarwa wajen Halimatu Sa'diya, to ka ga wannan an yi shi da niyya kuma  an sha nonon da yawa; ba sau ɗaya aka sha ba. Suka ce to wannan shine hujjar su ta farko. Hujjar su ta biyu hadisin Ummul fadli, cewa wani balarabe ya shigo wajen manzon Allah (SAW) lokacin Manzon Allah yana ɓangarenta a ɗakinta, sai ya ce "ya Annabin Allah ina da mata sai na auro wata ta biyu. To sai wannan matar tawa ta farko take cewa ta shayar da wannan matar tawa ta biyu, ka ga za ta rushe masu aure. Amma sau ɗaya ta shayar da ita wai ko sau biyu? Sai Manzon Allah (SAW) ya ce tsotso ɗaya da tsotso biyu baya haramta wa. Tunda dai ta ce sau ɗaya ta shayar da amaryarka ko sau biyu to wannan ba zai sa a saki wannan amaryar taka saboda matarka ta shayara da ita ba. Wannan hadisi shima yana cikin sahihul Muslim da Imamu Ahamad a cikin Musnad  da kuma Imamul baihaƙi ya ruwaito shi. Don haka wannan hadisi ne ingantacce wanda ya nuna haka.

Sannan hujjar su ta 3 suka ce, ai abinda ake la'akari da shi shine adadi da maimaitawa. Saboda haka ai ba za a ce wanda yayi tsotso ɗaya ya sha ba, sai dai a ce ya yi tsotso ɗaya ba a kira shi da sha ba. Sai dai a kira shi tsotso tunda bashi da yawa. To shine hujjar su.

Sannan malamai na 3 suka ce lallai sai an samu shayarwa daga 5 zuwa sama, kaga adadin ya ƙaru. Masu adadin ɗaya, da masu gani sai ya kai 3 da masu ganinn sai ya kai 5 zuwa sama. Daganan ne hukuncin haramci ya shiga tsakanin su da wannan mata. Wannan shine mazhabar Malam Shafi'i, da kuma wata shahararriyar magana daga Imam Ahmad bn Hambal da ibn Hazamin da malam Aɗɗa'u da malam

Ɗawusu. Kuma an rawaito irin wannan ma daga Nana A'isha da Abdullahi ɗan Mas'ud da Abdullahi ɗan Zubair. Sun kafa hujja da hadisin Nana A'isha cewa farkon abinda aka saukar na Al ƙur'ani, shayarwa 10 sananniya tana haramtawa yaro ya auri mace. Sannan sai aka soke wannan aka yi nuskin wannan cewa idan aka sha sau 5 ma, indai sannaniyar shayarwa ce. Wato an kai yaro da nufin a shayar da shi, kuma sai aka ga a shayarwar  ta kai 5, to wannan ya haramta ya auri wannan mata. Tace wannan abin har Allah Ya karɓi ran Annabi (SAW) yana cikin abinda ake karantawa na Alƙur'ani wanda an soke tilawarsa amma hukuncinsa yana nan kamar yadda ya zo a sahihu muslim, hadisi mai lamba ta 1452 da kuma ruwayar Abu Dauda me lamba 2062. Don haka su masu ganin sai shayarwa ta kai 5 wannan shine hujjar su.

Shine malam Imam Nur ya ƙara sharhi a wannan hadisi yake cewa, abinda ake nufi da cewa an soke wannan shayarwa 10 an mayar da ita 5, shine abinda ya zo daga ƙarshe. Amma idan shayarwar ba ta kai 5  ba shikenan. A cikin dangogin 'ahkamun naski', akwai inda ake soke tilawa a bar hukunci. Akwai inda ake sole hukunci a bar tilawa. Akwai inda ake soke tilawa da hukunci. Akwai kuma inda akwai tilawa akwai hukunci. Waɗanda suka karanta Ulumul Kur'an ɓangaren ilimin 'An'naskh' sun san waɗannan ƙa'idoji da waɗannan bayanai duk da akayi akan ayar.....

Sannan sun kafa hujja da cewa ya zo a cikin wasu ruwayoyin. Sannan sun kafa hujja cewa ya zo a cikin ruwayoyin Nana A'isha na Hadisin Sahlatu bin Suhail, cewa Manzon Allah ya ce mata "ki shayar da Salim sau biyar daga nan ne zai zama ɗanki wanda zai dinga shiga wurinki" , wanda za mu yi bayani akan shayar da babba. Babban mutum da gemu da komai ya zo ya sha nonon mace wanda shine tambayarka ko wannan matar ta zamo babarsa ta shayarwa ko ba ta zamo ba.

Na 4 sune malaman da suke ganin ba yadda za a yi yaro ya haramta ga mace sai idan ya sha nononta sau 10 ko fiye da haka. Wannan shima an rawaito daga Nana A'isha da Nana Hafsa, cewa Nana A'isha uwar muminai ta aika da shi Salim cewa ana shayar da shi lokacin zuwa ga 'yar'uwar ta da ake kira Ummu Kulsum ta Sayyidina Abubakar. Itace kamar za mu ce, 'yar autar Sayyyidina Abubakar, wacce bayan rasuwarsa aka haife ta. Dama Sayyidina Abubakar 'ya'yansa guda 6 ne- maza 3 mata 3. Akwai Abdullahi ɗan Sayyidina Abubakar, akwai Abdulrahman

ɗan Sayyidina Abubakar, akwai Muhammad ɗan Sayyidina Abubakar. Akwai kumma Asmaʼu, akwai Aʼisha to sai wannan Ummu Kulsum ɗin. Itace wacce lokacin da aka haifeta ya riga ya rasu.

To shine sai Nana Aʼisha ta turawa ita wannan ʻyarʼuwar tata wani yaro yana ƙarami ta ce ki shayar da shi saboda idan ya girma zai dinga shigowa wurina ina koya masa ilimi. Sai aka tura shi lokacin ita Ummu Kulsum ɗin tana shayar da ɗanta. Ta ce ki shayar da shi sau 10. Domin ya samu damar ya riƙa shigowa wurina ya zama kamar ɗa na wanda zai dinga shigowa wurina. Sai Ummu Kulthum ta shayar da shi sau 3. Sai rashin lafiya ta same ta, bata ci gaba da shayar da shi ba sai iya waɗannan guda 3. Don haka saboda wannan ne ya zama baya shiga wajen Nana Aʼisha sai da hijabi. Ba ta bari ya shigo wajenta saboda bai riga ya cika sharaɗin guda 10 da zai zama ɗanta ba. Wannan shine ita mazhabar Nana Aʼisha kenan. Kaga shyarwar sai ta kai adadin da ake buƙata. Domin ga wani ʻyarʼuwarta ta shayar da shi sau 3, amma ba ta gamsu ya shigo gurinta da wannan shayarwar ba saboda adadin bai cika ba. Wannan hadisi sahihi ne, yana nan a cikin Muwaɗɗa Maliki, haka Malam Abdulrazaƙi ya rawaiyo shi a cikin Musannaf. Hakanan imam Baihaƙi ya rawaitoshi a cikin Sunan.

Sannan hujjar su ta 2 mai cewa, shayar wa sai ya kai 10 shine hadisin Safiya ʻyar Abu Ubaid, matar Abdullahi ɗan Umar. Cewa Hafsa uwar Muminai ta aika mata da Asim ɗan Abdullahi ɗan Saʼad zuwa ga ʻyarʼuwarta Faɗima bint Umar bn Khaɗɗab cewa ta shayar da shi sau 10 domin ya samu damar shigowa gurin ta. Sai ita kuma ta shayar da shi sau 10. Sakamakon ya sha nonon ʻyarʼuwarta sau 10, sai ta bashi dama yana shigowa gurinta a matsayin ɗanta na shayarwa. Suka ce to ka ga wannan a cikin waɗannan bayanai ya nuna kenan malamai sun kasu kashi 4 dangane da masʼalar adadin shayarwa.  Jamhuru, wato mafi yawa sun tafi akan cewa ko sau 1 ne aka sha nonon nan, to wannan matar ta zama babarsa ta shayarwa, ʻyaʼyanta sun zama ʻyanʼuwansa na shayarwa, waɗannan ʻyaʼyan waɗannan ʻya'uwansa na shayarwa sun zama ʻya'yan sa na shayarwa. Kamar yadda ya haramta ya auri waɗanda suka haɗa nasaba da su a wannan ɓangaren, hakanan suma ba zai aure su ba, saboda shan nonon da yayi na gidan su.

Sannan sai malaman da suke ganin aʼa daga 3 ne zuwa sama. Sai masu ganin daga 5 zuwa sama, sai masu ganin daga 10 zuwa sama. To idan an tattara waɗannan

mazhabobi guda 4, wacce mazhabar ta fi rinjaye? Mun ga mazhabar farko da ba ta kawo adadi ba, malaman da suke kanta sun fi yawa. Inda zaka yi hukunnci da yawa to zaka ce waɗannan su suka fi yawa, ko kuma sune suka fi rinjaye dangane da yawan malamai waɗanda suke kan wannan mazhaba. Amma wasu malamai sun fi ɗaukar mazahabar sau 5 ɗin saboda wannan aya da aka soke tilawarta aka bar hukuncinta. Ka ga wannan shine abin da zai nuna cewa kamar su sun yi aiki ne da abinda aka saukar na daga sama na Al Kur'ani wanda yake an soke tilawarsa amma an bar hukuncinsa. Don haka suka ce ta ɓangaren dalili, wannan ya fi ƙarfi. Amma ta ɓangaren yaɗuwa da kuma gamsuwa da malamai suke kai shine shayarwa ba tare da an yi mata adadadi ba matuƙar yaro ya sha nono ya ƙoshi. To kawai wannan hukunci ya riga ya ritsa da shi cewa ya zama cikin waɗanda suka sha nonon wannan mata kuma dole ya karɓi wannan hukunci.

Sai ta ɓangaren Magana kan ko daga wane shekaru ne wannan hukunnci ya fara. Yanzu babban mutum ne sai ya sha nonon matarsa. Bakinsa ya tsotsa kuma ruwan nonon ya fito ya shiga cikinsa. Ka ga ai matarsa ce, shi kenan sai muce ya sake ta ko yace baba ina kwana? To wannan shine mas'alar da malamai suka ja  gwauron nunfashi na ilimi da tattaunawa ta basira da ilimi da fahimta dangane da wannan mas'ala. Har aka samu cikin maganganun su 3 sun fi shahara. Na farko shine wanda suke ganin shayarwa wanda zai zama haramun mutum ya auri mace shine lokacin shekara 2. Tunda Allah Ya ce da cikisa da yayen sa watanni 30. A wani gurin yake cewa yayensa shekara 2 ne. Wato mutum a shekara 2 ake yaye shi. To tunda ana yaye mutum ne a shekara 2, wata 24 kenan. Kamar yadda Allah ya faɗa a wata ayar kuma cewa wacce ta haihhu tana yaye abinda ta haifa a cikin she karu 2 cikakku, ga wacce take so ta cika shayarwar. Ka ga kenan dole yaro ya zamo an shayar da shi a shekara 2. Da an yaye shi duk abinda zai sha ba sunansa shayarwa ba, sunan sa abinci.

Saboda haka waɗannan malamai kashi na farko suka ce duk abinda aka shayar da yaro matuƙar ya haura shekara 2, to wannan ba za a ɗauke shi a matsayin shayarwa ba. Amma kafin shekara 2 duk wacce ya sha nononta to ta shiga ciikin lissafin wacce za a lissafa ta a matsayinn babarsa ta shayarwa. To cikin masu wannan ra'ayi akwai mazhabar Imamauna Maliku, akwai malam Shafi'i, akwai malam Ahmad, akwai malam Ishaƙ da malam Abu Saur. Da wasu manyan almajiran malam Abu Hanifa da malam Auza'i. idan ma muka duba cikin sahabbai,  za mu

ga sayyidina Umar da ɗansa Abdullahi da malam Abdullahi ɗan Mas'ud da malam Abdullahi ɗan Abbas da malam Abu Musa al Ash'ari. Kai da dukkan matan Annabi (SAW) in ka ɗauke Nana A'isha ita kaɗai, tana da tata mazhabar, duk sun tafi akan cewa shayarwa shekara 2 ne. Duk wanda ya haure shekara 2 an riga an yaye shi ya fara cin abinci. idan wata mace ta zo ta bashi nono, to kawai abinci ta bashi, domin baya buƙatar nonon a wannan lokacin saboda yariga ya fara cin abinci. Saboda haka ba shayarwa sunan wannan ba cin abinci sunan sa.

Masu wannan ra'ayi sun kafa hujja da ayoyi da hadisan Manzon Allah (SAW). Daga ciki akwai wannan aya da muka karanta ta suratul baƙara aya ta 233, inda Allah SWT yake cewa iyaye mata, waɗanda suka haifi 'ya'ya su shayar da su shekaru 2 cikakku ga wanda yake so ya cika shayarwa. Don haka suka ce kun ga anan Allah Ya riga Ya sawa shayarwannan iyaka.

Sannan na biyu akwai hadisin Nana A'isha da wani mutum ya shigo wajen ta sai fuskar Manzonn Allah ta canza. Manzon Allah bai ji daɗi da wannan ya shigo masa gida ba. Sai Nana A'isha ta ce ai ɗan'uwana ne. sai Manzon Allah ya ce ku bincika ku tabbatar su waye 'yan'uwanku, domin shayarwa sai lokacin da mutum y ake ƙarami, wato lokacin yana buƙatar nonon, sannan neza a yi maganar shayarwa.

Sannan suna kafa hujja da hadisin Ummu Salma inda suke cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce ba abinda yake haramtawa mutum dangane da shayarwa sai abinda ya ƙosar da shi- wato ya cika uwar hanjinsa na daga nono. Kuma wannan yana kasancewa ne kafin a yaye mutum. Sun kafa hujja ne da hadisin Abdullahi bn Dinar wanda yake cewa "wani mutum ya zo wajen Abdullahi ɗan Umar muna tare a lokacin, yana wani guri da ake kiran sa 'Dadul ƙada'. Yana tambaya game da shayarwar babba." Sai Abdulllahi ɗan Umar yake ce masa "wani mutum ya zo wajen Umar yake ce masa ina da wata baiwa. Na kasance ina kwanciya da wannan baiwar tawa. Sai matata ta lallaɓa ta je ta kamo wannan baiwar ta ba ta nononta ta sha. Da baiwar nan ta sha nono, ni kuma na shigo wajen baiwata, sai ta ce mini "na gama da kai." Na ce me ya faru? Sai ta ce "na shayar da ita, yanzu ta zama 'ya ta. Ka ga ba ka da iko ka je mata kenan." Sai ya zo ya samu Sayyidina Umar ya gaya masa. Sai Sayyidina Umar ya ce masa "ka je ka jewa baiwarka. Wannan abin da ta yi, ai shayarwa anayinta ne lokacin mutum yana yaro. Saboda haka ka ga

Sayyidina Umar mazhabar sa idan aka shayar da babba nono ba za a yi hukunci da wannan ba.

Hakanan Abdullahi ɗan Umar yake cewa babu shayarwa sai ga wanda yake buƙatar shayarwar  yana yaro. Idan an shayar da babba nono to kamar ya ci abinci ne kawai. Saboda haka ne ma wani malami yake cewa ko fura sai a dama da shi. Don hukuncinsa ba daidai yake da na maganar shan nono a shayar wa ba.

Tambaya kan aure 07

To sai malamai na uku da suke ganin cewa ko baban mutum ya sha nonon mace, to wannan matar ta zama babarsa. Don haka masu wannan raʼayi suna gargaɗin mutumin da zai sa nonon matarsa a bakinsa ya tsotsa. Cewa da ya tsotsa shi kenan aure ya mutu. Sai mace ta kwashe kayanta saboda yanzu ta zama babarsa ta shayarwa. Sai ya riƙa durƙusawa yana gaishe ta a matsayin uwarsa. Masu wannan raʼayi akwai su malaman Zahiriya- akwai malam Aɗɗaʼu akwai malam Laisu, kuma Nanan Aʼisha ma tana yin fatawa da wannan. Dama munc duk matan Annabi (SAW) sun tafi a kan cewa daga shekara 2 shayarwa wacce za ta haramta wa mutum ya auri mata ko ʻyanʼuwanta ko abinda ya yi kama da haka ta ƙare. Amma idan an haura haka shikenan ko an shayar da yaro ba za a yi musu hukunci da wannan shayarwar ba. Amma ita Nana Aʼisha tana ganin ko babba ne ya sha nono to shima ya shiga cikin wannan. Ita hujjarta itace hadisin Sahalatu bint Suhail. Ita wannan mata Sahalatu bintu Suhail mijinta ya kawo mata wani yaro da ake kiran sa Salim maula Abi Huzaifa, tun yana ƙarami ɗan ƙanƙani ya bata shi ta riƙe shi. Ita kuma ba ta taɓa haihuwa ba. Sai ya zamo wannan ɗan da shi ta dogara. ta raine shi har ya girma a hannunta. Kuma tunda mahaifinsa ba sananne bane sai ake dangana shi ga mijinta- ake kiransa Salim ibn Abi Huzaifa. Da aya ta sauka aka ce ...

“Kowa a kira shi da sunan mahaifinsa, shi ne ya fi adalci a wurin Allah”, wanda ya haifi mutum a jingina masa ɗansa. Bai kamata wani ya zo ya ƙwace maka ɗa ya riƙa jingina shi zuwa ga wani ba. Har hadisi ya zo cewa, wanda yake jingina kansa zuwa ga wanda ba babansa ba, ba zai ji ƙamshin aljanna ba. Domin butulci ne mutum ya haifeka amma ka cire sunansa ka riƙa anfani da sunnan wani daban. Ko babanka gyattai ne, ko babanka wanne iri ne, ko musulmi ne ko ba musulmi bane,

ka dai dangana kanka ga baban ka shine daraja. Domin Sahabbai bayan sun musulunta, akwai iyayensu da yawa sun mutu a zamanin jahiliyya amma basu daina amfani da sunayen waɗannan iyayen ba. Sun ci gaba da amfani a matsayi mahaifansu. Addini shiriya ce ta Allah. Ɗa ya zama yana wani addini, uba ya zama yana wani addini, wannan daga Allah ne. Amma duk wanda Allah ya sa ka fito ta hanyarsa, ko mutumin kirki ne ko ba mutumin kirki bane; ko musulmi ne ko ba musulmi bane bai halatta ka cire wannan nasabar; ka daina danganta kanka gare shi ba. Saboda haka ne sai ya zama yanzu dole a kira shi da sunan mahaifinsa. Sai Allah Ya ce...

"Idan ba ku san iyayensu ba, sun zamo 'yan'uwanku na addini kuma sun zamo barorin ku". Saboda haka shi ya sa ake kiransa Maula. To sai ya zama yanzu ta gama shan wahalarsa ya girma; ita ta raine shi amma ba ita ta haife shi ta kuma shayar da shi ba. Abinda zai bada dama ya riƙa shiga wurinta a matsayin ɗanta hanya 2 ce kawai. Shayarwa da haihuwa. To ba ta shayar da shi ba. Gashi ya riga ya girma, ya yi gemu har ya hardace Alƙur'ani izu 60. Har yana cikin mutanen da Annabi (SAW) ya ke cewa a koyi karatun Alƙu'ani daga hannunsa. Kuma gashi an ce ya daina shigowa wurinta. To sai ta zo ta samu Manzon Allah (SAW) ta ce "ya Rasulallah, ga Salim, irin wahalar da na sha a kansa, yanzu ya kai matsayin da zai yi mini hidima, ma'ana ya saka mini nima abinda na yi masa, to amma gashi ni ba ni na haifeshi ba, ba ni na shayar da shi ba, dan haka bashi da dama ya riƙa shiga guri na, to yanzu ya za a yi?" Kuma ta ce "idan ma zai shigo gurina sai na ga fuskar shi Abu huzaifa ta canja saboda kishi. Ba ya so ya ga wani ya shigar masa wurin matarsa." Sai Manzon Allah (SAW) ya ce mata "jeki ki shayar da shi." Sai ta ce "ya Rasulallah ya zan shayar da shi yana babban mutum, da gemu da komai?" Sai Manzon Allah ya yi murmushi "ya ce na san hakan, ki je ki shayar da shi a haka." Wannan hadisi yana nan a cikin sahihu muslim- hadisi mai lamba ta 1453. Suka ce to kaga wannan ya nuna Annabi (SAW) ya ce a shayar da babban mutum har da gemu. Don haka kenan wannan ya nuna cewa babban mutum ba shi da ikon ya sha nonon wata mace. To sai malamai suka ba da amsa cewa wannan ba hujja bace. Kasancewar an shayar da Salim akan wannan mas'ala ba hujja bace. Suka ce dalili wannan wata mas'ala ce ta taso mai rikici kuma mai wahala kuma mai tausayi. Shi yasa aka tausaya wa wannan mata. Ta sha wahalar yaro, ɗan riƙo ne, ta riƙe shi, ta yi masa hidima. Ta yi masa wanka ta masa tarbiya, har ya zama

babban malami. Amma kuma ba ita ta haife shi ba, ba ita kuma ta shayar da shi ba. Don haka babu hanyan da zai ci gaba da yi mata hidima ko da ta tsufa ko ya shiga gurin ta ya yi mu'amala da ita kamar yadda ɗa yake mu'amala da babarsa. Shi ya sa da ta nemi wannan dama, sai aka halatta mata, aka sauƙaƙa mata, ita ta je ta shayar da shi domin ya zama ɗan ta na shayarwa. Don haka suka ce kenan wannan mas'alar ba ta shafi kowa da kowa ba. Ba ta shafi tsakanin miji da mata ba. Ba ta shafi wani babba don ya sha nonon wata mata ba. Kamar yadda wani ya zo ya sami wani sahabi yake ce masa "matata ce nonon ta ya ƙafe a cikin jikin ta, ya ƙi fitowa . Saboda haka da ya ƙi fitowa ni kuma sai na sa baki na a jikin nonon sai na tsotsa. Wato ƙofofin ne suka toshe na nonon saboda haka sai na tsotsa na tsotse mata bakin nonon yadda yaro zai samu dama ya riƙa sha". To bayan ya gama wannan, sai ya zo ya sami Abu musa al Ash'ari, sai ya tambaye shi. Sai Abu Musa al Ash'ari ya ce masa "ta haramta a gareka. Wa ya saka?" To sai ya tafi ya gayawa Abdullahi ɗan Mas'udu wannan. Sai ya ce masa ya ta shi su je makarantar wanda ya yi masa wannan fatawar. Sai Abdullahi bin Mas'ud ya kwashi gayyar almajirai da wannan mutumin da aka yiwa fatawa. Suka je, sai ya ce "kaine ka yiwa wannan fatawa?" Ya ce "eh lallai ya bani labarin abinda ya faru, ni kuma na yi masa fatawa." Sai Abdullahi bin Mas'ud ya kama hannun wannan mutumin ya ce "yanzu wannan jariri ne? wannan mutumin jaririne? Haka kawai ka ɗauko fatawar jarirai ka yiwa babban mutum irin wannan?" Sai Abu Musa al Ash'ari ya ce "to jama'a kada ku ƙara tambayata matuƙar wannan malamin yana gari." Wato ya nuna Abdullahi ɗan Mas'ud ya ce matuƙar yana gari, to kada ya ƙara zuwa wajensa ya yi masa fatawa. Sai kuma suka kafa hujja da fatawar sayyidina Umar cewa yana wani gida da ake kira 'darul ƙara'i'. Abdullahi ɗan Umar yana zaune sai wani mutum ya zo ya ce menene maganar da ta fi rinjaye dangane da babban mutum ya sha nonon mace? Sai Abdullahi bin Umar ya ce masa wani mutum ya zo wata rana wajen Sayyidina Umar sai ya bashi labarin cewa yana da wata baiwa, ko saɗaka ko kuyanga kuma ya kasance yana saduwa da ita. Ashe matarsa tana jin haushi. Wataran ya fita sai matar ta kama baiwar ta zo ta sa ta a jikin nononta ta ce sai ta sha. Wannan baiwa sai ta sha nono. Bayan ya dawo zai shiga wajen baiwarsa sai matarsa ta ce to ai ta haramta gareka domin na shayar da wannan baiwa taka. Shi kuma da ya ji haka maimakon ya yi wani abu sai ya taho wajen Sayyidina Umar ya gaya masa. Wanda a ƙarshe Sayyidina Umar ya ce masa "ka je ka ci gaba da mu'amala da baiwarka. Wannan shayarwa da matarka ta yi mata ba za ta haramta a

gare ka ba. Wato wnnnan abin da tayi bai yi tasiri wajen da zai hanaka ka ci gaba da mu′amala da ita ba.″

Sannan ka ga matsalar shima wanda ya yi amarya sai matarsa, uwar gidan ta zo ta ce ″ai wannan yarinyar na shayar da ita tana ƙarama don haka auren bai yi ba dole ka sake ta.″  Shima ya je ya yi tambaya aka ce a′a, ai wannan shayarwa ba ta yi tasiri ba. Ka ga wannan ya nuna kenan cewa ƙaulin da ya fi rinjaye shine shayrwar babba, ko babban mutum ya sha nonon matarsa, ko wata lalura ya sa zai sha nonon wata, to wannan ba za a yi masa hukunci da wannan matar da ya sha nononta da cewa ita babarsa ba ce. Shine abinda ya fi rinjaye akan wnnan mas′ala.

Amma idan matsala ta taso irin ta Abdullhi ɗan Umar, wato mutum ya riga ya girma a hannun mace. Ita ta riƙe shi, ba ita ta haife shi ba, ba ita ta shayar da shi ba, kuma ya wuce lokacin shayar wa, ita ma tana so ta ci moriyarsa domin ba ta da kowa a duniya sai shi, to itama ana iya yi mata fatawa akan ta ɗauki mas′ala irin ta Sahalatu bint Suhail, matar abu Huzaifa dangane da matsalar Salim. Ta shayar da shi Salim ɗin amma itama sai irin hukuncin ya zo kanta. Amma duk wacce ba ta samu kanta a mas′ala irin ta Salim da Sahlatu bin Suhail da Abu Huzaifa ba, to ko ta shayar da mutum babu komai. Abinda za mu ce kenan a nan shine, ya halatta ga mutum in ya tsotsi nonon matarsa ya sha ba za a ce ya aikata haramun ba, ko da kuwa ruwan nonon ya shige cikinsa.

Dangane da yadda za a ba da nono ga babba a irin mas′alar Salim da matar Abu Huzifa. Wannan shine ɓangaren da malamai suka yi dangane da ita kanta siffar ta ya ya kamata ayi a ce mutum ya sha nonon. Shin dole sai ya je ya kama bakin sa ya tsotsa ko kuwa ya za a yi? To wasu Malaman suna cewa ita mas′alar Salim ita za ta warware wannan rigima. Shin yaya Sahlatu bint Suhail ta shayar da Salim? Wasu sun ce tatso masa shi a ƙoƙo ta yi ta bashi ya sha. Wasu sun ce a′a ta taga ta zuro kan nonon nata shi kuma yana daga waje ya kama ya sa bakinsa a ciki ya tsotsa har ya sha nonon yadda ake buƙata. Ka ga anan mas′alar ma ta yi Magana dangane da cewa ma ba sai ya sha ya ƙoshi ba. B a wai sha sau 3 ko 5 ko 10 bane. Sau 1 tak ya sha kuma ta taga ta zuro masa bakin nonon ya tsotsa. Daga nan ne sai ta haramta a gare shi.

Yanzu ta zama babarsa kenan ta shayarwa. Ka ga kenan wasu na ganin lallai tsotar nan shine asali. Amma idan aka riga aka zuba shi a kofi, ko aka zuba shi a wani

abu, wannan ya zama ba za a ce shayarwa bace. Ko idan aka ɗura masa ta hanci, to a mazhabar mu ta Malik suna ganin duk wata hanya da abu zai je cikin mutum, ta hanci aka ɗurawa mutum ko kuma aka zuba masa ta baki, matuƙar an ɗebo shi, ko da an gauraya shi da ruwa, misali da ka ɗebo nonon, sai wani ya zo ya zuba ruwa, matuƙar nonon ya rinjayi ruwan, sai dai in ruwan ya rinjayi nonon to ya riga yanzu ya zama hukunncin sa ya tafi. Amma idan har ruwa ya ɗiga a cikin nonon, kuma bai sa nonnon ya zama kamar ruwa ba, to shikenan  an sha, hukunci yana nan.

A wajen malamai da yawa cewa nonon ake la'akari da shi ba cewa dole sai an tsotsi hantsar nonon ba. Matuƙar dai an sha, ko ɗure aka yiwa mutum, ko ta hanci ne to hukuncin sa yana nan. Ko ta hanci, ko ta baki ne aka masa ɗure, ko aka masa irin abin da ake ba yaro koko ɗinnan. Yadda a ke kama bakinsa a gwale a yi masa ɗura. To ko ɗura aka yi masa ta baki ko ta hanci duk dai wannan hukunci yana nan;  wanda shine abinda malamai suka rinjaya.

Tunda mas'alar mun gamsu cewa sai mutum yana ƙarami sannan hukunncin ya hau kansa, ka ga kenan shi ƙaramin yaro ba zai gane an yi masa tilas ba ko an yi masa son ransa. Dama mun riga mun kulle  mas'alar babban mutum da cewa idan ya sha nonon mace ba ta haramta a gare shi ba.  Shi kuma yaro ba za ka iya gane tilas aka yi masa ko ba tilas ba ne. Saboda haka shi malam Ibn Hazamin ne yake ganin dole ne sai ya zamo wato ya kama da bakin sa ya tsotsa. Amma idan aka shayar da shi wannan nonon ta hanyar zubawa a ƙwarya ko aka mayar da shi madara aka dama fura aka bashi; ko aka mayar da shi abinci, ko aka yi gurasa da shi, wato ya zama shine ruwan haɗa gurasar, ko aka yi miya da tuwo da shi, in dai an cakuɗa shi da wani abu, to yana ganin duk wannan ba zai yi tasiri ba domin nonon ya fita daga asalin sa. Duka wannan ba zai nuna cewa wanda ya sha ɗinnan ya haramta ba.

To wanda kuma aka bashi nonon sai ya amayar da shi ko ya yi tumbuɗi, to wannan tunda dai ya riga ya shiga cikinsa amma ya dawo, shin hukunci yana nan ko baya nan? Shima malamai sun ce hukuncin da shigar nonon ake yi ba da fitowarsa ba. Matuƙar nono ya riga ya wuce maƙogwaro, ya kai ciki, sai yaro ya yi tumbuɗin sa ko ya amayar da shi, to wannan dai hukuncin haramcin yana nan. Amma da za a ce a bakinsa aka ɗura masa bai je ciki ba, bai wuce maƙogwaro ba sai ya zubar da shi to wannan ba za a yi hukunci ba tunda bai riga ya kai ciki ba. Ba shigar sa baki ne hukuncin ba, wucewar sa maƙogwaro ya kai uwar hanji shine hukuncin sa. Kamar hukunncin su ɗaya da karyewar azumi. Ka ga abin da ya wuce maƙogwaro ya kai

ciki, ko ta maƙogwaron ko ta hanci ya shige, shi ake yiwa hukunci da karyewar azumi. Amma da a ce za a yi masa allurar nonon- misali a ce za a iya yin allurar nonon, to shin wannan zai iya zama hujja? sai akace a′a ba zai zama ba. Ko kuma a ce a buɗe wani wuri ta cikinsa a zuba, suka ce wannan ma mace ba za ta zama haramun a gareshi ba. Idan aka buɗe cikinsa aka buɗe uwar hanjinsa aka ɗura nonon, ka ga bai shiga ta baki ba, bai shiga ta hanci ba, ɗura shi aka yi, to wannan duk ba zai nuna haramci dangane da wannan mata ba.

Abin lura da bin la′akari anan shine cewa shan nonon yana da ƙa′ida. Idan an samu waɗannan ƙa′idoji da muka lissafa sun cika, to wannan yaro da aka shayar da shi yana da kyau a lura da wannan hukuncin. Kuma mun ce irin wannan ya fi faruwa ne a gidajen biki ko gidajen suna, ko ʻyar′uwa ko wata mata; yaro yana kuka babar sa ba ta nan, ta ɗauka ta ga cewa ba zai yi shiru ba sai an bashi nono, sai a ga itama tana shayarwa, sai a bashi nono. Ko kuma ma ʻyar′uwar ta ta gamu da rashin lafiya, watama rasuwa takeyi a wajen haihuwa sai ta bar jaririn. Sai a kaishi wani gida a shayar da shi. To ya kamata a kiyaye wannan hukuncin cewa wannan yaro da mahaifiyarsa ta rasu yana jariri, ko aka tsinto shi yana ƙarami, ko aka kawo shi yana ƙarami, ko mahaifiyarsa ta kamu da wata rashin lafiya da ba za ta iya shayar da shi ba, sai wata cikin ʻyan′uwa ko cikin dangi ko abokan arziƙi ko bare ta ga cewa za ta shayar da wannan yaro, to matuƙar ta shayar da shi, to a kula da wannan. A kula da cewa wannan yaro fa yanzu hukuncinsa ya zama ɗan gidan. Duk abinda ʻya′yan gidan nan ya haramta su aura to shima fa wannan yaro dole ya kiyaye wannan ƙa′ida shima ba zai auri irin waɗannan matan ba.

## Tambaya Kan Aure 08

To sannan akwai maatar da ita kuma matar aure ce. Don haka mutum baya halatta ya auri matar aure. Ta yiwu anan mutum ya yi mamakin ya za a yi a auri matar aure? Kwarai kuwa ana samu. Mutum bai yi bincike ya ga me ya raba matar da mijinta ba sai ya zo ya aure ta. Sai daga baya sai ta bayyana cewa wannan mata da ya aura matar aure ce. Wataƙila ɓoye masa ta yi. Wata ƙila kuma aurenta na baya bai mutu ba, jahilci ya sa aka ɗauka ya mutu. Sai an ɗaura aure da mutum yana

zaune da amaryarsa, shikenan daga bisani sai a je a tamabyi wani malami  ya yi fatawa cewa hanyar da aka bi aka kashe wancan auren na baya ba hanya ce da musulunci ya amince da ita ba. Don haka har yanzu halastacciyar mata ce ga mijinta na baya.

Wannan ya sa duk mutumin da zai auri bazawara to ya binciki hanyar da suka rabu da mijinta. Da kuma yadda take yin idda domin ya tabbatar rabuwar a kan shri'a a ka yita. Sannan kuma ya tabbatar ta yi idda. Domin wata matar itama kanta ba ta san hukuncin iddar ba. Wata ta ɗauka koda tana jini idan ta yi watanni 3 to iddarta ta ƙarre. To akwai wacce sai watanni uku-ukun take yin jini, ka ga irin wannan sai ta yi watanni  9 kenan za ta gama idda. To maiyiyuwa in ta yi watanni 3 ta gaya maka ta gama idda, alhalin jini ɗaya ne ya zo a wata ukun, akwai ragowar watanni 2. Sai ka aure ta; daga baya sai ka ga cewa ba ta ma fita daga auren wancan mijinta na baya ba balle kai ta halatta ka aure ta. Don haka malamai suka ce mace ta 22 kenan- wato matar aure, ko wacce ta ke yin idda ta wani mijin .

Sannan wajen idda, idan aka ce ga mijin sannan ya tabbata cewa auren ya rabu. To kuma sai ka tabbatar cewa ta yi idda yadda shari'a tace. Munce mata dangane ga idda sun kasu kashi 4, wanda duk za mu ji labarinsu a gaba. Akwai mai yin idda da jinane 3. Sune wanda Allah Ta'ala Ya ce wacce aka sake ta za ta jira sai ta yi jini 3. Sannan akwai wacce take yin idda da haihuwa, wato mai ciki ce, ka ga kenan sai ta haihu. Sannan akwai wacce take ba ta jinin kwatakwata, ko jinin ya ɗauke, za ta yi ita kuma wata 3. Akwai kuma wacce ba ta iddar kwata-kwata. Kamar wacce an riga an aure ta, sai ya zamo mijin ya sake ta tun ba ta tare ba. Ka ga wannan babu ma idda; ko yanzu ma idan akwai mai sonta sabo, nan take sai a ɗaura aure.

To wannan idda ɗin- dole mutum ya bincika matar da zai aura ya tabbatar da cewa ta gama idda kuma a wane layi take a cikin dangogin matan nan da muka lissafa domin kada a yi aure a cikin idda. Kuma an taɓa yin hakan; inda  aka saki wata. Sai ta yi jini 1, ta yi na 2 amma ba ta ga na 3 ba sai aka yi aure.  Ka ga ba ta gama idda ba tunda jinni 3 Allah ya ce ita kuma ta yi 2. Aka ɗaura aure; sai bayan an haifi 'ya'ya daga baya da wannan mata ta ji ana wa'azi, sai ta ji ance sai an yi  jini 3 sannan ake gama idda. Ko da ta yi jinni 1 da na 2 to dole sai ta yi na 3, ko da bai ɗauke ba idan ta yi aure shikenan. Amma na 3 bai zo ba aka ɗaura auren, sai a gidan mijin na ukun ya zo. Saboda haka ka ga an ɗaura aure kafin a gama idda. Auren ka ga bai yi ba kwata-kwata. Gashi kuma an yi shekaru ana tare amma sai

daga baya aka gano babu aure. To irin wannan ake gudu. A zo a yi abu daga baya kuma a zo aga babu shi kwata-kwata. To shi yasa aka ce dole ne ka bincika ka ga nau'in irin yadda mace take idda kafin ka aure ta.

Haka matar da ta zo ta ce ta musulunta tana da miji a baya. Idan ta musulunta ba za a cigaba da mu'amala da itaba sai ta yi istibra'i ita kuma. Sai ta yi jini 1. Wannan jini 1 da za ta yi shi zai nuna cewa ta fita daga wancan aure. Ko irin matan da ake ribatowa daga wajen yaƙi. To suma haka ne in suka yi jini 1na  Istibra'i  shikenan. Amma ko an yi yaƙi an kamota ba za a ci gaba da mu'amala da ita ba har sai an samu wannan abun tukunna ya tabbata cewa ta yi jini 1. Wato ta gama istibra'i kenan wancan kuma ta sallame shi. Idan ko tana da ciki, to har sai ta haihu tukunna. Haihuwarta shi zai nuna ta yi istibra'i daga wancan auren wanda yake dama musulunci ya riga ya kasheshi tunda ita ta musulunta.

Wacce ba musulma ba da ke auren wanda ba musulmi ba, idan ta musulunta, auren ya mutu nan take saɓanin a ce shine ya musulunta. Idan shine ya musulunta, za a iya bada lokaci mai tsawo ma a ga cewa ko za ta musulunta. Haka idan itama ta musulunta za a iya ɗaukar lokaci mai tsawo idan an ga cewa akwai yiwuwar shi mijin nata zai musulunta. Amma idan babu raja'i  da ta musulunta shi kenan aure ya katse tsakanin su. Tana yin jini 1 shikenan za ta iya yin aure. Hakanan kuma idan ribatota akayi a matsayin fursinan yaƙi, itama idan ta yi jini 1 shikenan wancan auren ya riga ya ƙare.

To haka nan matar da aka mata saki 3 baya halatta wani ya aureta da niyyar zai halattata ga mijinta, ko an yi wannan auren bai yi ba. Don akwai waɗanda suke yin wannan. Sai mutum ya  je ya saki matarsa saki 3 kuma sai abin ya dame shi. Kuma dama duk abinda mutum ya yi shi babu lissafi dole ya dameshi. Mata suna nan da yawa waɗanda suka tsinci kansu a irin wannan yanayi. Mazansu sun musu saki 3 kuma sun zo suna jin takaici na dalilin da yasa suka rabu da su. To irin wannan ana samun ita matar ko shi mijin sai a haɗa baki da wani cewa jeka ka aureta. Ko rannan wani ya yi mini waya daga wata jiha yana tambaya akan cewa ya saki matarsa amma yanzu kuma ya shiga damuwa. Kullun kuka yake yi itama matar kuka take yi. To sai ya samu wani abokinsa ya ce ya taimaka masa zai ba shi kuɗi. Ya ce ya je ya nemi aurenta daga an ɗaura aure ta tare a gidansa dasati ɗaya ta tare sun samu saduwa ya sako a shi kuma sai ya mayar da ita. Nace to "ai bai yi ba. Shi nasan in ya yi shi da wannan niyyar bai yi ba. Kaima naka da za ka yi a bayansa

bai yi ba. Ka ga duka biyun babu wanda yayi. Saboda haka tunda har ka keta shari'a, ka yi abinda ba'a sa ka ba, sai a yi haƙuri har sai ta samu wani mijin da kanta."

Haka nan kuma ita matar itama ba za ta kirawo wani ta ce zo ka aure ni zuwa lokaci kaza ka sakeni ba. Itama idan ta yi haka auren bai yi ba. Domin abin da ake gudu yin auren da mutuwarsa an sa masa lokaci, kuma an sa masa sharaɗin da shri'a ba ta yarda da shi ba. Amma idan wani ne kawai shi tausayi ya kamashi ya a ransa ya sa wannan abun. Bai gayawa mijin ba, bai gayawa matar ba, kawai ya zo ya sa a ransa ko a zuciyarsa wato ya taimaketa ko ya taimaki mijin ko saboda ya hango'ya'ya da sauran su. Ya zo ya yi amma fa bai gayawa matar ba bai gaya wa mijin ba. Mijin kuma bai sani ba matar kuma ba ta sani ba, shine a ransa yayi wannan ƙudurewar. To wannan shi ake kira annikahu bi niyyatil ɗalaƙi, wanda wasu malamai suna ganin yay i, wasu kuma suna ga bai yi ba.

Sannan akwai ita matar ta ƙudure a ranta cewa za ta yi aure, amma mijin da za ta aura dama ba wani miji na a zo a gani za ta samu ba. Tana son ta samu dai gara-gara haka. Kawai ta je in same shi ta lallaɓa shi ta aure shi da saduwa ta samu tsakaninsu shikenan sai ta bijire masa. Idan ta bijire masa ta ɓata masa rai, to shi kenen zai sake ta. Idan ya sake sai ta zo ta yi idda ta koma gidan mijinta na da. To ita ta sa wannan a ran ta, ba ta dai kyautawa wancanba tunda shi bai san da wannan niyar ba. Amma idan ta yi hakan, auren da ta yi yayi, sakin da ya yi mata ma yayi. Sannan kuma idan ta gama idda ta zo ta koma gidan mijin ta ma yayi.

Ka ga kenan abubuwan ta fuska guda 4 e. A cikin fuska guda huɗun nan, biyu ya haramta, biyu ya halatta. Ya zamo 4 kenan. Wanda ya haramta shine, mjin ya sa wani ya je ya aureta dan ya dawo da ita. Ko kuma it matar ta umarci wani ya aureta don ya saketa ta koma. Wannan biyun bai halatta ba. Wanda ya halatta guda biyu sune, ita matar ta ƙudure a ranta cewa za ta yi aure ne na kisan wuta don ta koma gidan mijinta amma shi wanda aka yi auren bai san da wannan ba. Saboda haka in aka yi aka rabu, dama ka san ba za ta saki jiki da wannan mutumin ba. Kwalliya, tsabta, abinci mai daɗi kaga ba za a riƙa yi masa ba tunda dama so ake a ɓata masa rai ya ce ya yi saki. To idan ta yi wannan a ranta; kamar yadda wata mata ta zo, Manzon Allah (SAW) ya ce kina son ki koma gidan tsohon mijin ki, saboda haka ki mayar wa da wannan abinda kika karɓa a hanunsa na gonarsa. Ka ga manzo Allah (SAW) ya ɗagota cewa akwai soyayyar tsohon mijinta a ranta kuma nan take

so ta koma. Amma bai hanata ba, tunda ba za ta iya zama da wannan ba tunda ga abinda ta sa a ranta. To wannan shine.

Sannan kuma

Tambaya Kan Aure 09

Mun yi baya ni akan nau'o'in matan da bai kamata a aura ba su 24 har ma da ƙarin wasu guda uku waɗanda suka zama 27. To yanzu za mu yi bayani akan irin uren da bai halatta ba. Wato in za a yi aure sai an yi la'akari da idan an yi aure da irin wannan yanayin, ko irin wannan sigar to aure rusashene. Daga cikin waɗannan aure da basu halatta a yi su da wannan sigar ko sharaɗi ko ƙa'ida ko siffa ko kama ba, akwai abinda ake kira 'Nikahu shigari', shine mutum ya zo neman aure wajen mutum amma yana da sharaɗi. Idan ya zo sai ya ce to na zo ina so in auri 'yar ka ko ƙanwarka ko yayar ka; ko babar ce ma. Sai ya ce to na yarda amma ni ma naga ƙanwarka sai in ka yarda nima za ka aura mini taka nima sai in yarda in aura maka tawa. To wannan abun shine shari'a bata yarda ba. Shari'a bata yarda da wannan ba saboda abubuwa guda 2.

Na farko, ba dole ne a ce ko wacce daga cikin matan nan tana so ba. Ka ga kenan an takurasu, an ƙwace musu 'yanci da dama su auri wanda suke so. Kawai don ka je kace kana son 'yar wani, kawai sai ya ce shima yana son 'yarka; sai ka karɓi wannan sharaɗin? Kaga bawa 'yar dama ta auri wanda take so ba.

Na biyu a wajen yin sadaƙi ba za a basu sadaƙin da ya kamata ba. Don zamanin jahiliyya suna yin wannan ɗin da siga guda 2. Akwai sigar cewa ka riƙe sadaƙin taka in riƙe na tawa. Wato bani-in-baka kenan. Saboda haka kamar musanyar mata akayi. Babu sadaƙi tsakanin su.

Akwai kuma wanda ake yin sadaƙin amma kuma dole za a samu wata ta fi wata sadaƙi a cikin su biyun. Ko wata tana da ƙa'idojin ta da soyayyar ta da ɗayar bata da shi. To idan aka ce komai  za a yi shi baiɗaya, to dolene an shiga cikin haƙƙinta duk siga guda biyun.

Shine mu a mazhabar mu ta Malik sun ce idan akwai sadaƙi, ko wacce an bata sadaƙin da ya kamata to shi kenan auren ya yi. Sannan sai muke ƙara ƙa'ida kuma

sannan sai idan kowacce tana so. Idan ko wacce tana so, to wannan ba laifi. Mutum ya ga ƙanwarka yana so kaima ka ga ƙanwarsa kana so. Karshe ka aminnta za ka bashi ƙanwarka, ya aminta zai baka tasa, amma da sharaɗin kowa sai ya je zance tukuna ta amince. Kuma kowa zai yiwa tasa gwargwadon halinsa. Me yuwa ɗaya mai arziƙƙi ne, ka ga zai yo nasa mai yawa. Ɗaya mara arziƙi ne zai yi nasa kaɗan. Amma dole sai an gina soyayyya da kuma amincewar matan. Sannan kuma kowane zai yi sadaƙinsa daban ba tare da na wani ya zama a bakin na wani ba. To idan an yi da wannan sharaɗin guda 2, malamai suna ga ba laifi. Gama hadisi ya tabbata cewa manzon Allah (SAW) ya hana auren 'shigari'. Shine wato wanda ya tabbata a hadisin Musulim wanda yake me lamba ta 1417. Haka ma ya zo a hadisin Abu Hurairata yake cewa Manzon Allah SAW ya hana auren shigari.

Shi shigari shine mutum ya cewa wani auran mun da 'yar ka ko 'yar uwar ka da sharaɗin nima zan auran maka da tawa. Wato kaga kenan anan su matan ba a basu dama ba, kawai can ne su waliyan sukaje suka yanke shawararsu. Har an rawaito daga Arash yake cewa, Abbas ɗan Abdullahi bin Abbas ya aurarwa da Abdulrahman bin Hakam 'yarsa shima Abdulrahman bin Hakkam ɗin ya aurar masa da 'yarsa. Amma su sun sanya sadaƙi a tsakani, kowa akwai sadaƙin sa. Sai aka rubutawa Mu'awiya cewa ga abinda ya faru. Sai ya umarci Marwan cewa ya raba wannan auren. Shi a wurin Mu'awiya ai ko an biya sadaƙi ai ba'a nemi kuma yardar yaran ba. Saboda haka ya ce a'a shi a raba auren kawai. Yace wannan shine shigarin da aka hana. Duk da mun ce akwai malaman da suke ganin in dai har an yi sadaƙi, ko wacce an bata sadaƙin da ya dace, to shikenan aure yayi. Amma wasu na ganin kuma akwai soyayyya. Sai in kowacce tana so. Sai an ƙara wannan sharaɗin na 2 sannan ne wannan auren ya tabbata. Kuma suka kafa hujja da hadisin cewa Manzon Allah (SAW) ya ce duk wanda ya sanya wani sharaɗi wanda ba ya ciki littafin Allah, wannan sharaɗin ɓatacce ne, ko da ya kai sharaɗi guda 100. Kuma wannan auren ma baya ƙarko. Dalili shine idan ɗaya ya samu matsala da tasa ya sako ta, to kaga dangi za su zo su takurawa mutum shima sai ya saki wannan. Domin tunda ya sako tasa shima ya sakammar tasa. Abubuwan za su riƙa tafiya baiɗaya ko kafaɗa da kafaɗa wanda kuma za a iya cutar da wata. Ko kuma auren ma dai babu ma tsari a ciki. In dai ba kowa ne yake so daban ya je ya yi auren ba, da wannan sharaɗin, to wannan auren malamai suna ga bai halatta ba kuma in an yi shi da wannan siga bai yi ba. Wannan shine kashi na farko na aure wanda musulunci bai yarda da shi ba, wato shine 'Nikahu shigar.

Sannan na 2 shine ʻNikahun muhallil- shine auren wanda zai halatta mace ga wani mijinta wanda ya yi mata saki 3, wanda mun gabatar da wani abu mai kama da shi a baya. Wannan yana cikin ʻkabaʼiraʼ, wato manya-manyan laifuffuka wanda Allah Ya haramta kuma aka tsinewa wanda yayi da wanda ya sa shi ya yi. Kamar yadda ya tabbata a hadisin Abdullahi ɗan Masʼud. Yake cewa, Manzon Allah (SAW) ya laʼanci wanda ya halatta da wanda ya nemo wanda ya halatta auren domin ya sako matar da ya saka domin ta halatta a gareshi ya sake aurenta.  To su biyun duka tsinannu ne,  kamar yadda ya tabbata a hadisi wanda Imam Tirmizi ya ruwaito mai lamba ta 1120, Ima Nisaʼi ya ruwaito shi, Imam Ahmad ya ruwaito shi a cikin Musnad. Har wata ruwaya ta zo a cikin ibn Maja me lamba ta 1936 an kira shi ʻat taisul mus taʼan.ʼ wato ya zamo ɗan akuya wanda yake lebura; wato ɗan akuyan aro.

Wannan ita ruwayar ta kiransa ɗan akuyan aro bata inganta ba. Amma fuƙahaʼu suna kiransa da wannan domin a ƙara ƙasƙantar da wannan sanaʼa. Sanaʼa wacce mutum ya mayar da sanaʼarsa sai mutum ya saki matarsa saki 3 sai shi ya zo ya aureta don ya halattata ta koma gidan mijin ta na farko. To wannan ba sanaʼa bace. Don haka mafi yawan malamai suka tafi akai, kamar Imamu Malik, da Imamu Shafiʼi da wata magana ta Imamu Ahmad da malam Laisu da malam Sauri, har da malam ibn Mubarak da waninsu cewa wannan auren ɓatacce ne. Akwai bambanci tsakanin haramun da ɓatacce. Shi haramun shine wanda yay i ya aikata laifi, amma kuma abin yayi. Shi kuma fasid shine wanda bai yiba. Maʼana idan ma anyi auren, kada ma mutum ya ɗauka cewa shi kenan tunda tsinuwa ce, bari in je in ɗauki tsinuwar. Ya je ya yi auren tsinuwa ta hau kansa. Koma ba ta hau kansa ba dai, ya yi abinda ya cancanci tsinuwar. Saboda haka ya halatta ta ga mijin, shi kuma ya aikata haramun. Amma kuma haalattawar ma ba ta yi ba. Shine abinda waɗannan malamai suka tafi akan cewa babu auren ma kwatakwata.

Kamar yadda Sayyidina Umar yake cewa, ba za a zo minni da mutumin da yayi irin wannan auren ba face sai na sa an jefe shi. Wato da matar da wanda ya yi mata irin wannan auren, in dai duk sun sani suka yi, Sayyidina Umar yce "in aka kawo su zan musu hukuncin mazinata, in sa a jefe su." Ka ga kenan kwatakwata wannan ya zo a cikin musannaf  na malam Abdulrazaƙi, juzʼI na 6 shafi na 265 da kuma littafin Saʼeed bn Mansur a hadisi na 1992. Cewa Sayyidina Umar ya yi wannan cewa zai jefe waɗanda suka yi irin wannan aure. Hakanan an tambayi Abdulahi

ɗan Umar game da mutumin da ya auri mace don ya halatta wanda ake kira auren kisan wuta. Ko da yake auren kisan wuta ya fi zuwa daga mace da ta ƙudurtawa a zuciyarta. Wannan kuma auren halattawa; sabboda haka sai ya ce ai wannan zina ne kawai. Wannan yana nan a cikin Musannanf na malam Abdulrazaƙi wanda aka yiwa shi wannan sahabi fatawa akan cewa wannan zina ce.

Dama abinda muka ce idann wannan ya faru yakan fito ne ta fuskoki 4.

1- Mijin matar na farko wanda ya saketa saki 3 ya kirawo mutum ya ce masa "na saki matata saki 3 amma ina sonta. Ina son ka taimaka mini ka jeta aure ta. Idan ka aure ta bayan kun sadu sai ka sako ta don ni na aure ta. To wannan haɗin bakin da akayi tsakanin mijin ta na farko da kuma wanda zai aure ta; mijinta na biyu, akan zai sako ta don mijinta na farko ya aura, wannan shine tsinuwa ta hau kan mijin na farko da na biyu. Shi ya sa ya ce Allah Ya tsinewa wanda ya halatta da wanda aka halattawa. Kaga tunda sun haɗa baki ne shi yasa tsinuwar ta dawo kan mijjin. Shi yasa su biyun suka shiga cikin tsinuwa.

2- Ita matar ta gayyato wani ta sharɗanta masa cewa zai aure ta amma bayan suna tare ya sadu da ita zai sake ta domin niyarta shine ta koma gidan mijinta. Ka ga shima dai a nan an samu haɗin baki tsakanin miji na biyu da kuma wannan matar. To anan tsinuwar akan shi mijin na biyun take ba akan matar ba- domin ita matar ba ta da ikon saki ba ta da ikon aure. Aurar da ita ake yi, kuma sakinta akeyi. Saboda haka shi da ya karɓi wannan sharaɗin, to shine tsinanne. Saboda haka anan ma auren bai yi ba. Ka ga hali 2 kenan auren bai yi ba.

3- Ita matar ta ƙudure a ranta cewa "tunda miji na ya sakeni bari in nemi wani ba tare da na gaya masa ko ya sani ba in aure shi. Sannan niya ta in ɓata masa rai ko kuma in yi abinda zai sake ni don in koma gidan miji na." Wannan shine abinda ya faru ga matar Rufa'atul Kurazi. Matarsa ta zo wajen Annabi (SAW) tace "Rufa'atu ya sake ni kuma saki 3. To shine na auri Abdulrahman bn Zubairu Kurazi a bayansa. To shi gaban sa baya tashi, wato bashi da lafiya." Saboda haka sai Manzon Allah ya ce ke dai kina so ki koma gidan mijin ki Rufa'a, to ba ki isaba har sai ya ɗanɗani zumarki kin ɗanɗani tasa. Ma'ana sai saduwa ta shiga tsakanin ku." Ka ga kenan a nan niyarta so

take ta koma gidan mijinta kuma Annabi ya ganota cewa niyar komawa gidan mijin nata ne- amma kuma bai ce auren bai yi ba, cewa yayi sai an sadu tukunna. Wato ta yi haƙuri a sadu; in so take ta koma ɗin in aka sake ta sai ta koma. Saboda haka ka ga anan ita matar ba a ce auren in ta ƙudure ranta da wannan niyar bai yi ba. Sai dai duk da haka an dai san akwai alhaki da ta ɗauka na shi wannan mutumin. Wataƙila shi ya aureta da niyar a zauna dindindin, wataƙila ya je ya kama haya, ko ya sayi gida, ko yayi fenti. Ya gayawa danginsa ya yi angwanci da saurann su. Shi duk bai san da wannan ba, ashe akwai yaudara a ɓangaren matar. Amma ta ɓangaren aure yayi.

Muka ce na 3 shine inda za a samu wani ya shiga tsakani. Shi bai gayawa mijin ba, bai gayawa matar ba kuma matar ba ta sani ba, mijin bai sani ba. Labara ne ya zo masa cewa wane ya saki matarsa saki 3 amma ya shiga damuwa, itama ta shiga damuwa, ga 'ya'ya tsakanin su. Sai ya ƙudure a ransa cewa to sshi bari ya je ya aureta da nufin idan ya tare da ita sai ya saketa domin ta koma gidann mijinta. Muka ce wannan shi ake kira 'yin aure da niyar saki'- wato mutum ya tafi ya yi aure amma a ransa akwai niyar saki. To a nan ne muka ce wasu malamai sun ce halal ne, wasu sun ce haram ne.

Waɗanda suka ce bai yi ba daga farko, suka ce wani mutum ya zo wurin Abdullahi ɗan Umar sai ya tambaye shi bisa wani mutum da ya saki matarsa saki 3. To sai wani ɗan'uwansa ba tare da haɗin baki da shi ko da ita ba ya zo ya aureta domin ya halatta ta ga ɗan'uwansa, shin ta halatta ga na farkon idan wannan na biyun ya sake ta? Sai Abdullahi bn Umar ya ce a'a, sai auren da yayi da niyar ya zauna. Ya ce mu a zamanin Manzon Allah (SAW) muna ƙirga wannan aure a matsayin zina.

To ammma malam Abu Hanifa da mala Shafi'i sun tafi akan cewa wannan auren yayi idan ya sake ta kuma wannan ra'ayinsa ne. Amma dai auren ya yi tunda ba a faɗi wannan niyar a wajen ɗaurin auren ba, kuma mijin bai san da wannan niyar ba, matar ba ta san da wannan niyar ba, waliyin da ya ɗaura aure ba a gaya masa wannan niyar ba. Matuƙar ana samun wanɗannan sharuɗɗa guda 3, suka ce shi wanda ya zo ya yi wannan abu, auren yay. To ka ga mas'alolin sun zama 4 kenan, muka ce biyu an yi ittifaƙi ba a yarda da su ba sannan kuma ɗaya an tabbatar da cewa ta yi; sannan kuma ɗaya akwai saɓani- masu ganin anyi da masu ganin ba a yi ba. Abinda ya kamata dai shine mazaje su yi haƙuri da matayensu. Idan aka yi haƙuri mas'alar ba za ta kai har ga wani ya zo yana neman ko ya halatta ko kar ya

halatta, ko kuma ya  zo ya yi irin wannan auren wanda daga baya za a zo ayi nadamar da ta sa aka yi shi ba. To wannan shine aure na 2 daga cikin aure waɗnda bai halatta ba.

Kash na 3 shine 'nikahul mut'ati' wato auren mut'a. Wato shine mutum ya auri mace amma an sa lokaci. Sharaɗin aure ya cika, akwai soyayya, akwai amincewar waliyi da bayarwarsa, akwai sadaƙi, akwai shaidu. Komai akwai, abinda aka yi kawai an salokaci cewa zuwa wata, ko zuwa shekara, ko zuwa shekara 2, ko shekara 5, ko shekara 100 aka sa, tunda aure ba a san ko za a kaishi ɗarin ba-idan dai an sawa aure lokaci bayan ya cika duka sharaɗi. Misali, sai waliyi yace wannan aure da za mu ɗaura wanda ga muhallin ɗaurin aure, shine miji da mata, ga sadaƙi an bayar, ga shaidu, ga siga, ga waliyi, ka ga sharucɗɗa guda 5 sun cika, sai yace to amma auren za a yi shi ne nan da shekara 5 ya ƙare. To auren ya zama na mut'a, ya kuma lalace. Saboda haka aure ana yin sa ne da niyar a zauna dindindin.  Idan dai har an sa sharaɗin za a yi saki, ko auren zai ƙare zuwa wani lokaci, to wannan auren bai halatta ba kuma yana cikin auren da aka haramta.

Wanda kamar yadda ya zo cewa da can wannan auren halal ne a zamanin manzon Allah (SAW), sannan  Allah ya soke shi akann harshen Manzon Allah (SAW). Sannan aka sake halatta shi, aka sake soke shi, ƙarshe dai aka soke shi sokewa ta dindindin ila yaumil ƙiyamati. Wanda wannan shine malamai ma'abota ilmi suke kai. Da mazhabar Malikiya da Shafi'iya da Hambaliya da Hanafiya duk suna kan wannan. Kawai saɓanin da aka yi shine a wane lokaci ne aka soke auren mut'a gaba ɗaya daga addinin musulunci.

Ya tabba ta daga Sayyidina Ali, ya cewa Abdullahi ɗan Abbas cewa Manzon Allah (SAW) ya hana auren mut'a, ya hana cin naman jaki a lokacin khaibara. Wato a lokacin da aka yi yaƙin khaibar ,shekara ta 7 kenan bayan hijira aka soke waɗannan abubuwa guda 2. Kamar yadda ya tabbata a hadisin Buhari mai lamba ta 5115, da hadisin Muslim mai lamba ta 1407. Kuma wannan shine bayanin da malamai sukayi a cikin mudawwana, da cikin biyatul mujtahidi, da Nihayatul Muhtaj, da Almabsuɗ, da Almugni, da Al'Insab, da Al Tamhid, da Sharhi Ma'anu Athar, da Muhalla, da Jami'u Ahkamun Nisa'i, da Nikahul, Mut'a indal Ka'ilina Bihi, da Al'Iztizkar, duk dai manyan litattafai na musulunci sun tattauna wannan mas'ala ta wannan aure lokacin da ya fara da lokacin da kuma aka soke shi baki ɗaya.

Sannan wasu suka ce an soke shi ne a shekara ta 8 bayan hijira, wato lokacin da aka yi fatahu Makka. Kamar yadda ya zo a hadisin ibn Samra, baban s aya ce sun yi yaƙi tare da Annabi (SAW) lokacin fatahu Makka, ya ce muka zauna a Makka kwanaki 15. Manzon Allah (SAW) ya bamu izni, ya bamu dama mu auri mata amma da niyyar in za mu koma za mu rabu da su. Saboda haka muka yi irin wannan auren. Ya ce ban fita daga garin Makka ba; hrr sai da Manzon Allah (SAW) ya ce mana wannan auren daga yau an hana shi, kamar yadda ya zo a cikin Sahihu Muslim a hadisi mai lamba 1406. Yake cewa Matan da muka aura sun kasance tare da mu da niyar za mu sake su zuwa wani lokaci, kwana 3. Sai manzon Allah (SAW) ya yi umarni da a rabu da su, ma'na kada a sake yin irin wannan aure. Kamar yadda ya zo a hadisin muslim mai lamba ta 1406, haka Imamul Baihaƙi ya ruwaito wannan. A wani lafazin yake cewa Manzon Allah (SAW) ya umarce mu da yin aure zuwa wani lokaci a lokacin da aka yi fatahu Makka. Kuma ba mu fita daga Makkan ba har sai da aka soke wannan auren, cewa a dena yinsa. Wannan ma ya zo a hadisin Muslim mai lamba 1406.

To sannan a lokacin da aka yi 'Amu auɗas', nan ma ya zo a hadisin Salamatu bn Akwa, yake cewa Manzon Allah (SAW) ya yi mana sauƙi a amu auɗas da yin mut'a kwana 3. Wato mu auri mata da niyyar bayan kwana 3 ko wata 3 za mu sake su. Saboda haka sannan kuma sai aka haramta shi har izuwa ranar alƙiyama.

To akwai bayanai guda 2, waɗanda wataƙila su ya kamata a ƙara faɗaɗawa dangane da maganar auren mut'a ɗinnan. Shine akwai hadisin Jabir bn Abdullahi, wanda yake cewa mun kasance mukan auri mata da nufin zuwa wani lokaci za mu sake su, kuma mukan basu ma abin da bai wuce tafin hannu na dabino ko tafin hannu na gari ba. Wannan a lokacin Manzon Allah (SAW) da lokacin Sayyidina Abubakar duk muna yin haka. Har sai lokacin da Sayyidina Umar ya hau gwamnati sannan ne ya hana mu.

Akan ƙissar Amr bn Kurais, sai malamai suka ce wannan ya dangana ne da waɗanda hadisi ko kuma labarin cewa an soke wannan aure bai kai musu ba. Don ana samun hukunci ya sauka amma wasu su yi ta amfani da tsohuwar doka kafin sabuwa ta zo. Wannan sanannen abune a kowane zamani, a kowane lokaci ana samun irin wannan. Ana samun canji a cikin wani abu amma saboda ƙarancin kafafen yaɗa labarai wani abun baikkai musu ba, sai daga baya ya kai musu ko sai abin ya yaɗu kowa ya ji. Tunda aure ne wani ba zai san yaya aka yi auren wane da

wance ba. Ko sai idan ka ji labari sai ka karantar, kamar yadda muke ganin har yau ɗinnan muna da jahilci na hukunce-hukuncen addinin musulunci. Sai an yi wani abun daga baya in an ji bayanin malamai sai a fasa. To ka ga a zamanin mu, yanzu kenan, inda hanyoyin yaɗa labarai da hanyoyin isar da saƙo suka yi yawa amma duk da haka sai ka ga mutane suna yin abubuwa waɗanda shari'a ba ta ce a yi ba, sai daga baya in sun samu ilmi sai su gyara, to a wancan lokcin ma an samu irin wannan.

Hakanan ya tabbata Abdullahi bn Abbas ya kasance yana halattawa mutane su yi auren mut'a a lokacin da lalura ta same su. Wato lokacin da mutum ya sauka a wani gari yake jin tsoron zai yi zina, to sai ya je ya auri mace da komai na sharaɗai sai ya cika- da waliyanta da shaidu da komai, amma za a gayawa waliyinta cewa wannan aure zuwa lokaci kaza ne. To amma shi yana cewa kamar idan mutum ya shiga halin tsanani aka halatta masa ya ci naman jaki, ya ci mushe, to haka shima in ya shiga tsanani da zai kaishi ga halaka, kuma ya sauka a garin da yake baƙo ko bashi da damar da zai iya auren da zai riƙe dindindin, to yana iya yin auren da wannan niyar. Amma duk da wannan fatawa ta Abdullahi ɗan Abbas da waccan Magana ta Jabir ɗan Abdullah, duka waɗannan abubuwa guda 2 malamai sunce ba za su isa dalili da za su ci aba da halatta auren mu'a ba. Domin an yi shi a zamanin Annabi (SAW) an kuma halattta shi; kuma hikimar da ta sa aka yishin ta gushe. Domin aure ana samun ciki, ana samun haihuwa, ana samun zuriya. To idan aka ce an sa masa lokaci zai mutu, to ɗan shi yake shiga matsala. Domin  an ce in aka rabun, wasu suna ga ma ɗan da a ka haifa ko gado bashi da shi. To ka ga meye bambanci da karuwar da za ta shiga ɗaki ka ɗauki kuɗi ka bata, ka yi mata ciki kuma ta tafi ta je ta haihu ta jefar a kwararo. Saboda haka malamai suke ganin aure ya kamata a yi shi da niyyar  zama dindindin. Idan wata ƙaddarace ta kawo aka samu rabuwa, wannan kuwa abune da  yake iya faruwa o ya ƙi faruwa. Amma kada a riƙa yin aure da niyar cewa za a buɗe ƙofar a sake ta zuwa wani lokaci. Idan kuma mutum ya bada ƙofar wannan to shima zaka ga ya haifi 'ya'ya kuma azo a dinga yi musu irin wannan. Kamar ma misali yanzu da zaka riƙa ganin ɗalibai a cikin makarantu kawai sai ka ji an ce wance da wane wai sun yi auren mut'a. Saboda haka su samari ne yanzu  abin yana kan ganiyarsu, ba za su gane illarsa ba sai lokacin da suma suka yi 'ya'ya  suka tura makaranta aka yi masu irin wannan abun, sannan mutum zai ji ciwon abun. Tunda yanzu shine yake yi da 'ya'yan wasu, ba zai ji zafi ba kamar lokacin da za a fara yi da nasa. Don haka idan mutum

ya buɗewa kansa ƙofar ɓarna yana ga kamar lokacinsa ne shi yayi ɓarnar, to lokacin da za ta juye shima ta koma cikin gidansa da iyalansa da matansa da ʻyaʼyansa da sauransu, to a lokacin sai ka ga abun yayi yawa. Kuma in ka buɗe wannan ƙofar, za a riƙa yi da ʻyan mata, za a yi da matan aure, matarka ma tana iya zama da aurenka kuma ta je ta auri wani da wannan niyar. Ko ʻyarka ta tafi makaranta ta auri wani ta je tana saduwa da shi har ya yi mata ciki, kuma wai aure suka yi kai baka sani ba. To duk irin waɗannan abubuwa su shariʼa take duba da shi take toshe ƙofar ɓarna kar ta shigo cikin addininn musulunci, domin ba a san iya inda zata tsaya ba kuma ba a san irin ʻyaʼyan da za a samu ta wannan mugunyar hanya ba.  Wanda za su zo su zama tashin hankali ga addini da alʼummma da ƙasa baki ɗaya.

Tambaya Kan Aure 10

To kuma akwai wani aure shi kuma da ake kiransa ʻazziwajul urfiʼ. Shi kuma wannan aure abinda ya sa bai halatta ba, ɗalibai ne suke yin sa a sirri a tsakaninn su. Ɗaliba ta shiga jamiʼa za ta yi shekara 4 ta yi digiri ko sama da haka. Haka ɗalibi ya zo, to sai su haɗu da abokansu sai a ce to maimakon wane yana son wacce su dinga zina, kuma in an ce a yi aure babansa ba zai yarda ya yi masa aure bai gama makaranta ya samu aikin yi ba. Itama iyayenta ba za su yarda su yi mata aure ba saboda bata gama karatu  ba. Don haka mu je mu a tsakaninmu ɗalibai muje mu ɗaura musu aure, mu rubuta takarda amma a yi auren a ɓoye. Saboda haka lokacin da suka gama makaranta da ma da aurensu, kawai sai mu je mu ce wa baba kawai wane yana son wacce. Saboda haka su za su ga sun sake ɗaura aure, amma namu suka jaddada. Dama can ya aureta saboda wai kada su yi zina.

Wannan a wasu ƙasashe an samu irin wannan auren wanda malamai sukayi tir da shi. Saboda “walanikaha illa bi waliyyin”, “wa la nikaha illa bi izni waliyyin”. Babu aure sai da izinin waliyi. Ba za ta yiwu a yi aure a ce waliyi bai sani ba. Kawai ɗalibai su taru su ɗaurawa wata ɗaliba da wani ɗalibi aure. Iyayenta a gida su suna ɗaukar ta a matsayi ɗaliba, amma su suna ga matar wani ce wanda suke muʼamala a jamiʼa. Wai suna yin haka ne don su kauce wa yin zina. To wannan auren bai halatta ba. Kuma a nan ne muke bada shawara ga iyaye waɗanda ʻyaʼyansu suna buƙatar aure, har ma wasu kunya ta sa sun gayawa iyayen, wato sun daure sun gaya wa iyayen, wasu kunya ya sa sun cije amma suna gayawa wasu,

cewa itafa ta matsu tana son aure amma babanta ya matsa sai ta gama karatu. To wata idan ba Allah ne ya so ta ta samu kariya ba, sai ka ga cewa ta shiga harkar lalata.

Ita kuma abinda yasa Annabi ya ce matasa maza da mata su yi aure da wuri, saboda kada mutum ya fara da lalata. Idan saurayi ko budurwa, abin da ya fara buɗe ido da shi shine zina, to ko ya yi aure ko ta yi aure, in ba Allah SWT ya ba da kariya ba, za ka ga cewa sai an ci gaba da wannan muʼamala ta zina ko da bayan aure. Saboda haka wannan mun sha jin ƙissoshi da labarai, wanda ake kama mutum yana da mata amma bai dena zina ba. Ko mace tana da miji ba ta dena zina ba. To mafi yawa abinda yake jawo wannan sabo da zinar tun kafin a yi aure. Aure shi ya zo da ga baya, to ka ga abinda aka saba da shi, aka fara biyan shaʼawa dashi sai a ɗauka ya fi komai daɗi.

Saboda haka sai ka ga mace tana da aure amma tana da tsohon saurayinta ko tsohon masoyinta, wanda har wasu ma jawo irin waɗannan suke yi cikin gidaje wanda ake kira kwartaye. Ta jawo shi idan mijin ta ya yi tafiya ko baya nan, sai ta zo su yi mumunar muʼamala. Musamman kuma yanzu da yake akwai waya; ana samu ka ga mace tana haʼintar mijin ta. Tana muʼamala da wasu mazaje tana musu waya suna alƙawari suna haɗuwa a wani guri. Shi miji an barshi nan sususu matarsa wani yana anfani da ita. Ko shi mijin ka ga cewa shima ya riga ya saba da muʼamala da matan banza. Gashi ya auro mace ta sunna ta aure, amma sai ya ajiye ta a gida ya fita waje yaje yana muʼamala da karuwai da fasiƙai. Kuma yayi ta ɓoye mata- a yi ta waya ana shirya ajanda iri iri. Wani ma don cin mutunci, a gaban matar ake yin waya da waɗancan matan na waje kuma tana ji kuma ba maganar aure bace, magana ce ta fasiƙanci da lalata. To ka ga wannan duk binda yake jawowa shine sabo da saɓo kafin mutum ya zo ya yi aure.

To in aka yi maza da wuri aka yiwa mum aure to an toshe ƙofar. Bai ma san wani abu a rayuwarsa ba sai ta auren. Zinar bai fara ta ba, bai saba da ita ta zame masa jiki ba. Saboda haka daga anyi aure sai ka ga an zauna lafiya. Ba dalili bane ba hujja bace karɓaɓɓiya a shariʼa ko a hankali ka riƙa bawa ʻyar ka abinci tana ci kana bata kayan shafawa tana shafawa, kana ba ta kayan kwalliya shaʼawar ta tana ƙaruwa, niʼimar jikinta tana ƙaruwa kuma ka ce ba za ta yi aure ba. To ka ga ka buɗe mata ƙofa. Yadda take buƙatar ta ci ta sha, haka kuma take buƙatar wanda zai kwanta da ita. Idan ba a bata dama ta yi shi akan adddini ba, to kuma za ta iya

yinsa ta hanyar da bata dace ba. Saboda haka wannan ba uzuri bane, ba hujja bace, cewa wai karatu in ana yinsa ba za a yi aure ba sai an gama kuma alhali an isa auren. Wata ma inda ana wuce auren ai muce ta kusa wucewa. To wannan shima malamai sun tattauna cewa wannan auren bai halatta ba.

Sannan akwai wani aure da ake kira ʻaz ziwajul misiyar.ʼ, wato auren ɗauke sandarka. Amma shi irin wannan ɗin ya bambanta da wanda muka sani a ƙasar mu. Shi wannan yadda ake yinsa shine, mace ce maʼaikaciya ko wace take da hali take da arziki, ko kuma dai ta kai wani matsayi a muƙami ko a kuɗi ko a shekaru. Idan wani ya fito ya ce zai aure ta sai su yi yar ejeniya saboda ita ce ta fi bukatar auren, akan cewa za ta ragewa mijin ko za ta saukewa mijin wani haƙƙi domin a yi auren. Kamar ta ce to ni maʼaikaciya ce, ina aikin gwamnati don haka in muka yi aure da kai to za ka bani dama in ci gaba da yin aiki na. Kai kuma na ɗauke maka ci na da sha na da kuma yin tufafi. Abinda nake so kawai ka riƙa zuwa inda nake, a gidana zan zauna sai ka riƙa zuwa. To wannan shi ake kira ʻaz ziwajul misyar.

Ko kuma mutum ya yi aure ɗin da sharaɗin cewa to ni ina da arziƙi ko ina yin kasuwanci. Mun yi wannan aure da kai amma ba zan ɗora maka nauyin wahalhaluna ba saboda sun yi maka yawa ko sun yi maka nauyi, don haka na sauke maka cikin haƙƙoƙi na kashi 50 cikin 100. Wato ka bani abinda ya sawwaƙa ni kuma zan riƙa cikawa ina kaiwa daidai buƙata ta. Wannan shima ana kiransa az ziwajun misyar saboda an yi su da wani sharaɗi ko kuma matar ce ta sauka daga wani sharaɗin ta. Ko ta ce na san kana da iyali kuma kana cikin gidansu, ina so ka aure ni amma ba sai an fraba kwana da ni ba, duk san da ka samu lokaci kawai ka bushi iska, ni dai mijin na ke so kawai don in samu rufin asiri. Ko ta ce ko ina na shiga a ce ina da miji don na yi ƙima. Saboda haka duka sanda ka samu lokaci kawai ka zo ba sai an raba kwana da kaza ba, aʼa duka sanda aka samu zuwa kawai sai a zo. Wannan waɗanda suke yin aiki na tafiye-tafiye, kamar wata za ka ga tana cikin masu kula da jirgin sama, kullun suna sama, ko tana tafiya wani gari ta yi kasuwanci, ta tafi watanni, to ka ga anan ba maganar rabon kwana da ita. Saboda haka sai tace duk sanda nake nan abinda ya sawaƙa kawai a zo wuri na in ba na nan kaza. To irin wannan shima malamai sun duba shi ta ɓangarori guda 2.

-: Na farko suka ce haƙƙoƙin na matar ne. Dama shariʼa ce tace a bata waɗannan haƙƙoƙin na ci da sha da tufafi da sauran su. Idan ta ga cewa za ta iya haƙura da haƙƙoƙinta kuma haƙƙoƙin nan basu shafi wani haƙƙi da ya zama wajibi na

haƙƙin Allah ba nata ne, to ana iya yin wannan auren. In dai an yi wannan yarjejeniya da shraɗi sai a yi a rubuce domin kada daga baya ta zo tace akwai haƙƙoƙinta da ba a bata ba. To wasu malaman suka ce in an yi wannan a rubuce to ba laifi ya halatta. Wasu malaman suna ganin aʼa bai kamata a yi aure da sharaɗin za a soke haƙƙoƙin da ya shafi auren ba duk da cewa ita macen ce ta saryar da haƙƙoƙin ta. Amma akwai haƙƙoƙin da in ta saryar da su duka ba za a yarda ba. Kamar ta ce, mun yi aure amma da sharaɗin ba zaka sadu da ni ba. Ko mun yi aure da sharaɗin ba zan haihu ba, zan dinga shan maganin da ba zan haihu ba. To wasu malamai suna ganin waɗannan shruɗɗa guda 2 bai kamata a sa su ba. Domin rashin saduwa da ita ai matsala ce sannan kuma ba za ta haihu ba shima matsala ce- sai dai indan ba ta haihuwar.

Amma idan lalura gareta wacce ta hanata haihuwa, ko kuma ta ɗauki ciki da za ta riƙa shan wahala, wataƙila ma ya kai ga nakasa ta ko salwantar rayuwar ta, to anan malamai sun yarda da cewa in ta ce "na yarda zan aureka amma da sharaɗin ba zan haihu ba saboda likitoci sun ce bai kamata in haihu ba, ko in na haihu zan sha wahala ko zan gamu da wata babbar lalura". To anan idan an yi aure da wannan sharaɗin to babu laifi. Kamar yadda idan mutum zai auri mace maʼaikaciya sai ta ce masa "to ni ka ga ina yin aiki, saboda haka sai dai muyi yarjejeniya da kai akan bayan mun yi aure ma zan cigaba da yin aiki na in ka yarda. Idan ba ka yarda ba shikenan". Shima yana iya cewa "to nima ina da sharaɗi na, a wajen aikin nan na ki sai kin yi min alƙawarin za ki kare mutuncinki za kuma ki kare mutunncina. Kuma za ki riƙa yin shiga ta addini. In kin yarda da wannan sharaɗin nima na yarda ki yi ikin. Sannan idan aka kai wani mataki da muka tara ʻyaʼya  dole ki yi ritaya domin mu zo mu tarbiyanci ʻyaʼyan, kada lokacin da ƙarfin ki ya ƙare kuma ba a raini yaran ba kuma su zo basu da tarbiya. Kuma sannan mun tsufa muna buƙatarsu su kuma suna buƙatar mu a lokacin bau saba da mu ba." Akwai maʼaikata  da yawa da suke shiga wannan matsalar. Ta tafi koyarwa ko ta tafi aiki ta bar ʻyaʼyanta a hannun ʻyar raino. ʻYar rainon nan ba ʻyar uwar uwar su bace, ba ʻyarʼuwar unbansu bace. Ba dole ne wannan ʻyar raino ta ba waɗannan yara kulawa yadda ya kamata ba. Saboda haka ma wani sai ka ga sun tashi ma suna shan ƙwaya, wasu sun tashi cikin wahala, wasu basu saba da ita ba. Lokacin da za ta shekara 35 tana aikin gwamnati ta yi ritaya ƙarfin ta ya ƙare kuma yaran ba masu tausayinta bane. Sai ka ga cewa kuma ta gamu da ciwon zuciya saboda wahalar

ʼyaʼyan da za ta sha wanda kuma ba ta yi aiki na shekara 35 ɗin da ta yi a wajen rainonsu da kulawa da su ba. Saboda haka sai ka ga ƙarshe an zo ana nadama.

Abin da malamai suka ce idan mace tacewa mijinta "na ɗauke maka ciyar da ni." To anan babu laifi domin ciyarwa abu ne da yake a fili. Amma abinda ba za ta ce ba shine "na ɗauke maka saduwa dani ko kwanciya da ni ko na ɗauke maka haihuwa ba." Waɗannan guda biyu ɗin ba lalura bace kamar a ce dama an san tana da lalura a gabanta wanda ba za a iya saduwa da ita ba. Amma tana son ta samu miji domin ta samu rufin asiri. Sai ta yi wa mijin alƙawarin cewa "ba maganar saduwa saboda ina da lalura, sai dai kawai ka zo mu kwanta." To idan ya yarda da wannan shikenan, amma fa sai idan akwai lalura.

Hakanan idan ta ce "an ce mini bazan ɗau ciki ba, ko in na ɗau ciki zan nakasa saboda haka ina son ka aure ni amma da sharaɗin ba haihuwa." To wannan shima idan akwai lalura waɗannan abubuwa guda 2 ana iya karɓar su a matsayin sharaɗi kafin a ɗaura aure. Amma idan babu lalura waɗannan guda biyun ba za a yarda mace ta sharɗantawa rashin haihuwa ko rashin saduwa ba. Amma idan ta ce na ɗauke ma abinci ko na ɗauke ma abin sha ko kuma tunda ina yin aiki kana aiki kuma na ga ƙarfin mu ɗaya ko ƙarfina bai kai naka ba, to wurin gudanar da gida ka riƙa ba da rabi nima ina bada rabi. Ko kuma "yaran mu mun kaisu makaranta na san tana da tsada. Albashin ka ba zai iya ɗaukar nauyinsu gaba ɗaya ba, to kai ka ɗauki nauyin wane da wane, ko wane da wance, ni kuma zan dinga ɗaukar nauyin wane da wance tunda duk ʼyaʼyan mu ne." Saboda haka anan idan maccen ta yarda shikenan babu matsala. Amma idan mace ba ta yarda ba komai arziƙinta, komai kuɗinta; shi kuma miji komai talaucinsa wajibi ne ya ciyar da ita. Ba zai ce ai tunda kina da kuɗi ba; don akwai mazan da idan matansu suna da hali sai su dena basu abinci wai tunda kina da kuɗi kina da hali, kuma na leƙa ma naga an kawo miki kaza daga gidan ku. To sai ya ɗauke ƙafa a daina ba ta abinci har sai wannan abun da ta samu ya ƙare, to wannan zalunci ne. Ba a laʼakari da arziƙin mace a shariʼa a ce ba za a yi mata kaza ba. Ko kai ka fi kowa talauci a ƙasar nan kuma ka auri wacce ta fi kowa arziƙi a ƙasar nan, to ba z ka zo ka zauna ba sai dai ka tafi nema ka je ka awo mata abinda Allah ya sawwaƙe maka. To, Hajiya ko Hajjaju ko Wance ko Mrss Wance, abinda Allah Ya hore mini a matsayina na mijinki talaka wanda kin sani, rogo na kawo miki da gyaɗa da ƙuliƙuli. Sai ta ce to madalla na gode. Bayan ta karɓi rogo da gyaɗar da ƙuliƙulin, sai tace to shikenan kuma a je a

sayo wani abun a haɗa a dafa. Ka ga wannan ita ta ga dama. Ko kuma abinda mutum zai iya ba ta, ya ce "to Hajiya kin ga bani da ƙafi. Abinda da zan iya baki kullun shine Naira 300. Naira 100 da safe, Naira 100 da rana, Naira 100 da daddare. Don na ga wasu haka suke yiwa iyalansu. Ba maganar girki ko maganar kaza. Kawai kuɗin ake yankawa a yi albashi. Wannan ma yana nema ya zama a wasu guraren ƙa'idar da ake bi kenan, sai mutum yayi lissafi gwargwadon ƙarfin sa. Wani ya ce ɗari biyar biyar zai riƙa bata safe da rana da daddare. Don haka duk wata ba ruwansa da girki ;ko waye kawai zai Naira 45,000 ya bata, ita kuma a ciki za ta sayi kayan cefane da duk abbinda take buƙata ta yi abinci. Saboda haka shi baya cikin waɗanda za a yiwa abinci. Ko ya zo ko bai zo ba, ko an yi ko ba a yi bas hi baya cikin lissafi. Ko kuma ya zo an yi abinci shikenan a bashi. Wani kuma zai ce zai ba ta Naira ɗari bibbiyu, saboda haka za a lissafa na wata sai ya bata. Wani kuma ya ce ɗari uku-uku, wani dubu ɗai-ɗai, yace duk wata zan baki dubu talatin kuɗin abincin ki. Ke kuma kika san me za ki saya me za ki girka. Amma dai kada a tambaye ni abinci har sai wata ya cika. Ke kuma kika san me za ki ci me za ki sha ke da 'ya'yan ki. To akwai ma su yin haka.

Idan ta yarda ba matsala ai dama haƙƙinta ne. Duk abinda yake haƙƙi ne na mutum ya kamata a kiyaye shi. Akwai haƙƙi wanda mun ce na tarayya ne. Ka ga kamar saduwa ai haƙƙi ne na tarayya, 'ya'ya haƙƙi ne na tarayya amma cin abincin matar haƙƙinta ne. idan ta saryar to babu matsala. Hakanan kuma idan shi, misali yace to shikenan, ta ce to ni sharaɗina da zaka aure ni shine ina yin karatu saboda haka ba zaka dakatar da ni ba har sai na gama karatu na. To idan ya yarda da wannan, aka rubuta a matsayin yarjejeniya, to ba shi da iko, bashi da dama ya dakatar da ita daga wannan karatu. Dole ne ya bata dama tunda ya yarda kafin a ɗaura aure. Da yawa mata sukan kawo ƙara cewa mijina ya yarda zan yi karatu. Da ya samu ya lallaɓani na shiga ɗakinsa, kawai shi kenan sai ya ce ba zanyi ba. Tunda yanzu ta riga ta zama maytar saka ga ba yadda za a yi dole ta haƙura ta bi shi amma dai abin yana cinta a rai saboda an mata alƙawari ba a cika ba. To wannan duk mutumin da ya san mace tana da sharaɗi wanda bai saɓawa Allah ba kuma shi ba zai iya cikawa ba to kada ya aure ta sai daga baya kuma ya zo ya ce zai hanata ko kuma zai shiga cikin haƙƙin ta.

Akwai kuma wacce za ta ce ni na san kana da mata dan haka zan aure ka amma sharaɗi na ba zaka haɗa mu a gida ɗaya ba, ko wacce gidanta daban. Idan ya yarda

da wannan sharaɗin fa dole ya cika. Domin asali mata kamata ya yi su zama gidan su daban-daban, ba a haɗa su sai da izinin su, haka shari'a ta ce. Mu nan matan mu ne Allah ya basu haƙuri da juriya. Shi yasa za ka ga mafi yawan ƙasashe idan ka shiga a duniya da wuya ka ga inda ake haɗa mata banɗaki ɗaya, rumfa ɗaya, kicin ɗaya, tsakar gida ɗaya, ɗaki ne kawai ake rabawa, amma shekara da shekaru a haka a ke zaune. Sai matan mu na nan. A nan kam ya kamata a yabawa itama matar Bahaushe da ake cewa itama tana kaza da kaza.

To idan mutum bashi da halin da zai yi gida daban-daban, ya nuna mace ɗaya zai iya kenan. Ka ga bai kamata ya yi mata biyu ba. Idan mutum ya san ba zai iya tanadawa mata gidan da zai ishe su yalwata ba, to bai kamata ya yi da yawa ba, sai ya yi guda ɗaya. Sai ya jira in Allah ya hore masa ya ƙara gina wani gidan sai ya sake yin guda ɗaya. Idan  Allah ya sake hore masa sai ya sake aurar wata. Ko da ma a ce zai yi gidan guda ɗaya, to akwai buƙatar da bai kamata a yi tarayya a cikin ta ba, kamar banɗaki. Ka ga ya kamata ka raba banɗaki ko da ma a ƙalla matan sun yarda a haɗa su gida ɗaya, ko wataƙila kaima kana ga maslahar haɗa su gida ɗayan ya fi domin zai sauƙaƙa maka wajen yin abinci ba sai an yi biyu ba. Ka ga komai ba sai ka sayo biyu-biyu ba. Idan ka sayo ɗaya sai a raba. Hakama ya kamata a raba ɗaki. Saboda haka akwai abubuwan da ya kamata a cikin gida ɗayan ma a raba su. Kaga in aka ce kowacce tana da banɗakinta to ba za a riƙa samun matsala ba. Inda zai yiwu a ce gida ɗayan ne amma ko wacce a ce tsakar gidanta daban ne, ɗakinta daban da rumfarta daban, kicin ɗinta daban, to ka ga a gida ɗayan ake ana haɗuwa ana gaisawa a tsakar gida, amma kuma kowacce tana da ɓangarenta daban. In da hali abinda ya kamata mutum ya yi kenan.

## Tambaya Kan Aure 11

Haƙiƙa mai neman aure kamar yadda muka gabatar ya kasu kashi 5. Tun kafin ma ka fara tunanin za ka yi aure, ka fara tunanin kai wanene. Shin ya ma kamata ka yi auren ko bai kamata ba? Sannan abinda ake buƙata kafin aure, kana da su ko baka da su?

Bayan mutum ya yi tunani akan ya ma kamata ya yi auren ko bai kamma ta ba, sannan idan ya ji cewa ya kamata ya yi, to yaushe ya kamata ya yi? Idan ya yanke, to me ake buƙata ya shirya da su kafin aure?

1- Ya zama yana da lafiya ta hankali.
2- Yana da lafiya ta jiki.
3- Yana da wata sana'a wacce ya dogara da ita. Kamar yadda muka faɗa cewa, yanzu wajibi ne idan mutum ya zo neman aure, to a bincika abubuwa guda 3 game da shi. A bincika sana'arsa da asalinsa da kuma addinin a. A tabbatar mutum ne mai tarbiya ta addini sannan mutum ne da yake da sana'a wacce ya ke yi sannan kuma an san asalin daga ina yake. Domin an taɓa yin aure da wani mutumi da ba a san daga ina yake ba. Daga baya ya gudu ya bar matar. Har yanzu tana nan da 'ya'ya kuma mijin ba a san inda yake ba, ba a san dangin uban 'ya'yan ba. To ka ga akwai buƙatar irin abinda iyayen mu su ke yi da, idan mutum ya zo a tambaye shi daga ina ya ke. Idan aka gamsu mutum ne wanda an san asalin sa, kuma aka bincika aka ga mu'amalarsa da addini suna da kyau, to waɗannan abubuwa sai su sanya a ba shi aure.

To saboda haka bayan mutum duk ya gama wannan lissafin, sai ya fara tunani wacce mace ya kamata ya aura? Waɗanne irin siffofi ne ake so ga macen da zai aura? Saboda haka waɗannan siffofin sune za mu yi bayani wanda ya kamata mutum ya duba su, ko mafi yawansu idan zai yi aure. Ba sai an samu wasu siffofin duka ba; idan dai a ka samu mafi rinjaye ko waɗanda suka fi muhimmanci, ragowar ko babu su sai a haƙura. Kamar yadda ita ma macen za mu yi bayani a kanta; domin kamar yadda na miji yake jin yana da raɗi ko iko ko damar ya zaɓi matar da yake so, to haka nan itama mace tana da dama da 'yanci na ta zaɓi mijin da take so. Sannan wata shawara da za mu bawa miji ko mata wanda suke so su yi aure, ba dole ne duk matar da kake so ya zama tana son ka ba. Haka kuma ba dole ne duk mijin da kike so ya zama yana son ki ba. Maiyuwa ke ta ɓangaren ki za ki ga ya cika sharuɗɗan da kike buƙata. Shi kuma ta ɓangaren sa ba ki cika sharuɗɗan irin matar da yake so ba.

Haka nan mai yuwa kai wannan matar ta cika dukkan sharuɗɗan da kake so, amma kuma ita in ta kalle ka, itama tunda tana da na ta sharuɗɗin da burika, sai ta ga ba ka cika sharaɗin su ba. To wannan ne sai ka ga an samu matsala. Kana son matar da ba ta son ka. Ko kina son mijin da ba ya son ki. Saboda ke ce kike so ɗin don kin ga yana da abinda za ki so shi. Amma shi ya kalle ki sai ya ga ba ki da abinda zai soki.

Haka na faruwa ga mazan, yana faruwa kuma ga matan. Shi yasa wataran muke ganin ya kamata masu neman aure maza da mata su rage buri. Babu wani abu yanzu da za ka same shi ɗari bisa ɗari. Saboda haka idan kina so ki yi aure, mijin da za ki aura, cikin burikanki 10 da kike da su a kan sa, ya zama yana da 6, kuma a ce muhimmai ne, to sai ki haƙura da guda huɗun da bashi da su. Hakanan kaima cikin siffofin da kake so mace ta haɗa sai ka samu wasu mafi rinjaye, ko mafi muhimmanci, to ba dole sai ka sami wacce ta cika dukkan sharuɗɗan da kake buƙata ba. Mai yiyuwa wacce ta cika sharuɗɗan ta fi ƙarfin ka. Kema maiyuwa wanda ya cika sharuɗɗan ya fi ƙarfin ki. To kullum idan ka ga mutum yana shiga rigima a duniya, to yana zuwa inda aka fi ƙarfinsa ne. Saboda haka ba wata matar da ba ta da miji. Babu wani mijin da bashi da mata. Amma matsalar itace, kullun mutum yana neman abu ne da ya fi ƙarfinsa. Saboda haka yana neman mata ta sama da shi. Itama tana neman miji na sama da ita. Amma da za ka nemi daidai da kai ko na ƙasa da kai to ba za ka rasa ba. Idan kai talaka ne ba ka da hali, akwai 'ya'yan talakawa da suma ba su da hali kuma basu sa buri da yawa a ransu ba, sai ka je nan. Amma ka taho a kan keke, ka tafi gidan da idan za ka shiga gidan ma sai an baka buta ka wanke ƙafarka, sanan ka ce nan ka zo neman aure? Ka ga idan aka wulaƙanta ka kai ka jawowa kan ka. Amma idan ana sonka ne aka jawo ka, to ka ga jawo ka aka yi. Amma kar ka je gurin da ka san cewa ba za ka samu kyakkyawar lale da marhaban ba.

To malamai sun yi dogon bayani cewa daga cikin abinda ya kamata mutum ya duba idan zai auri mace, wato za mu fara da siffofin ita matar kenan, ta zamo ma'abociyar adini. Addinin nan na da muhimmaci saboda Allah y ace...

Wato "mace ma'abuciyar addini, baiwa mumina ita tafi alheri daga mushrika ko da ko waccan ta ƙayatar da ku." Kuma Annabi ya ce.... Wato "ka rabauta da ma'abuciyar addini. Idan ka ƙi hannun ka zai yi turɓaya." Saboda haka wajibi ne mutum ya kiyaye hannunsa kada ya yi turɓaya. Kamar yadda ya zo a hadisin Buhari, me lamba ta 5090 da hadisin Muslim mai lamba ta 1466, cewa lallai mutum idan zai yi aure to ya tabbatar cewa matar da zai aura abin da zai fara dubawa a cikin siffofin da ya ke so shine addini.

Mutane da yawa sun ɗauka idan an ce a auri mace me addini ana nufin kada a yi la'akari da ragowar siffofin, a'a bah aka bane; ragowar siffofin suna tafe. Wani yana son mai addini kuma mai kyau. Ka ga ba za ka ce ya ɗauki mai kyau kawai

ko mai addini kawai ba. Dole mai addinin da ya ke so sai ta zama kuma kyakkyawa. To ba zaka hana shi ka ce idan an samu mai adddini kuma mara kyau sai ya aura ba. Ko idan an samu mai kyau mara addini sai ya aura ba. Sai a bar shi ya yi ta bincikawa har sai ya samu wacce ta kwanta masa a rai kuma mai addini. Domin wata tana da addini amma ba ta kwantawa mutum a rai ba. To idan ya rufe ido ya aure ta haka, ana ganin ta kullum alaramma ce ko ustaziya ce. Ta cika siffofi na ustazanci amma kuma bata cika siffofin halitta na irin wanda mijin ke so ba, to idan suka yi rigima ya sako ta sai a ce "ka ga mutumin banza, yanzu wannan baiwar Allah, wannan waliyya, wannan saliha mai kwana karatun Alƙur'ani amma ya sake ta." Saboda ba wannan siffa kaɗai yake buƙata ba. Wannan siffa ce tsakanin ta da Allah, kuma hakanyana da kyau. Don wacce ta riƙe addini yana da kyau ka ga tana gyara tsakanin ta da Allah.

To kuma akwai abinda shi mijin yake so. Sai ka ga wani yana son mai addini amma fara yake so. Wani na son mai addini amma doguwa yake so. Wani na son mai adddini amma mai haƙuri yake so. Wani na son mai addini amma wacce ta iya mu'amala ta goge yake so. Domin an ce mace ta zama mai adddini ba ana nufin ragowar siffofi kuma kar ta iya ba. Kamar yadda wani ya kawo ƙarar matar sa; ya ce ko shigowa yayi gida sai ta nemi hijabi ta saka. Kuma sai ta yi ta salla da tsakar dare, ta ɗauko ƙur'ani ta yi ta karatu da rana. Ba a wata hira ta duniya sai dai ƙalallahu, sƙala rasulu. Saboda haka sai mijin ya ga ai wannan shima yana da lokacinsa. Karatu yana da lokacinsa, zikiri yana da lokacinsa, addua na da lokacinta, hira ma na da lokacinta.

A saki jiki a yiwa miji hira. A kawo masa abinci da ruwa sannan a yi masa kwalliya. Amma wata matar idan mijin ya ce ta yi kwalliya ta sa kaya tsukakku wanda za ta riɗa sakawa a gida, sai ta ce ita ba 'yar iska bace. Ko idan ya zo za su yi wani wasa da ita sai ta ce ita wannan iskancin fa ba ta iya ba. To ka ga anan ga ta da addinin amma kuma ba ta da wayewa ta rayuwa. Saboda haka ba yana nufin don mace mai adini ko mutuniyar kirk ice kuma ya zamana baki da wayewa ta rayuwa ba. Tabbas wannan abune mai kyau, amma bashi yake nufin kuma a ce ba ki iya girki, kwalliya, tsabta, Magana, iya kallo, karairaya da sauran abubuwa da za su riƙa jan hankalin mijin ki ba. Ba kuma ana nufin don kin iya waɗannan sai kiyi watsi da addini ba. Matsalar da ake samu, wasu da suka iya irin waɗannan abubuwan, sai kuma ka ga babu addinin. Ga girki za a yi, ga kwalliya, ga tsabta, ga

iya Magana, ga iya fari da ido, za a yi maka ɗaurin ɗankwali iri iri, a yi maka wasa kala-kala amma kuma idan lokacin sallah ya yi sai da rigima za ka tashe ta ku yi sallar. Kullum idon ta yana kan Zee Aflam. A kalli fina-finan India da safe, a kalla da rana da wasu lokutan. Kullum ba addini amma kuma kai tana kyautata maka. Amma alaƙarta da Allah kuma ba ta gyarawa. Ka ga mai irin wannan halin ba za a aureta ba kuma bai kamata aureta. Hakanan kuma don kina da alaƙa mai kyau da Allah, kina sallah, kina zikiri kina salatin Annabi,kina dai kula da addini, ba kuma shi yake nufin ba za ki iya waɗancan abubuwan da za ki ja hankalin mijin ki a zauna lfiya ba.

To matar da ta haɗa duniya da lahiran nan, tana da wahalar samu. Mafi yawa 'yan duniyan basu san lahirar ba. Mafi yawa sukuma waɗanda suka damu da lahirar, basu goge a harkar duniyar ba. Saboda haka sai ka ga waɗancan su matan su sun iya komai. Sun iya duk wani abu na farantawa miji rai. Akwai wanda ma ya ce matar sa ta iya aski kuma tana da abin aski, saboda haka ita ce ta ke masa askin hammata, askin gaba, har ma da askin gashin kansa kai. Ita take yanke masa farce, ta ce ba za ta bari wani ƙato ya yankewa mijinta farce ba. Zuwa ta yi ta koyi yadda a ke yi, kamar yadda ake horas da wanzamai da masu askin baba, itama sai ta je a yi mata irin wannan horon.  Da ma ya kamata a ce nan gaba matan aure a riɗa basu horaswa. Domin nan gaba ma saboda tsaro, ya kamata a ce matan aure ne za su riƙa yin irin waɗannan abubuwa. Saboda haka sai ta je ta koyi duk waɗannan. Hatta goge takalmin nan, shi mutumin ya ce bay a bawa  shushaina ya wanke masa saboda matar tasa duk ta sayo kayayyakin goge takalman. Su kuma tufafinsa na ciki, irin su gajeren wando, singileti da safa duk ita take wankewa. Tana kuma da dutsen goge wanda ta ke amfani da shi wajen goge masa kayansa na sawa. Ka ga wannan ai abune mai daɗi; an haɗa komai. Duk kusan komai ita take yi masa. To amma kuma ya ce mini idan an zo sallah, sai a yi ta fama da ita. Ta yi kallo da yawa ta gaji, don haka sai ya zo yai ta fama da ita da asuba a kan ta tashi ta yi sallah, ko da rana ma y ace a tashi a yi sallah. To ka ga shi kukan da yake kawowa shine, ta ƙware a kan harkar duk yadda za ta faranta masa rai, amma bata kula da addini. Ya ƙara da cewa idan ya fita, kafin ya dawo, nau'ukan lemo, da nau'ukan ruwa da sauran ababan sha, sai a yi masa kala goma. Wani a yishi da karas, ayaba, lemon fata da sauran kayan marmari. Wani ayi mai kala 2 wani mai kala 3, har da mai kala 5 a guri guda. Sai wanda yake so zai sha amma kuma ba ta kula da addini. Yace nan kaɗai take bashi haushi. Idan ta faranta masa rai ta ɓangaren yadda take

kyautata masa, ya ke sa mata albarka, to idan ya ga bata damu da addini ba- ba za ta zauna ta yi zikiri ba, ba za ta yi salatin Annabi da yawa ba, ba za ta yi hailala ba, ba za ta ɗauki littafi ta yi nazari ba, amma kuma duk abin da zai ɓatawa miji rai ta san yadda za ta kauce mishi ba za ta yi shi ba. Duk kuma abinda zai faran ta masa rai tana yi, amma matsalar sa da ita addini.

To shi kuma ga wani ya kawo ƙarar matarsa. Ya ce a ɓangaren addinin duk sati sai ta sauke Al ƙur'ani, kuma azumin Litinin da Alhamis ɗinnan in dai ba al'ada take ba, ba ta fashi. Kuma da daddare ko bai tashi ba za ta tashi ita ta kama Sallah. To amma kuma ba ta da wayewa, ba ta da gogewa, sai ya zo yayi minti 5 ba a kawo masa ruwa ba. Ko ta ce tana nafila ya jira. Ko kawai idan suka kama hira, sai ya ga bakinta yana salati. Sai ya ga to wannan ita kullum sai a yi ta jan hadisi da aya. Ita aya ai tana da lokacin da ya kamata itama a ja ta.

Kamar yadda wani sahabi yake cewa, wato mun kasance idan muka zo gaban Annabi (SAW), idan yana yi mana wa'azi sai ka ga mun yi tsit sai kace mala'iku. Amma kuma idan mun dawo gida, sai mu zo mu yi ta wasa da matan mu, mu yi ta wasa da iyalan mu, mu yita dariya mu yi ta shewa da kewa. Sai ya ce; anya ko wannan ba munafucci bane? Saboda haka sai ya ce, "nafaƙa Hanzalatu", Hanzalatu ya yi munafirci, saboda haka ya zargi kansa. Da suka gamu da wani sahabi, sai ya ce masa "ina jin fa ni munafiki ne." Sai ya ce "a'a me ya faru"? ya ce "to gamu a gaban Annabi (SAW) ana wa'azi, sai ka gan mu kamar ka ɗora tsuntsu a kan mu. Komai mun nutsu mun tara hankali, mun yi tsit da mu, amma kuma in muka dawo gida sai ka ga mun kama hargowa da abubuwan rayuwa." Sai shima sahabin ya ce masa "to ai nima haka nake ji. In haka ne nima na zama munafiki kenan. To yanzuu ya za a yi?" Kowa aka tambaya ma haka zai ce. Sai suka ce to bari mu je mu tambayi Annabi (SAW) mu ji idan wannan abun da muke yi na sakarwa iyalan mu fuska, wanda ya saɓawa yadda muke a gaban Annabi ko hakan munaficcci sai mu dena. In ya so idan mun zo gida sai mu ɗaure fuska, ko mu ci gaba da zikiri da addua da salati.

Saboda haka sai suka je suka gayawa Manzon Allah (SAW) game da wannan hali na su. Sai Manzon Allah (SAW) ya ce, da ace yadda kuke a gabana haka za ku zama a ko ina, to da mala'iku sun sauka suna gaisawa da ku. Domin kun zama mala'iku kenan. In ka zama mala'ika, ka ga mala'ika sai ya sauko ku haɗa abota. Ya ce ai da mala'iku za su riƙa gaisawa da ku domin kun fita daga ɗabi'a ta

mutane kenan kun koma ta mala'iku. "wa lakin sa'atan fa sa'atan". Ya ce ai rayuwa sa'a ce. Wata sa'ar ta karatu ce, wata sa'ar ta barci ce, wata sa'ar ta rayuwa ce. Haka mutum zai karkasa lokutan. Ba ana nufin ka zama mai addini shikenan sai ka yi watsi da duniyarka ba. Kuma ba ana nufin dan ance ka nemi duniya kuma ka yi watsi da lahirar ka ba. Ya ce sa'a sa'a ce. To daga nan hankalin sahabbai ya kwanta cewa zuwa su iya zuwa su yi wasa da iyalan su ko su sakan masu fuska bay a daga cikin alaman cewa sun saɓawa addini.

Kuma wannan shine ya faru tsakanin Salmanul Farisi da Abdarda'i. malam Abu Darda'i, ne ya watsar da matarsa, ya ci gaba da harkar lahira. Kullum cikin sallah da azumi yake. Saboda haka matarsa ta ga cewa kwalliyar nan fa da ake yi don miji ake yi. Sharar gida da sa turare don miji ake yi. To tunda miji ya watsar da ita ya kama wannan, itama bari ta kama gabanta. Sai ta daina shara, ta daina gyara jikinta. To kuma shi Salmanul Farisi, bayan musuluntar sa da yiwo hijirar sa zuwa madina daga can yankin Farisa, sai Annabi ya haɗa su bota da 'yan'uwantaka da wannan sahabin. Dan haka sai ya zama duka sanda ya dawo daga kasuwa ko daga wajen aiki ya kan biya ya tambayi halin da abokinsa da matarsa suke zaune. Idan ya ga wani abu na gyara, ya gyara musu.

To da yazo gidan rannan, shi Abu Darda'i baya nan, sai ya tarar da matarsa ta yi butu-butu gidan ma ya yi busu-busu. Sai ya tambaye ta ya ce lafiya Ummu Darda'i na ga gida haka? Sai ta ce to ai ɗan'uwan naka ne bashi da buƙatar komai a duniya. Ya watsar da ni ya kama azumi da sallah, shi ya sa nima naga bani da buƙatar na yi ta ɓat wa kaina lokaci ina girki da kwalliya da tsabta da ƙunshi da kitso. Duk bai damu da waɗannan ba. Don haka nima sai na ajiye wannan. Sai ya ce to kawo mini abun shinfiɗa. Ya samu wuri ya zauna ya jira shi. Can ko sai ga Abu Darda'i ya dawo. Yana zuwa ya yi marhaban da Salmanu tunda ɗan'uwansa ne na musulunci. Sai suka zauna. Shikenan ya ce a dafa masa abinci. Sai aka dafo masa abinci aka kawo masa. Sai shi kuma ya tura gaban Salmanu. Sai ya ce "bisimillah". Sai Salmanu ya ce kai fa? Sai ya ce ni azumi nake yi. Salmanu ya ce to wallahi sai ka ci, wannan azumin naka sai ka karya shi tunda na nafila ne. To a nan ne ma aka nuna cewa idan mutum yana ibada za a iya sa shi ya barta dole. Haka dole ya karya azumin saboda Salman ya riga ya rantse kuma ya tsaya don ya tabbatar da cewa ya karya azumin. Saboda shi Salman ya ga azumin na Abu Darda'i ya wuce na nafila kuma yana nema ya dinga cutar da matarsa.

Sai ya karya azumin suka ci abincin tare. Ya kuma ce "yau a gidan zan kwana na ga da dare me kake yi, tunda na rana ya ga azumi ya ke yi ya kuma sa ya karya shi. Da dare ya yi sai Salman ya ga Abu Darda'i ya tashi sallah. Sai ya riƙe shi ya ce "barin sallar nan za kayi." Sai ya fasa sallar ya kwanta barci. Can dare ya sake tashi, sai ya kuma riƙe shi; ya sake tashi ya sake riƙe shi. Sai da can dare ya tsala, da Abu Darda'i ya tashi, sai Salman ya ce to yanzu ya kamata a yi sallar yanzu. To da gari ya waye, dama abinda yake so ya gwada masa, kada shagalarka da ibada ta sa kuma ka ɗauki haƙƙin matarka. Sai ya ce masa, ya kai ɗan'uwana, ka sani cewa matarka tana da haƙƙi a kanka, kaima kana da haƙƙi a kanta. Maƙotanka suna da haƙƙi a kanka, dan haka dukkan mai haƙƙi ka bashi haƙƙinsa. Kamar bai gamsu da wannan shawarar ba, sai ya tashi ya tafi wajen Annabi (SAW) saboda Annabi ne zai tabbatar da karɓa ko rashin karɓar  wannan shawara. Da ya je sai ya gayawa Annabi (SAW) duk abinda ya faru tsakanin su da Salmanu na hana shi azumi da Sallar dare, da kuma cewa ya bawa mace haƙƙinta, ya kuma bawa maƙoci haƙƙinsa, ba kawai salla za a yi ta yi da azumi ba alhalin kowa yana da haƙƙi a kanka. Dole ka raba ka ba kowa haƙƙinsa ba tare da ka yi watsi da ibadar da kake yi ba.

Da Manzon Allah ya ji abinda ya gudana a tsakanin su, sai ya ce "sadaƙa Salmanu," wato Salmanu ya yi gaskiya. Ka ga shikenan abinda Salmanu ya ɗoraka a kai na cewa ka kula da iyalinka, to wannan gaskiya ya gaya maka.

Haka an samu wani mutum lokacin Sayyidina Umar, shima kawai da ya karanta wasu surori a Alƙur'ani suka firgita shi, sai kawai ya daina kula matarsa. Idan ta zo da daddare sai ta ga yana ta sallah. Idan ta zo da rana kuma sai ya ce azumin nafila ya ke yi. To ta gaji dai da wannan hali sai ta kai ƙara gaban Sayyidina Umar; ta ce "ya Amiral muminin, mijina salla yake yi da dare kuma azumi yake yi da rana." Sai ya ce ai madalla da miji irin naki, ai kin yi sa'a, ba haka ake so ba? Ke kin auri miji mai ibada ba shikenan ba. To sai ta ga bai fahimci ma saƙonta ba. Sai wani ya ce "ya Amirul muminin wannan mata fa ba wai tana yabon mijinta bane, cewar yana sallah da dare yana azumi da rana to ina haƙƙinta ita? In ana Sallah ana taɓa mace ne? in ana azumi ana taɓa mace ne? ai abinda take nufi shine ka karɓar mata haƙƙinta a wajen wannan miji nata mai yawan sallah da azumi." Sai Amirul muminina ya ce tunda ka fahimci ƙarar to ka je ka kira mijin ka kira ta ka yi masu sulhu.

Saboda haka mutumin aka tafi da shi ya kira mijin ya kira matar. Ya ce to kai me ya faru. Ya ce wallahi wasu surori ne na karanta a Al ƙurʼani sai suka firgita ni. To da na firgita shine na ga gara in watsar da kowa in koma lahira. Ya ce ai duk da ka koma lahirar ai a duniya kake. Wanda yake duniya kuma ai ba zai yi watsi da ita ba. Saboda haka mu ɗauka waɗannan ayoyi da kake cewa sun firgita ka, ka ɗauka yanzu matan ka 4, mai mata 4 ko wacce zai ba ta kwana 1 ne, ko kwana biyu-biyu, ko abinda ya yi sama da haka. To ka ɗauka yanzu matan ka 4 ne, wannan ita ce ta huɗun. Wannan dararen naka kuma na sallah sune waɗannan mata ukun. Idan ka yi ibada yau- ka yi sallar dare ka yi azumi, gobe ka yi sallar dare ka yi azumi, jibi ka yi sallar dare ka yi azumi, to cikon ta huɗu babu sallar dare mai yawa babu kuma azumi domin matarka ta samu lokacin da ita kuma za ka saurare ta. Daga nan kuma ba za ka ƙara sauraren ta ba sai bayan kwana 4. Sai ya ce to ya yarda da wannan. Ka ga kenan bai watsar da ibadar da ta zaburar da shi ba, bai kuma watsar da haƙƙin matarsa ba. To sai ya ce ya yarda da haka.

To shine wannan mutumi ya zo ya gayawa Sayyidina Umar cewa na shawo kan wannan matsalar. Kuma ya gaya masa hanyar da ya bi ya shawo kan matsalar. Matar ta amince mijin ya amince. Sai ya ce to na naɗa ka kaine mai yin sulhu ko alƙali a gari kaza. Ka je ka dinga sulhunta maʼaurta. To kaga wannan hikima ce. Shi yasa muka ce siffa ta farko mace mai addini mutum ya kama ta ya nema. Amma dan mun ce a nemi mai addini ba yana nufin kuma wacce ba ta goge ta san harkokin zamantakewa ba.

Tambaya Kan Aure 12

Muna bayani akan siffofin mace da ya kamata mutum in zai yi aure ya fara bincika su. Mun ce waɗannan siffofi iri 2 ne. Akwai siffofi na ɓoye, akwai siffofi na fili. Siffofi na fili sune waɗanda akewa mace hukunci da su da cewa doguwa ce ko a ce gajera ce ko a ce mai ƙiba ce, ko a ce siririya ce, ko a ce fara ce ko a ce baƙa ce. Ko a ce mai murmushi ce ko a ce mai haɗe fuska ce. Ko a ce mai tsafta ce ko mara tsafta. Ko ʻyar masu kuɗi ce ko ʻyar talakawa ce. Duk wannan abu ne a fili da za a iya gani.

To akwai siffofi na ɓoye wanda su ba a ganin su da ido, sai an yi muʼamala da mutum ake gane su. Kamar a ce mai haƙuri, amana, mutunci, tausayi. Mai muʼamala ce da maƙota, da miji da iyayensa da ʻyanʼuwansa da abokansa da

abokiyar zamanta, da'ya'yan kishiyarta da 'ya'yan maƙota. Ta iya mu'amala tana da hali mai kyau. Wannan abun ba abu ne da za a gan shi a fili ba. Don haka wata sai ka ga Allah ya bata siffofin na baɗini, ma'ana tana da halaye masu kyau, amma ba dole ne kuma a ga siffofin ta na fili sun zama irin wanda miji ya ke so ba.

Wata kuma za ka ga, dukkan siffa ta cika; ta kyau da iya kwalliya da direwa ta halitta Allah ya ba ta. Ita ce abinda bahaushe ke cewa "son kowa ƙin wanda ya rasa", to amma kuma sai ka ga cewa ba ta da hali mai kuyau. To, da siffa mai kyau da hali mai kyau suna wahalar haɗuwa. Idan aka samu mace tana da hali mai kyau, tana da siffa mai kyau, to a riƙe ta kam-kam. Domin da yawa an ga masu hali mai kyau amma ta ɓangare sifa sai ka ga ba a ɗauke su ba. Ko kuma a ga mace mai siffa mai kyau, amma ta wajen hali, sai ka ga ba a ɗauke ta ba. Wani za ka gan shi da kyakyawar matarsa suna rigima. Wani kuma sai ka ga da matarsa da shi, wataƙila wani ba ya ganin kyanta amma suna zaman lafiya; yana ta sa mata albarka. Wani kuma ka ga yana da kyakkyawar mata amma yana ta tsine mata albarka saboda kyan bai amfaneta ba sakamakon ba ta da kyan hali. Waccan kuma munin bai cuce ta ba saboda tana da kyakkyawan hali.

To shi yasa muka ce waɗannan siffofi na farko shine addini. Kuma kamar yadda muka yi sharhi cewa yin addini ta ɓangaren mace ba yana nufin kar ta iya sauran abubuwa na wayewa da rayuwa ba. Kamar yadda kuma siffofin addini ga namiji ba ana nufin shima ya zama wani bagidaje ba ne, don shi addini ba gidadanci ba ne. Don kana da addini don ana ganin kai ustazu ne ko kana da siffofi na zahiri, wanda ake gani na adddini, kar kuma a zo a yi zama da kai ka zama macuci, azzalumi, mai kaushin hali, mai kaushin siffa, mai mummunar ɗabi'a. Saboda cutar da ka ke yi mata har ta wayi gari siffar nan taka ta addini tana tir da ita. Tana ganin wannan abin da kakeyi ma ƙarya ka ke yi ba addini ba ne, domin ta gano haƙiƙanin sirrinka cewa kai ba mutumin kirki bane. To ka ga wannan abin takaici ne. Shi ya sa muka ce to a haɗa waɗannan siffofin guda 2 na zahiri da na baɗini.

To sannan abu na biyu ta zamo cewa tana da ɗaya daga cikin waɗannan siffofi guda 4 wanda ake neman auren mace sabboda su. Manzon Allah (SAW) ya ce, a hadisin Buhari da Muslim "tunkahul mar'atun arba'in; li maliha, wa li jamaliha, wa li hasabiha, wa li diniha...Annabi (SAW) ya ce ana auren mace saboda abubuwa 4. Ba wai kuje ku auri mace don abu huɗun ba. A nan labari Annabi yake bayar wa; cewa duk wanda ya zo ƙofar gidaka ya ce yana son 'yarka ko ƙanwarka ko

babarka, ko ma wacece, to abu 4 ne ya koro shi, ko ɗaya, ko biyu ko uku daga cikin huɗun ya gani. Amma idan mace ba ta da ko ɗaya daga cikin huɗun nan, ba kasafai akan yi cikowa wajen neman aurenta ba. To sai Annabi (SAW) ya ce, wani dukiyar mace yake dubawa. Yana la'akari da Hajiyan nan tana da kuɗi, ko matarnan tana da kuɗi, ko baban matar nan mai kuɗi ne. A ƙalla dai za a rage zafi, ko kuma "in na aure ta auren jari na yi", ko auren hutu ne. Ko y ace "babanta zai saya mana gida ya saya mana mota mu ji daɗi, ko ya bata kuɗi ni kuma ta bani. Ko kuma ya mutu mu ci gado ni da ita mu samu kuɗi." To tunanin wannan shine tuanani farko na waɗanda suke tafiya neman aure ko ɗaya daga ciki ko sashen masu tafiya neman aure.

Wani kuma gani ya yi kyakkyawa ce. Saboda haka kyawun ne ya sa ake ta fakin ɗin mota a ƙofar gidan. Kowa yana zuwa, sai wanda aka ga dama ma za a fito a zo wajen sa. Wannan ya sayo waya blackberry, wancan ya sayo wancan kala, duk haka ake ta yi kowa yana ta ƙoƙari ya shigar da kansa. To ka ga wannan wataƙila kyau ne ya tara mata masoya, ko kuma duk kyau ne ya jawo su.

Wani kuma saboda darajar nasabar ta. 'Yar gidan wane jikar wane ce. Iyayen ta hamshaƙan malamai ne ko kuma hamshaƙan masu kuɗi ne, ko hamshaƙan masu sarauta ne, ko hamshaƙan 'yan boko ne waɗanda suka daɗe a cikin harkar aka san su. Ko wasu shahararrunn mutane ne da aka san su a ƙasa, ko a gari, ko a al'umma, ko a cikin ƙabila. Sai ka ga ana ta gaggawar zuwa, domin idan mutum ya auri ɗaya daga ciki ko 'yar gidan, to shima darajarsa ta ƙaru ta ɗaukaka. Ka san akwai mutumin da darajarsa take ɗaukaka da matar sa. Shi ba za a gane waye ba sai an ce ai mijin wance ne, sai a ace to shi ne wannan? To kaga ta hanyar matar ake sanin sa. Ko kuma in aka ce ai wane ne mijin ta. Wane? lallai ta yi sa'a. Ka ga ta tashi da mijin, wato sai an raɓa shi ga wani sannan shi kimarsa take fitowa. Shi a kan kansa bai da wata kima da za a ambaci sunansa shi kaɗai ba a raɓa shi ga wani ba. To shi ba wani sannannen abu bane. Sai an ce, ko kuma a ce ai ɗan wane ne sai a ce to!, ɗan wane ne? to tunda an san wanen to shi sai ya ci albarkacin wannan mahaifin nasa, ayi kwatancen sa da mahaifin na sa.

To akwai kuma wanda shi a kan kansa ne da ka faɗeshi, shi ne darajar. Shine wanen. Da 'ya'yan sa, da matansa, da jikokin sa da sauran su duk suna taƙama ne da shi saboda shi shine wanen. Shi kuma ba wai baban sa ya gada ba ko wani, a'a shi shine wanen kuma ake raɓuwa gare shi. To akwai waɗanda suke zuwa neman

aure saboda wannan. Saboda wane ne baban ta. Saboda haka in aka ce ka auri ʻyar wane, ko kuma kun haɗa alaƙa da wane, to kai kana ga wannan ya ishe ka cin abinci a wani wurin. Ko ya isa wani wurin in kaje a buɗe ma ƙofa ko a buɗe maka gate a ce ka shiga ai tunda kai sirikin wane ne

Wani kuma addini ne. Za ka ga an cika ƙofar gida ana neman mace cewa ai addininta ne ya sanya ake zuwa nemanta. An ga tana da kamewa; musamman yanzu da samun masu addinin yake ƙaranci. Saboda haka wani sai ka ga cewa shi ya fi so ya auri mai addini, natsattsiya, saboda ya tabbatar hankalinsa a kwance ya ke. Tsoron Allah da tarbiyar ta da ilimin ta da wayewar ta ba zai sa ta je ta ci amanarsa ko ta dinga abubuwa na rashinn mutunci wanda wasu miji suke yi ba. Saboda haka abinda ke kawo su kenan.

To wannan ka ga kenan a wannan hadisin, Annabi yana gaya mana kenan abinda ke kai mutum neman aure ne. Ba wai cewa ya yi ka auri mai kuɗi, ka auri mai kyau, ka auri mai daraja ba. Kai mai zuwa neman aure ga abinda ke kai mutane neman auren. Sai ya ce don haka ka rabauta da mai addini.  Wato da za a samu mace ta haɗa waɗannan huɗun, to da sai ka ga duk ta haɗa abinda mutane suke so. A ce mai kuɗi ce, kyakyawa ce, ʻyar wane ce kuma tana da addini; kaga kowa zai so ta kenan. Saboda mai son kuɗi tana da shi, mai son kyau tana da shi, mai son nasaba tana da shi, mai son addini tana da shi. Kuma kaima in ka samu mai irin wannan ɗin za ka ɗauka don ga addinin ga kyaun ga kuɗin ga darajan. To amma yawanci basa haɗuwa. Wacce za ta haɗa huɗun nan ita kaɗai; zaka ga a cikin dubu kaɗan ne. To wata sai ka ga ga kyawun amma ba addini, wata kuma ga addinin amma ba kyawun. Wato shi kyau kada mutane su ji muna cewa amma ba kyawu. Kyawu a idon mai kallo ne. Domi abinda ka ke gani da kyau, ba dole wani ya zama yana ganin kyawunsa ba. Don haka babu wani abu da aka yi ittifaƙi a matsayin shine kyauʼ babu  shi. Babu kuma wata mace da ta haɗa kyau. Babu wata sarauniyar kyau. Duk faɗin duniyar nan ba wata sarauniyar kyau. Domin sarauniyar kyau sai dai sarauniyar kyau irin waɗanda suke shiga takarar, ai  an. Ai akwai matan aure, akwai masu mutuncin da ba za su je su sa ɗan kamfai su fito ba kuma sun fi waɗannan kyau. To ka ga a ce wannan ita ce sarauniyar kyau, alhalin dukkan mata na gida. Da  mata  waɗanda basu shiga gasar ba suna nan miliyoyi, waɗanda sun fi waɗanda suka shiga gasar kyau amma su ba sa shaʼawar suje su zubar da ƙimarsu ko mutuncin su ne. Ashe ka ga kenan ba za ayi hukunci da wata

mata a ce ta fi kowa kyau ba. Saboda haka sai ka ga in fara ce, to wani shi ba ya ganin kyawun fara, in baƙi ne, in siranta ce, in hanci ne dogo, wani ya fi son nananne, wani ya fi son ma mai faffaɗan hanci saboda ta fi shaƙar iska da yawa. Saboda haka babu wani abu da za a ce shine kyau wanda duk duniya ta yi ittifaƙi a kansa. Saboda haka abinda kake gani da kyau wani ba ya gani da kyau. Shi ya sa Allah Ya ce "tabarakallahu ahsanul khaliƙin".

Don haka duk abinda Allah Ya yi mai kyau ne. Sai dai kai kawai abinda kai kake gani da kyau, kai shine kyau a mahangar ka. Shima wancan shine kyau a mahangarsa. Duk da akwai abubuwan da za ka ga waɗanda suke la'akari da kyau ɗin suka haɗu a kan cewa idan mace tana da shi kyau ne. Amma kuma za ka ga wani abin ya tauye ta. Kamar yadda malam Ibn Kayyum ya rubuta a cikin littafinsa wanda ya kawo akan 'Raudatul muhibbin'. Ya kawo abubuwa masu tarin yawa wanda ya ce sai mace ta haɗa su sannan za a ce mata tana da kyau. Kuma yana ga kamar babu irin waɗannan matan ma sai a aljanna. Wannan shine abu na biyu.

Sannan abu na uku ta kasance mai tausayi mai kuma hali irin na mata. Wannan abun yana da muhimmanci. Abinda ake kira hali irin na mata, akwai macen da za ka ga mai kaushin hali ce; mai faɗa da rigima da son kwazozoto ce da hargowa da hayaniya. Saboda haka maganganun ta ma  da daɗin ji. Bata iya magana ba, ga tsiwa da son a yi faɗa. Irin su ne suke maida tsakar gida kamar kana tsakiyar kasuwa. To wannan ita ake kira mace mai hali ba irin na mata ba. Amma an fi son mace ta zamto mai taushin murya, taushin hali, tausayi, son yara, murmushi da kuma sakin fuska da haƙuri. Saboda haka shi yasa Manzon Allah (SAW) ya ce mafi alherin mata da suka hau raƙuma sune nagartattun matan ƙuraishawa. To me ya sa haka? Sai Annabi  (SAW) ya ce su suka fi ko wacce mace tausayawa yaro yana ƙarami. Kullum ɗan su yana hannunsu, ko yana goye, ko yana kan cinya ko yana rungume. Sai ya yi barci a kwantar da shi. Da ya farka a ɗauke shi a bashi nono, a yi masa wanka, sannan a je a gyara shi, a ci gaba da lura da shi. Saboda haka suna da tausayin yaro. Idan yaro ya taso zai samu kulawa ta uwarsa yadda ya kamata.

To ka ga mace mai irin wannan siffa ana son ta. Amma akwai wacce in ta wurgar da yaron ta shiga harkokin ta, yana kuka ma sai ta ce "ku ƙyale shi in ya gaji zai bari." Saboda haka yaro yai kashi har kashin ya bushe a jikinsa ba a zo a wanke masa ba. Yaro yana jin ƙishirwa ba a zo an bas hi ruwa ba. Yana jin yunwa ba a zo

an bashi nono ba. Yana kuka ba a rarrashe shi ba har zuciyarsa ma ta bushe yana ƙarami-ya ga cewa ashe duniyar nan da ya shigo ta marasa mutunci ce. Har shi da kansa ya fahimlci cewa kukan nan da ya ke ba mai tausaya masa, gara ma ya daina. Har ya fahimci cewa wace irin duniya ya shigo da ba a tausayawa mai yin kuka? Idan ya yibayan gida ba a wanke masa, ba a goya yaro ya ji ɗumin bayan uwarsa, ba a ɗorashi a kan cinya, a rungume shi a jiki ya ji ɗumin mahaifiyarsa. Kullum yana kan keken turawa, ko yana cikin nafkin, ko an ratayo wata jaka. Saboda ai kada yaro ya ɓata mata jiki sai a rataye shi. Nono ma tana ganin idan ta bawa yaro tsufa za ta yi da wuri, saboda haka sai ta nemo wata tana kula da shi. Har yanzu ma wai an fara zuwa ƙasashen waje. Wani ya ke gaya mini cewa yanzu an fara zuwa China ana ɗauko mai raino. Ya je wani gida ya tarar da wani ya ɗauko wata mata daga China ana bata N90,000, kawai abinda ta ke yi shine ta canzawa yaro nafkin, idan yana kuka ta rarrasheshi, in kuma ya buƙaci nono ta sanar da uwarsa;ita uwar tana can tana wasu harkokin ta. To shine ta ɗauko wata daga China ta dinga yi mata raino. To shima ɗin shawara aka bashi aka ce akwai masu raino a ƙasar China ana zuwa ana ɗauko su. Suna zuwa suna rainon yara saboda matanmu ba su da lokacin da za su raini 'ya'yanmu. To kaga wannan al'amari in ya tafi a haka, to za mu ga cewa wacce irin al'umma za mu samu nan gaba? To saboda haka ya ce mafi alherin matan da suka hau raƙuma sune nagartattun matan ƙuraishawa. Waɗanda su suka fi tausayawa yaro a lokacin da yake ƙarami. Wannan shi yake jawo shaƙuwa tsakaninn uwa da ɗa. Yaro ya taso ya ga yadda ake ta wahala da shi.

Sannan wannan shi ya ce "wa ar'ahu ala zaujin fi zati yadihi", ma'ana, tare da cewa tana kula da ɗanta bai hana kuma a kula da miji ba. Wanda yanzu daga cikin matsalar da muke fuskanta shine idan mace ta fara haihiuwa sai ta ɗauke hidimar da takewa mijinta da soyayya da kulawa da take yi masa sai ta mayar kan 'ya'yanta. Sai ka ga uba ya shigo ko kallonsa ba a yi ba, amma ga yara can ana ta kula da su, ana basu abinci. Shi miji tunda ya haifa, to ba ta shi take ba, yanzu 'ya'yanta take tunani. Cewa tunda shi uba akan hanyan lahira yake, dole ta kula da 'ya'yanta. To saboda haka sai ka ga to a'a, ni yanzu menene amfani na? ni yanzu bani da amfani kenan a gidannan sai dai in kawo tuwo a tuƙa? Bazan dawo a tareni ba, ba kuma za a yi mini sannu da zuwa ba? Yara ma an ba su lokaci na. Sai kishi ya shiga uban, cewa to tunda an yi watsi da ni bari in samo wata, itama ta zo ta kula da ni.

To ka ga wannan, matar da za ta iya haɗa kula da yara, sannan ta kula kuma da miji, to itama kuma kaɗan ake samunta. Matar da za ta bawa miji haƙƙinsa cikakke, yara ma ta basu su haƙƙinsu tana da wahalar samu. Kuma siffofi ne a hadisin Annabi Muhammadu (SAW), kamar yadda ya zo a hadisin Imamul Bukhari mai lamba ta 5082 da hadisin Muslim mai lamba ta 2527, Manzon Allah (SAW) ya ce to, mata mai kula da miji a bisa ma'abociyar hannun sa, sannan kuma mai tausayawa yaro yana ƙarami. Ta shaƙu da mijin ta ta shaƙu da ɗanta. Kuma wata ana samu in mijinta ya zo, in ta zo ta liƙe masa, ko yaron yana ta kuka sai a ce ku ƙyale ni ina waje mijina. To kaga wannan itama matsala ce. Haka kuma wacce za ta maƙalewa 'ya'ya tayi watsi da miji matsala ce. To samun wacce za ta iya, saboda abu ne ba na yau da gobe ba, ba me ƙarewa ba, shi ya sa sai an yiwa mace horo akan waɗannan abubuwan guida 2, in ba haka ba, daga ta fara haiuwa sai ka ji ba ka son ta. Saboda za ta koma kan 'ya'yanta kai tayi watsi da kai. Ko kuma tayi watsi da 'ya'yan ta dawo kanka. To duka biyun nan fa kuskure ne a cikin harkar aure a ce mace ba ta iya haɗa waɗannan abubuwa guda biyu ba. Wanda kuma sai an samu nagartacciya.

To akwai wata siffa da malamai suke cewa idan mutum zai yi aure ya duba duk da ita ba wai dole ne sai an sameta ba. Wannan siffa itace mutum ya auri budurwa, maimakon bazawara. Sun faɗi wannan ne saboda hadisin Jabir ɗan Abdullahi, Allah Ya ƙara masa yarda; ya ke cewa, "a lokacin da na yi aure sai Manzon Allahah (SAW) ya gamu da ni; ya ce me ka aura; budurwa ka aura ko bazawara? Ya ce "sai na cewa Manzon Allah bazawara na aura. Sai Manzon Allah ya ce "don me ba ka auri budurwa ba, wacce za ka yi wasa da ita, itama ta yi wasa da kai. Ka yi mata dariya, itama ta yi maka dariya? Domin itace kamar shekarun ta bai yi nisa da naka ba. Za ku zama kamar abokan juna."

Kasan kowanne in ya girmi kowanne to ana samun matsala idan nisan ya yi yawa. Yanzu idan mutum yana da shekara 60 ko 50, ya auro 'yar shekara 15 ko 18, to ita fa kaawai za ta riƙa yi masa kallon dattijo ne saboda wataƙila ma ya girmi babanta. Wataƙila tana zaune da shi ne saboda kunyar babanta, ko saboda kuɗinsa ko kuma ma saboba ba ta samu miji ba. Saboda haka ba za su samu dama irin ta masu ƙananan shekaru ba. Shima ba zai iya sakewa ba- ya zo tsofaitsofai da shi, dattijo da shi, ba zai iya saukowa daidai da ita ba. Shi yasa idan aka ce Annabi (SAW) ya auri mace me shekaru da yawa kuma ya auri mai shekaru kaɗan, shi

Annabi (SAW) ya fi kowa iya sanin zamantakewa ta muʼamalar aure. Yana sakkowa ne daidai da ƙaramar, babbar kuma in ya tashi sai ya hau kusa da ita. Saboda haka mu kuma ba haka mu ke yi ba. Bama koyi da Annabi Muhammadu (SAW) cikin wannan muʼamala. Saboda haka yanzu mutum zai kafa maka hujja cewa, ai Annabi (SAW) ya auri mace tana da ƙarancin shekaru. Sai mu ce hakane, amma yadda Annabi ya yiwa wacce ya aura mai ƙarancin shekaru kaima haka kayi mata? Shi Annabi (SAW) yakan sauko su yi wanka da matarsa, su yi tsere da matarsa, su yi abubuwa daban-daban. Idan yana karanta Al ƙurʼanin ma da cinyar ta yake tada kai. Ita take taje masa kai, ita take masa hidimomi iri-iri. Saboda haka ya sauko yadda zai faranta mata. Kuma har da doki da kayan wasanta na yara ta zo gidan- amma yanzu mutanenmu ba za su iya wannan ba. Ba za ka saki jiki ka sauko a ganka a tsakar gida ʻyaʼyan ka suna kallon ka kuna guje-guje da wacce shekarunta bai wuce ƙaramar ʻyarka ko jikarka ba.

Saboda haka sai kawai ta zauna dai kusan kullum  a tsorace take. Tana ganin kamar kakanta ne ko babanta ne ko wani nag aba da ita. Kawai dai don aure ya haɗa su. To wannan ya sa sai ka ga mutum shekarunsa sun tafi, lokacin da ita ta isa ta zama mace cikakkiya, shi kuma lokacin ƙarfinsa ya ƙare. To ka ga wannan ma matsala ce sosai. Domin lokacin da ƙarfin sa ya ƙare, ita kuma shekarunta sun kawo, tana buƙatar kulawa sosai. Shi kuma bashi da ƙarfin da zai iya kulawa da ita. Wanda da yawa muna samun koke daga mata waɗanda suka auri maza masu irin waɗannan shekarun. Shi ƙarfinsa ya ƙare, ita nata ya kawo. Wani ma ya kasa ma saduwa da ita saboda ba zai iya ba. Ita kuma yanzu take da buƙata sosai. Saboda haka sai ka ga idan ta ce a saketa sai a ga ta yi rashin mutunci. Idan ta zauna kuma ta cutu. Wata bata da tsoron Allah ma, sai ta kama zinace-zinace. To ka ga dole ne a riƙa kula da wannan.

Sannan hakanan idan mutum ya auri matar da ita kuma shekarun nata sun yi masa nisa- shima halal ne.  Duk waɗannan maganganu da muke faɗa guda 2 duka halal ne. To amma kuma in za a yi a lura da yanayin cewa idan mutum ya auri matar da shi kuma ta girmeshi da yawa, to da wuya shi kuma ya hau ya zama irin ta. Saboda haka sai ya riƙa ganin dama ta girme shi ko za ta yi masa wayo ko ta fishi hankali ko ta fishi basira da sauran su. Saboda haka ba zai iya hawa ya je ya tarar da ita ba. Itama ba za ta iya saukowa ta yi wasa da shi yadda ya kamata ba. To shi yasa wannan hadisi na Jabir, da Mannzon Allah (SAW) ya yi laʼakari da shekarunsa,

cewa shekarunsa basu yi nisa ba amma ya je kuma ya auro bazawar. Shi ya sa Manzo Allah ya ce masa don me ba ka auri budurwa ba?

To sai ya ce "ya rasulallah ina da dalilin da ya sa na bar budurwar na auri bazawara. Na farko, mahaifina ya rasu ya bar ni da ƙannena mata su 9, duk ƙanana kuma." tunda dama shine babban yayansu. Kuma a lokacin da ake wannan magana shima bai kai ashekara 20 ba. Yace "idan na auro wata daidai da su ko sa'arsu ka ga na aurowa kaina aiki, shi ya sa na yi tunanin auro mai hankali wacce za ta kula mini da waɗannan ƙanne nawa." To ka ga ashe hankali ne da basira da hangen nesa ya sa Jabir ya haƙura da auren budurwa, ya auri bazawara, domin ta taimaka masa wajen rainon ƙannensa. Da Manzon Allah ya ji haka sai ya ga ashe Jabir ya yi dogon tunani. Sai ya ce "to Allah ya yi maka albarka," wato ya yaba masa da wannan abu da ya yi na haƙura da buƙatarsa don maslahar ƙannensa.

To kenen ka ga auen bazawara shi dole sai in akwai wata maslaha. Maslahohi wanda ya shafe ka ko wanda ya shafe ta. Kamar a ce mai 'ya'ya ce wacce in ka aure ta kai kuma za ka kula da 'ya'yan. Ko wata mai addini ce wacce mijinta ya rasu; wacce a ke ganin za ta tozarta idan ba a aureta ba. Ko kuma a taimaka mata ta riƙe kanta, idan ba ta yi aure da wuri ba za ta shiga wata matsala. Ma'ana dai akwai wani abu da ka duba. Ko kana da 'ya'ya waɗanda mahaifiyar su ta rasu. Ko kana wani aiki na addini wanda in ta zo za ta taimaka maka ko aiki na rayuwa. Ko tana da wata ƙwarewa a wani fannin da kake buƙata, wanda idan ka aurota za ta ba ka gudunmawa a wannan fannin ta cike ma. Duk sai ka duba wannan dalilan; ai ka ga wacce za ka koya mata ba daidai take da wacce ta iya ba. Wacce za ta taimaka maka ba daidai take da wacce za ka taimakawa ba. Sabo da haka bisa waɗannan dalilai, mutum yana iya rinjayar da auren bazawara akan budurwa.

## Tambaya Kan Aure 13

Wanda muka ce waɗannan dalilai suke sawa aka fifita auren bazawara akan budurwa. Idan bazawarar tana da wani hali wanda ya riga ya shahara, kamar yadda Asma'u bint Umais ta yi aure wajen sau 4 a zamanin sahabbai. Wajen sahabbai 4 ta yiwa takaba. Mijinta na farko yayan Sayyidina Ali, shine Jafar bn Abi Talib, shi ta fara aura suka auri 'ya'ya sai Allah ya yi masa rasuwa a wajen yaƙi. Daga nan sai

ta auri Sayyidina Abubakar. bayan shima ya rasu, ta yi masa takaba, sai ta auri Sayyidina Ali. Shima da ya rasu, ta yi masa takaba, wanda ance daga ƙarshe ma dai, wani ya sake aurenta bayan sayyidina Ali. Kaga wajen aure 4 kenan ma a jere, kuma ka san duk wacce ta yi irn wannan ai an san ta yi shekaru kuma ta haihu da yawa. Kuma duk gidan da taje sai ta haihu. Ta haihu a wajen Jafar, ta haihu a wajen Sayyidina Abubakar, na ƙarshen ne ba mu ji labarin ko ta haihu a can ba. Sannan kuma a wajen rasuwar su, musamman wajen rasuwar Sayyidina Ali da wannan kusan shekara 30 ne ba kaɗan. Wanda wannan kenan ya nuna ta daɗe tana gogayyya kuma kowa yana sonta saboda an san imaninta da gogewarta da iliminta da basirarta wanda za ta iya taimaka musu, musamman su abinda yake gabansu lahira ne ba irin yanzu da duniyar ta yi tasiri da yawa akan mu ba.

To wannan ko kuma tausayi na cewa tana da ʻyaʼya marayu, ko tana da wani ilimi, wanda za ta taimakawa mutum a maytsayin sa na maʼaikacin gwamnati, ko ɗan siyasa ko malami da sauransu. Wanda za ta iya bashi wannan gudunmawar ta iliminta ko basirarta ko gogewarta ko basirarta. To wannan duka ya kan sa a rinjayar da auren bazawara akan budurwa. Amma idan ba haka ba, wanda zai yi aure abinda aka fi so, ya zama shi ya auri budurwa saboda shi zai ɗora a akan irin tunanin da yake so.

Muka ce amma a nan, duk wanda yake da shekaru mai yawa, ya je ya auri mai ƙarancin shekaru, to lallai ya tsaya ya yi lissafi mai zurfi. Ya san cewa shekarunta nawa shi kuma shekarunsa nawa. Sannan kuma in an yi auren, shi idan shekarunsa suka yi nisa, ita nata sun kawo ya zai iya biya mata buƙatunta na rayuwa da na saduwa da na muʼamala da zamantakewa. Saboda haka idan ya san ba zai iya wannan ba, to kada ya shiga ya kai ta lokacin da ba zai iya yi mata muʼamala ba, wanda hakan zai iya halaka ta, ko ya jawo tana ƙinsa, ko ma ta je ta kama yin zinace-zinace, wanda an sha samun irin wannan da yawa.

Sannan abu na gaba wanda ya kamata ayi laʼakari da shi shine, lallai mutum ya lura da macen da aka koya mata abubuwa guda 4 a gidansu.

1- Ya bincika ya gani gidan su suna da tsafta kuma an koya mata? Duk da ba sharaɗi bane sai mahaifiya tana da tsabta ʻyarta za ta yi tsafta. Amma dai mafi yawa idan an koya mata tsafta a gida takan ɗore a kai. Saboda haka lallai tsafta muhimmiya ce. Musamman tsafta ta ɓangarorin nan guda 4 ko 5.

Ya zama mace ce mai tsafta dangane da abin da ya shafi jikinta, ba ta zama da ƙazanta. Ana iya samun mace wacce take gashin kanta ma gwanin ƙazanta yake. Kamar ƙazanta daga sama take farawa ta dire ƙasa. Kazantar farko itace gashi, wanda Annabi (SAW) ya ce duk wanda ya bar gashi to ya girmama shi. Kamar yadda ya gayawa wani mutum mai tulin gashi. Don haka girmama gashi ga mata shine a riƙa wanke shi, ana taje shi, ana sa masa mai. A riƙa wanke shi da sabulu yadda ba zai tara datti har kan mutum ya haifar da ƙwarƙwata ba. Ba zai kuma yi ƙazwa ba, ba zai yi kora ba, ba kuma zai yi kirci da amosani ba. Tana kula da gashin kanta yadda kullun yana cikin ƙamshi da kyan gani. Ta kuma maida gashinta mai kyau yadda mijinta ma zai riƙa sha'awarsa. Idan mace ba ta kula da gashinta, to lallai za a samu ƙazanta wacce za ta haifar da abubuwan can da muka faɗa. Kullum mace kanta yana cikin susa; tana susa a hanya, a makaranta, ko a gaban miji, kaga ana ɗauko ƙwarƙwata ana sa yatsa ana kashe ta a ƙasa. Duk da yanzu Allah Ya taimake mu duniyar ƙwarƙwata ta ƙare. Yanzu iyalan ƙwarƙwata gaba ɗaya- da 'ya'yanta da jikokinta kusan an yi bankwana da su, indai ba wajen ƙazaman da ƙazantarsu ta zamo me yawan gaske ba.

Daga nan sai ido. Wato ƙazanntar ido, mace ta tashi da kwantsa. Akwai wanda ya ce shi abinda ya fi damunsa shine matar sa ta zo masa da kwantsa. Ko duba madubi ne ba ta yi? Allahu a'alamu. Idon ta zai yi kwantsa kuma ta zo gaban miji. Saboda haka wannan shima ƙazanta ne da ya kamata a ce mace ta kiyaye tsabtar idonta. Idan ma ta dinga ciwon ido ta riƙa sa ruwan zafi tana wanke su. Kuma abinda likitocin ido suka amince da shi, su bata shawarar irin abinda za ta riƙa yi wanda mijinta ba zai riƙa ganin ƙazanta a idonta ba. Domin za a ce akwai wani kwalli wanda ake sawa wanda garin magani ne ake niƙa shi. Wanda ƙarshe mace idonta ya riƙa neman ya yi rami, ko ya yi baƙi ko da tasa sai ka ga idon ya yi baƙi. Saboda tasirin wannan sinadarin cikin wannan kwallin da ta sa a idonta ya kashe idon ko ya lalata shi. Wata ma ƙarshe da gilas take ƙare rayuwarta saboda idon bashi da ƙarfi. Saboda haka a yi bincike a tambayi masana kafin a fara anfani da nau'i na kwalli da ake sawa a ido.

To daga nan sai ƙazantar hanci. Hanci ɗinnan da ake gani, shima fa ƙazami ne idan ba a kula da shi. Akwai tasono, majina, ƙura da kuma datti. Saboda haka wata za ka ga cewa hancinta ya cika da datti, kai kanka kana hango dattin. Ko ka ga hancin wata akwai tasono ko majina. Musamman wacce take mura dole ta kiyaye saboda

mijin ta kada ya rika ganin majinar. Ya zama kullum a jakarta akwai ƙyalle. Ko hira suke da mijinta, idan za ta fyace majina to ta tashi daga wajen. Amma ta zo tana ƙaƙaro majina, ko tana fyato majina a gaban miji ba abu bane mai kyau. Ko fyace majinar ma ai abune da bashi da kyawun gani . Duk wani sauti da duk wata murya, da duk wani abun da bashi da kyau ya kamata mace ta riƙa kiyayewa ba ta yi a gaban mijin ta. Domin idan tana yawan fyace majina, tana yawan kaki tana tofarwa a gaban mijinta, to hakan zai sa ya fara ƙin ta. Amma idan za ta yi, sai ta tashi, ta ce "ina zuwa," sai ta je can sai ta gama fyace-fyacen nata da sakace-sakacen, da ƙaƙare-ƙaƙaren ta, sai ta gama tsaf, sai ta dawo. Saboda haka shi bai ga abinda ya muzanta masa ba. To wannan shine tsafta ta 3, bayan tsaftar kai da ta hanci.

To uwa uba shine na huɗun, wato baki. Bakin nan dama kamar juji yake, ko kamar shadda yake. Shi ya na ɗaukar wari, yana samami, yana ɗoyi. Ba abinda baki ba ya yi. Dalili,  ta nan abinci ya ke shiga. Idan mutum zai ci abinci ci kowanne iri, wanda daga bisani ya koma kashi a ciki sannan a fitar da shi ta ba haya, to duk ta baki ya ke bi.  Gashi kuma murya tana fita, ga ƙura tana shiga, ga abubuwa daban-daban a cikin bakin nan. Ga harshe, ga haƙora. Baki yana da loko-loko kuma ya fi komai lunguna a jikin mutum. Tunda baki yana da waɗannan lokuna, ya kamata a riƙa kurkure shi, ana tsabtace shi. Kuma a riƙa sa magani ko asuwaki, ko makilin da buroshi. Ya dai zama cewa ana wanke baki kamar yadda muka gani a hadisin Annabi (SAW) cewa yana yawan yin asuwaki. Har ma malamai suka ce a hali 6 lallai mutum ya kiyaye asiwaki. Ko ba ka yin asiwaki ko da yaushe, to ka riƙa yin shi a hali 6.

1- Lokacin da mutum ya farka daga barci to ya zama abinda ya fara shine asiwaki.
2- Idan mutum zai kwanta barci ya zama lallai ya yi asiwaki.
3- Mutum ya yi asiwaki a lokacin da zai yi sallah.
4- Mutum ya yi asiwaki a lokacin da zai yi alwala.
5- Mutum ya zamo ya yi asiwaki a lokacin da ya ke tare da iyalansa; musamman lokacin da zai yi hira da su, ko zai yi magana da su.
6- Mutum ya zama ya yi asiwaki a lokacin da zai karanta Al ƙur'ani. Saboda Manzon Allah (SAW) ya ce "ku tsaftace bakunan ku domin ta nan ne

Alƙur'ani yake fita. Ka ga idan mutum bai tsaftace bakinsa ba yana karatun Kur'ani, bakinsa ɗin zai riƙa yin tsami da wari.

Saboda hakama za ka ga abinci ya daddanƙare a cikin baki; wanda hakan sai ka ga hoƙora sun yi ja maimakon farare. Ko ka ga haƙora sun yi shuɗi, ko sun yi kala-kala saboda abinci da yak e maƙalewa a jiki kuma ba a wankewa. To rashin tsaftar baki ga namiji ko mace ya kan haifar da kowa ya dinga kau da kai lokacin da suke Magana, ko suke kwance. Ka ga kan miji ya kalli kudu, na mata ya kalli arewa. Ba wanda ke so ya ga fuskar ɗan'uwansa saboda idan ta buɗe bakinta tsami, shima idan ya buɗe nasa tsami. Saboda haka tsaftace baki yana daga cikin tsafta da ake so idan mutum zai yi auri ya tabbatar da macen da zai aura tana da tsafta.

Sannan sai tsaftar hammata. Hammata loko ne da ke tara gashi da ƙazanta. Wanda wasu har sai ka ga suna da fararen kaya, amma saboda ƙazanta sai ka ga wurin ya dafe. Wata macen kuma sai ka ga inda akwai mai kitso ma da sai ta yi kitso a cikin hammatarta saboda gashin ya taru ya yi tsawo har ya fi na kanta. To wannan ƙazantane. Shari'a ba ta yarda da gashin hammata ba kuma ta yi umarni da a riƙa aske shi. Kuma a dinga sa abinda zai dusashe warin hammatar ta riƙa ƙamshi. Ko da yaushe mace ta ɗaga hammmatarta sai ka ga mutane na komawa baya. Wasu ma dalilin da ya sa ba a cin girkinsu kenan. Domin idan hammatar ta tara ruwa, dama idan an yi aiki za a yi gumi, to gumi ya ratsa ya gangaro ta kan kafaɗa ya shiga hammata ya tarar da hammata ta yi baƙiƙƙirin. Nan ma ya haɗu ya sake wankowa ana girki yana ɗiga cikin abinci. Kaga ai ƙazanta ta ƙare. Saboda za ka ga guminta yana ɗiga cikin abinci, musamman masu tuƙin tuwo ko masu aikin girki mai wahala. Dole ne a dinga aske hammata ko da sau ɗaya ne a sati. In ya yi nisa kada ya wuce kwana arba'in, kamar yadda ya zo a hadisin Abdullahi bn Mas'ud.

To sannan akwai tsafta da ta shafi gaba. Shima gaba yana da loko wanda ya haɗa da ɗuwawu da gabansa. Kuma da matematsi wanda shima gashi yana fitowa kuma yana tara datti. Idan ba a lura ba, sai a yi ta tara datti a cikin wurin, wanda shima yake da matsala har yana ma haddasa abun gaban ma ya samu matsala. Ko kuma mace ya zamo ta samu wasu ƙwayoyin cuta ma sun shige ta wanda daga nan ma sai kaga ta kamu da wata cutar a gabanta. Ko shima namiji ya kamu da cuta a gabansa. Ba kuma komai ya jawo wannan ba illa ƙazanta. Don haka akwai buƙatar

ya zamo ana aske gashin gaba, ko ana sa sindaraiu  masu ƙamshi, ko kuwa ana yawan lura da gurin cewa kullum a dinga wanke shi.

To sannan akwai cibiya. Cibiya itama musamman in ta shiga loko tana kawo datti da ƙazanta. Saboda haka akwai buƙatar a riƙa kula da cibiya. A riƙa tabbatar da cewa ba ta tara datti ko ƙazanta ba. To daga nan sai zuwa ƙasa dai, har zuwa ƙafa. Can ƙafa shima akwai dunduniyar ƙafa, akwai bayan ƙafa, wanda shima za ka ga ta yi faso da kaushi. Wata ƙafar duk ta goggoge, ta suɗe saboda bata kula da ƙafar da goge ta da lura da ita.

To haka dai ake so a riƙa yi. Ga wanka, ga sauran gyaran jiki da ba mu faɗa ba, duka idan mace ta bi su loko-loko tana kula da su. Saboda haka ana son mace dai mai tsafta .

Sannan na 2 ana son mace ta zama mai kwalliya. Kwalliyar nan tana da muhimmmaanci a wurin mata. Kwalliya aba ce da ke canjawa daga zamani zuwa zamani. Daga lokaci zuwa lokaci. Daga wuri zuwa wuri. Don haka duk kwalliyar da ta canja kema ki zama kina updating ɗin kanki. Kada ya zama cewa kwalliyar da ake yi tun zamanin da can har yanzu ita ki ke yi. Ta lura da yadda zamani ke tafiya. Don haka mijjinta aka yarda ta yiwa kwalliyar nan. Ba wai an ce ta yi kwalliya ta tafi yawo ba ne. Duk irin ɗinki da mata suke yayi, ko irin kwalliyar da ake yayi, wanda zai iya ɗaukewa mijinki hankali ki zama kina iya wannan. To mutum lallai ya zama cewa matar da zai auro ta iya kwalliya.

Sannan kuma ta iya girki, duk da iyaye mata a da suna ƙoƙari wurin koya wa ʻyaʼyansu girki. Amma gaskiya yanzu mutane suna kai ƙarar ʻyaʼyansu kan cewa zai yi cefane iya cefane, amma saboda ta tafi makaranta, lokacin da ake gama abinci, sai dai ta zo ta ci. Ba ta taya uwarta aiki a gida kuma gashi an mata aure ba ta koyi komai ba. Sai ta zo gida ta yi ta dafa abinci mara daɗi. Shi yasa wasu ma suke haƙura da abincin iyalan. Sai ka ga ya je ya gayyato wani ƙato shi ke yi masa abinci. Da yawa na sha zuwa gidajen mutane in taras masu girkinsu ma ba matansu bane, wasu ne aka ɗebosu suke musu girkin.

Wani ma abin takaici ƙabilar su da addinin su ba ɗaya bane da wanda ya ke musu girkin. Wannan abin takaici ne. Saboda haka ya kamata a ce mata sun iya girki sosai. Idan ma ba ta iya ba, to mutum ya tura ta koya. Ana buɗe makarantu yanzu, har cikin jamiʼoʼi. Ina ga akwai fannin koyon girki da ake yin digiri na ɗaya, a yi

na biyu har ma na uku ana yi. Ana Certificate da Diploma. Saboda haka akwai buƙatar a ce mace ta iya wannan, kuma mutum ya lura da wannan.

Sannann na 4 ya zama ta iya muʼammala. Muʼamalar nan tana da muhimmanci, domin ita ce zaman auren gaba ɗaya. Muʼamala da kai da ita. Muʼamala tsakaninta da ubangijin da ya halicce ta. Muʼamala tsakaninta da ʻyan uwanka da iyayenka. Wani za ka ga matar tana kyautata masa amma tana rigima da iyaye sa, ko iyayensa auna rigima da ita. Ko ʻyanʼuwansa ko maƙota suna rigima da ita, sai ka ga duk halin nan nata mai kyau da addininta amma ta samu cikas a rayuwar aure. Ko kuma a ce tana da abokiyar zama, kuma ba ta iya muʼammala da abokiyar auren ta ba. Ko kuma ta je ta tarar da yara, ita kuma ba a koya mata muʼamala da ɗan da ba nata ba. Ita kamar kaza take. Saboda haka kaga kenan idan ba ta iya muʼamala da ɗan wani ba, itama ba za a iya muʼamla da nata ba. Mai yiwuwa ta zo ta tarar mijin ta suna rigima da matarsa ta fita ta bar masa ʻyaʼya. Za ta je ta tarar da ʻyaʼya idan bata iya muʼamala da su ba akwai matsala. Ko ta mutu ta bar mata ʻyaʼya.  Ko mijin yana da wasu ʻyaʼya ko ya ɗauko wasu ʻyaʻya. Ko yana da ʻyan uwa. Ya zama kawai mijin take so ba ta son iyayensa, ba ta son ʻyan uwan sa ba ta son maƙotansa, ba ta son abokansa. To duk irin son da mijinta yake yi mata watarana sai ya lalace. Domin duk inda ya kai maganarta zai ji sukarta kawai akeyi. Tun ba ya yarda har sai ka ga a ƙarshe abin ya yi masa tasiri wanda wannan yakan taimaka wurin gurɓacewa da lalacewar aure.

Sannan ya zama mai haihuwa ce. Haihuwa dama tana daga cikin maƙasudin aure. Duk da akwai maganganu da wasu suke ganin mutum zai iya iyakance abinda zai haifa, ko kuwa kawai ya bari sai irin abinda Allh ya turo masa. An zo wani zamani yanzu da akwai ƙasashenn ma da sukayi doka kada ka Haifa musu ɗan da ya wuce biyu ko ɗaya. Wasu ƙasashen ma ɗaya. Da an haihu ɗaya, sai a je a yiwa ɗan rijista cewa, a je a toshe mahaifar matar ba za ta sake haihuwa ba. Saboda kamar suna ganin idan misali, suna da mata 100,000, ko wacce ta yi ciki ta haihu, to an ƙaru da mutumm 100,000. Sabooda haka idan su 1,000,000,000 ne; biliyan ɗaya kenan, misali a ce matan da mazan sun raba, a ce mazan ne su miliyan ɗari biyar ne (500,000,000), to idan duk suka yi ciki suka haihu a shekara 2 zuwa 3, to ka ga an samu ƙarin mutum miliyan ɗari biyar (500,000,000). Saboda haka sun doshi biliyan biyu (2,000,000,000).

To wannan wasu a tunanin su yana da matsala ta wajen tsaro, yana kuma da matsala ta ɓangaren tattalin arziƙi. Duk da mu a musulunce yawan mutane rahama ne, amma da sharaɗi guda 3:

1- Idan an koya musu ilimi.

2- Idan an koya musu tarbiya.

3- Idan an koya musu sana'a.

Idan an samu waɗannan ukun, to ba matsala komai yawansu. Amma idan babu sharuɗɗa ukun nan, to yawan al'umma matsala ne. Domin za a yita haifar maka matsala ne. Saboda haka sai ka tarar da mutane basu da aikin yi, basu da ilimi, basu da sana'a, suna zaune suna shan ƙwaya da ɗaukar makamai suna kashe mutane, suma ana kashe su. Ko kuma ka tarar da ana yawan rigingimu, ko ana fitintinu a cikin ƙasa. Ko yara sun ƙi zuwa makaranta suna zaman kashe wando, sun fara sace-sace da ɗauke- ɗauke a cikin unguwa. To ka ga wannan yawan bashi da amfani. Idan ka haifi irin wannan 'ya'yan ma Allah wadai mutum yake da su, ba ma wai a sa musu albarka ba. Saboda haka idan za a yi tarbiya, itace al'umma da Annabi zai yi alfahari da ita. Ya ce "ku yi aure ku hayayyafa. Zan yi alfahari da yawan ku, to yawan ai ba na yuyuyu bane. Don Annabi ma ba ya son yuyuyu. Abinda Annabi (SAW) ya ke so shine al'umma mai tarbiya, mai yawa, wacce za ta shiga aljanna, wacce za ta zamo mai amfani ga kanta, da ƙasar ta, da al'ummar ta.

To sannan mata ta zamo mai soyayya ce, wato an koya mata ƙa'idojin soyayya. Kada ya zamo mutum ya auro macen da bata iya so ba, ko ba ta sonsa. Da yawa mutane basa la'akari da so a wajen aure. Sai mutum ya ga cewa idan iyayen mace suka tursasa mata, zai iya aurenta, kuma yana ga tsawon lokaci zai sa ya shawo kanta. Akwai matar da take ce mana shekararsu talatin cur da mijinta, amma ba ta taɓa jin tana son shi ba ko misƙala zarratin. Babanta ne ya kira ta, ya ce wannan mutumin ki yarda ki aure shi. Ta ce "baba ba na son shi," ya ce "ki dai yi haƙuri kawai ki aure shi haka", to shine ta yi haƙuri ta aure shi. Shekara 30 ba ta taɓa jin ƙaunarsa ko misƙala zarratin a ran ta ba. Ba ta ƙara ɗauko maganar ba sai da mahaifin nata ya rasu, sannan ta ce to ta riga ta gama biyan haƙƙin baban. Ba ta yi abinda zai ɓata masa rai ba. Amma fa yanzu tana jin babu taƙi ɗaya da za ta iya yiwa wannan mutumin domin ta nuna tana son sa. Saboda haka ƙin ƙaruwa yake a duk tsawon shekarun nan.

To ka ga gaskiya shawarar da zan ba ma'aurata, kada su kuskura kunya ta sa su auri waɗanda bas a so.  ko biyayya ga iyaye ta sa a auri wand aba a so. Ko a aura masa matar da baya so. Su kuma muna ba iyaye shawara cewa, da can an yi aure babu so kuma an zauna lafiya, dalili ba wayewa irin ta zamanin yanzu. Yaran da basu yi primary ba, basu yi sakandare ba, wasu ma basu je jami'a ko su yi diploma ba. Lokacin babu kayan kallo, babu waya. Babu na'urorin da za ka ji BBC ko America, ka ji rediyon ƙasa, ka ji ta waje. Babu irin waɗannan abubuwa na internet- irin su Facebook da sauran abubuwa na sadarwa na zamani. Babu labarai da jaridu da mujallu. Yanzu an waye da karance-karancen litattafai waɗanda idan ma kai 'yarka ta yi haƙuri, to  za ka samu wani da zai zuga ta, ko ta karanta wani abu na wata da aka zuga,  itama sai ta ɗauki wannan zugar. Saboda haka mu dinga tarbiyantar da 'ya'yan mu a kan su so mutanen kirki. Ko mu yiwa mutumin kirki kamfe domin ya samu karɓuwa a wajen 'ya'yanmu. Idan mutumin kirki ya zo yace yana son 'yar ka ai ya baka aiki. Aikin shine yadda za ka je ka gina shi ka kuma sanyawa 'yar taka son shi a zuciyar ta. Amma ba wai ka ce mata "miji ya zo, ni na gamsu da shi." To kai da ka gamsu da shi, kai za ka zauna da shi? To ba ka ba 'yarka dama ta nuna gamsuwarta ko amincewar ta ba, to wannan auren gaskiya a daina yin sa. Auren da ba ya so ba ta so, ko tana so ba ya so, ko yana so ba ta so, duk kada a yi. Sai  dai a yi auren da duk su biyun suna so. Kuma sannan in an yi za a samu zaman lafiya da fahimtar juna. To irin wannan auren ne ya kamata iyaye su shige gaba, su kuma ƙarfafawa 'ya'yansu gwiwa akan su yi shi.

Tambaya Kan Aure 14

Kamar yadda bayani ya gabata dangane da irin siffofi da ya kamata mutum ya lura, da la'akari da su lokacin da ya ga wata yarinya yana so, kada ya yi gaggawa, kada ya yi sauri. Ya tsaya tukunna, ya bi a hankali sannan ya yi bincike, ya ga mafi yawa daga cikin siffofin da muka faɗa wannan yarinya ko wannan mata da zai aura ta haɗa su, domin a samu ingancin aure da daɗewarsa da ƙarkon sa da kuma ɗorewarsa har i zuwa mutuwa.

To da yawa malamai sukan tsaya a nan. Wasu ba sa faɗaɗa bayani dangane da itama mace irin siffofin da ya kamata ta lura da shi lokacin da mutum ya fito auren ta ko lokacin da ita ta ganshi tana son sa. To kada itama ta yi gaggawa ko ta yi

sauri. Ta lura cewa yana da wsu siffofi da ya kamata a ce mai irin waɗannan siffofi an aure shi.

1- Ya zama mai addini. Abinda ya sa ake sa addini a farko, domin addinin mutum, matuƙar yana aiki da shi yadda Allah ya saukar, da shi to za ka sameshi na kirki ne. Matuƙar mutum zai dinga yin addini yadda Allah yace. Aƙidarsa da ibadarsa da mu'amalarsa da zamantakewarsa sun zama yana kwaikwayon Manzon Allah (SAW), to za ka same shi ba zai zama mai cuta mai cutarwa ba. Saboda haka allah Ya ce .... "Bawa mumini shi ya fi alheri daga ɗa mushriki, ko da ko ya ƙayatar da ku" wato imani shi yake ɗaga darajar mutum, kuma saɓo da laifi da shirka su ke ƙaskƙantar da darajar mutum.

2- Ya zama yana da ilimi. Wato ilimi shi yake ba mutum dama ya dinga yin abubuwa bisa hujjoji da dalilai. Duk abinda zai yi, zai riƙa yin shi da ilimi. Ana so ya zama mai ilimi kuma mai aiki da ilimin. Saboda akwai wani mutum da ya zo, saboda darajar Al ƙur'anin da darajar ilimi, bashi da kuɗin da zai biya sadaki ya auri wata mata. Sai Manzon Allah (SAW) ya ce, "na aurar maka da wannan mata saboda abinda Allah ya azurta ka da shi na Al ƙur'ani," Kamar yadda ya zo a hadisin Bukhari mai lamba ta 5029 da hadisin Muslim mai lamba ta 1425. Ka ga wannan ya nuna kenan ilimi yana da daraja, kuma ya kamata a ce an auri mai ilimi.

3- Ya zamo cewa zai iya ɗaukar nauyin matar ta ɓangarori guda 2.

A- Yana da cikkiyar lafiya da zai iya gamsar da ita ta fuskar aure.

B- Ya zama zai iya ɗaukar nauye-nauyen auren. Kamar yadda Annabi (SAW) ya zaburar da matasa cewa, wanda ya samu dama, 'manista ɗa'a alaikumul ba'ata'. 'Ba'a', an fassarata ta hanyoyi guda 2. Na farko shine "al ƙudratu alal jima'a", wato ya zamo yana da iko, ko yana da dama da zai iya gamsar da matar ta ɓangaren saduwa. Sannan kuma na biyu shine "mu'unatuzzawaj", zai iya ɗaukar nauye-nauyen auren- ciyarwa, shayarwa da tufatarwa. Bayanin waɗannan zai zo a gaba, cewa idan mutum yaga cewa ba zai iya ɗaukar wannan nauyi ba, to ya shiga harkan auren ma bai kamata ba. Kamar yadda kuma za mu ga hadisin Faɗimatu bintu Kai; lokacin da mutane 2 suka fito neman aurenta. Manzon Allah

(SAW) ya ce mata, shi Mu'awiya da ya fito neman auren ki, to fa ki san talaka ne futuk, bashi da ko sisi. Saboda haka Annabi (SAW) yana nuna mata, mutumin da ba shi da sana'a ko bashi da hali bai kamata a aure shi ba, domin wata sabuwar rigima za a buɗe. Saboda haka, hadisin Muslim mai lamba ta 1480 da hadisin Nasa'i mai lamba ta 2245 da hadisin Abu Dauda mai lamaba ta 2284, Manzon Allah (SAW) ya nuna cewa, ba'a gaggawa wajen aure; a tsaya a yi bincike. A tabbatar da cewa mutum yana da sana'a, yana kuma da hali mai kyau sannan yana kula da addini.

4- Ya zama mai tausasawa mata. Ba a son auren mutum mai faɗa, ko rigima ko mai saurin kai duka, ko mari, ko mangari, ko naushi. Kamar yadda shima a hadisin Faɗimatu bintu Kais, Manzon Allah (SAW) ya ke gaya mata game da abinda ya shafi Abi Jahamin, ya ce"kada ki auri Abu Jahamin shima domin mutum ne da baya sauke sanda daga kan kafaɗa, wato mai yawan dukan mata ne." Ya shahara an sanshi a gari cewa in dai ya auri mace, in ta ɓata masa rai, za ta sha ɗan karen duka. Saboda haka Annabi (SAW) ya hana Faɗimatu bintu Kais ta aure shi. Ya ce "ki auri Usama". A nan idan mun lura, za mu ga cewa shi Usama ba ya cikin 'yan takarar da suka je neman auren ta, to amma, Annabi (SAW) ya san Usama yana neman aure don haka ya ce mata ta auri Usama. Idan muka lura, da Usama da babansa Zaidu, duk Manzon Allah (SAW) ne ya nema masu aure. Saboda shi Zaidu a gidan Manzon Allah (SAW) ya taso kuma ya haifi ɗan sa Usama. Sai ya zama Annabi (SAW) yana ƙaunar Zaidu da matarsa Ummu Aiman al Barkatu Habashiya da kuma ɗansu Usamatu bin Zaidin. Don haka ya ce a aure shi tare da cewa bai kai waɗancan ba ta ɓangaren asali, amma kuma ya fi su ta ɓangaren hali mai kyau. Don haka ya ce "wannan bashi da dukiya, wannan kuma mai yawan dukan mata ne, don haka ki auri Usama." Ita da farko har ta ɗan tagi haka. Tana ga kamar Usama ai bai kai ma ta yadda take buƙata ba, to amma da ta yi la'akari cewa Manzon Allah ne ya zaɓo mata, kuma ta san babu son rai ko son zuciya a cikin zaɓin sa, ta ce "sai na gamsu da wannan zaɓi na Annabi kuma sai Allah Ya sa albarka a cikin wannan aure. Na yi farin ciki, na ji daɗi, na yi murna da shi."

5- Ya zama wanda mace za ta aura mutum ne da idan ta ganshi ba za ta ji tana ƙyamar sa ba. Wani ana ƙyamar sa saboda siffar sa, wani ana ƙyamar sa sabo da halin sa, wani ana ƙyamar sa saboda ƙazantar sa. Za ka ga ana ta umartar mata su dinga wanka, suna kwalliya, suna tsafta, suna goge bakin su. Amma sai ka ga wasu mazajen in banda datti da wari da ɗoyi da annakiya ba abinda suke yi, kuma haka matan suke zama da su. Don haka mace ta yi la'akari da cewa bata auri irin mijin da idan ta hango shi ran ta zai ɓaci, ko za ta shiga cikin damuwa saboda bashi da kyawun hali, ko bashi da kyawun siffa, ko bashi da kamanni ba. Saboda haka wannan ma yana da kyau mace ta tabbatar cewa miji ya kwanta mata a rai, ta gamsu da yanayin sa na halitta ko yanayinsa na ɗabi'a ko yanayinsa na zamantakewar sa.

6- Ya zama ba wanda ba ya haihuwa bane, saboda an zaburar a cikin hadisi cewa a yi aure dan a hayayyafa, domin Annabi (SAW) zai yi alfahari da yawanmu ranar Al Kiyama; musamman yawa mai nagarta da ƙarko, ba wai yawan yuyuyu ba. Ko bahaushe ma ai cewa ya ke yi, da yuyuyu gara ka samu ɗa ɗaya ƙwaƙƙwara. Ya fiye maka ka tara 'ya'ya, ko ka tara zuriya waɗanda ba su da alheri. Saboda haka a yi la'akari da wannan. Annabi (SAW) ya gaya mana ma game da mata, cewa ku auri matan da suke ƙaunar ku kuma masu haihuwa.

Ya za a yi a gane wannan matar za ta haihu ko wannan namijin yana haihuwa? Wani ya yi auren ya daɗe bai haihu ba, kuma idan ya saki mace ta je wani gidan sai ta haihu, ka ga ya nuna matsalar daga gareshi ne kenan. Wata kuma za ka ga cewa danginta ba sa haihuwa sosai, wato ba irin haihuwa bace. Amma wata idan aka yi la'akari da babarta, da ƙanwar baba ta da yar babarta wacce suke uwa ɗaya ko uba ɗaya ko uwaɗaya uba ɗaya da babarta, ko ƙannenta da yayyenta da aka aurar za a ga suna ta haihuwa. To mafi yawa ba wai dole bane idan aka aure ta sai ka ga Allah itama ya bata irin wannan. Iri ne na haihuwa da za ta haifi 'ya'ya. Kuma wani wurin za ka ga suna da himma da ƙwazo wurin kula da tarbiyar yaro. Saboda haka irin waɗannan su ake aure, waɗanda aka koya musu tarbiyar kula da yara.

7- Ya zamo kufu'i ne na matar, wato suna daidai ta ɓangarori daban-daban. Abinda malamai suke kira kufu'i shine a samu daidaituwa taɓangaren cewa macen ba ta yiwa na mijin nisa da yawa ba, na mijin ma bai yiwa macen nisa da yawa ba. Domin in an yiwa juna nisa a shekaru ko a ilimi ko a fahimta ko a kuɗi ko a daraja, gara ma in namijin ne in ya fi matar kuɗi da yawa, to akwai sauƙi. Amma idan ta fishi wadata, ta fishi kyau, ta fishi asali, idan ba sa'a ya ci ba, wannan abu sai ya sa ta ƙi yi masa biyayya yadda ya kamata. Saboda haka ake so mutum idan zai yi aure ya dinga neman daidai ajinsa. Ya dinga neman daidai da shi, ya dinga neman wacce ba za ta raina shi ko ta walaƙanta shi ba. Hakanan mace itama ta dinga neman daidai da ita, kowa ya daina neman abinda ya san ba ajinsa bane, ko ba layinsa bane, ko ba irinsa bane.

Kafa'a ɗinnan malamai sun kasa ta kash 6. Suka ce akwai kafa'a a cikin addini, wato kufu'in mace ya zama cewa addinin su ɗaya kuma ƙarfin addinin su ɗaya. Saboda haka idan mace za ta yi aure, kada ta auri mutum mai sakaci da riƙon adddini. Da yawa za ka ga mata suna yin aure sai su ce daga baya sun fahimcin mijin yana shan giya ko kayan maye, ko baya kula da sallah, ko yana sakaci da addini. Sai daga baya kuma an zo an haifi 'ya'ya a gano haka. A rabu da shi kuma a shiga wata rigimar, a kuma zauna da shi kuma ba ya kula da addini. Saboda haka rashin kula da addini a cikin gida yana tasiri a kan yara, domin sun ga baban su ba ya tashi ya yi sallah, ba ya tashin iyalansa su yi sallah, b bayan Allah ya ce 'wamr ahalaka bi salati'......

Alllah Ya ce ka umarci ahalin ka, wanda suka haɗa matanka da 'ya'yanka da duk wanda yake ƙarƙashinka da yin sallah da kuma juriya wajen kula da sallah akan lokaci, da cika sharuɗɗanta da dokokin ta. Allah Ya ce ba mu tambaye ka wani albashi, ko wani arziƙi, ko wani abu da za ka riƙa bawa Allah duk wata, ko duk mako saboda ni'imar da Ya yi maka ba. Allah Ya ce "nahnu nar zuƙuka", "Mune muke maka arziƙi muke wadata ka", "walaƙibatu littaƙwa", "ƙarshe can ake gudu domin na masu tsoron Allah ne." Idan mutum ya rayu yadda ya ke so to ba zai ga abinda yake so ba. Saboda haka addini shine abu na farko da za a lura da shi. Kuma mutum ya zamo ba fasiƙi bane wanda ya ke aikata kaba'ira manya-manya har ya shahara, to kada ka shigar da 'yarka wurinsa, kada kuma a bashi aure irin wannan.

Sannan akwai kafa'a a cikin nasaba. Duk da yake malamai da yawa suna ganin, ya kamata a yi la'akari da ita cewa ya zama shima sharifun nasabu ne, wato nasabar sa shima maɗaukakiya ce kamar yaddaitama matar ta zama irin wannan . Duk da Imam Malik yana ga wannan ba dalili bane, in dai akwai addini shi kenan.

Sannan akwai kafa'a a cikin kuɗi. Ya zama cewa mutum ne wanda yake da halin da zai iya riƙe matar, irin ta. Don wata matar ta saba da wani yanayi. Idan mutum ya auro ta ya sauko da ita ƙasa daga yanayin da ta saba, to sai auren ya ƙi yin ƙarko. Saboda haka idan ka san za ka auro 'yar masu wadata ko 'yar masu kuɗi, to ka tabbatar cewa lallai kaima kana da hali daidai gwargwado. Ko da ita ce ta yarda, to dai ka yi mata bayanin yanayi ka domin kada ta zo daga baya ta ga abin da take ci da abin da take ɗaurawa da inda ta ke kwana ya yi ƙasa da yadda ta saba a gidan su, to ka ga akwai matsala. Ko dai ya zama sama da abinda ta saba a gidansu, ko daidai da shi. Amma idan aka yi ƙasa, da yawa akan samu matsala.

Sannan akwai kafa'a cikin hurriya. Wato dukkansu su zama 'ya'ya. Ba a son ɗaya ya zama bawa ɗaya ɗa. Wannan dama an wuce ta yanzu saboda zamani. Ba maganar bayi yanzu sosai a duniya.

Sannan ya zama kuma akwai kafa'a cikin ilimi da kuma sana'a. Idan mutum, misali yana da kwalin sakandare, sai ya auro mai kwalin digiri biyu ko digiri uku ko digiri ɗaya. Ta fi shi iya turanci, ta fi shi ilimi. To in ba sa'a ya yi ba, sai a samu matsala. Domin wayewar kanta da zurfin iliminta za t riƙa fahimtar wasu abubuwa akasin yadda mijinta ke fahimta. Idan namiji ya auri mace mara ilimi da sauƙi, sai ya koya mata; shine samanta dama. Amma idan macen ce mai ilimin,miji bashi da ilimi akan samu matsala da yawa. Domin za ta yi ta kawo abubuwa a ilmance, sai ya ga shi kuma ba haka ya kamata a yi ba. Saboda haka malamai suka ce a yi la'akari da wannan.

Sannan ya zama ya kuɓuta daga dukkan aibubbbuka, wanda za mu yi bayanin su a gaba. Ba shi da wata tawaya. Musamman tawayar da zai iya sa mata. Akwai tawaya ta zahiri wacce dama ana ganin ta. Kamar a ce makaho ne, kaga ta san wa ta aura. Kamar a ce gurgu ne,ta san wa ta aura, a ce bebe ne, ta san wa ta aura, duk waɗannan abubuwa ne na fili. Ko a ce yana ɗingishi, ka ga ta san wa ta aura. Ko a ce baƙi ne ita fara. Ko a ce mai kauri ne ita siririya. Ko a ce shi gajere ne ita doguwa. Duk wannan siffa ce da ba a ɓoye take ba za a iya ganin ta a fili. Amma

akwai aibubbuka na ɓoye wanda wasu za a iya fahimtar su, kuma dole a yi bayanin su. Domin kada a zo sai an yi aure, musamman abinda zai tauye juna game da haƙƙin saduwa ta aure. Duk wata cuta da ta shafi yanayin na miji to wajibi ne a yiwa mace bayani. Haka kuma duk wata cuta da ta shafi mace, dole a yiwa namiji bayani. Domin kada sai bayan auren, ya ga wannan cutar ko wannan rashin lafiyar kuma auren ya zo ya samu cikas ko a samu matsala. Don haka wannan za mu yi bayanin kasha-kashe da nau'ukan cutukka wanda aka fi samun namiji da su da kuma nau'in cutukka da aka fi samun mace da ita.Wanda kuma sukan yi tasiri wajen lalacewar aure idan ba a yi la'akari da su ba. Don haka malamai sun sharɗanta wannan ya zama an yi la'akari da shi.

To duk da cewa ba laifi idan mutum Allah ya bashi wata daraja ta ilimi ko ta karatu. Ko ya bashi wata daraja ta muƙami ko ta wata dama. Zai iya uren ko wace mace da irin wannan damar. Kamar yadda muka gani a hadisi na Zainab bintu Jahash, wacce ita tana ga ita baƙuraishiya ce, tana cikin manyan ƙuraishawa masu nasaba mai girma, amma Annabi (SAW) ya laurar da ita ga Zaidu bn Harisa. Wanda shi a wannan lokacin bararre ne kamar yadda Allah ya faɗa, kuma daga baya dai auren bai tafi yadda ya kamata ba. Kuma Allah Ya gayawa Annabi (SAW) cewa "wannan aure ba zai ɗore ba, kuma za su rabu, kuma ƙarshe kaine za ka aure ta." To a lokacin ya shahara ana kiran Zaidu ɗan Muhammadu (SAW), saboda Annabi ne ya riƙe shi. A hannunsa ne ya girma.To wannan ne ya sa abin ya yiwa Annabi (SAW) nauyi saboda jama'a za su yi ta faɗa a gari cewa ai ma matar da ya aura ma ta ɗan riƙonsa ne. Saboda haka Allah kuma so ya ke ya kashe wannan al'ada ta idan ka riƙe ɗa, ya girma a hannu ka, sai ku ɗau alƙawari da shi, shi ya koma ɗanka kai ka koma mahaifinsa. Ko ka koma babansa. To Allah ta'ala y ace ....

"Ku kira su da sunan iyayen su shine ya fi adalci ya fi dacewa a wajen Allah." To sannan kuma Annabi (SAW) ya aurar da 'ya'yansa guda 2 mata ga Usmanu ɗan Affan. Wanda kuma wannan aure shima kamar yadda Annabi (SAW) ya faɗa, haƙiƙa Allah ya zaɓi Kinanata daga 'ya'yan Annabi Isma'il, sannan ya zaɓi Kuraishawa daga 'ya'yan Kinana, sannan ya zaɓi Bani Hashim daga Kuraishawa, ni kuma ya zaɓe ni daga cikin Banu Hashim. Ka ga kenan ƙololuwar nasaba ta ƙarshe ita ce nasabar Annabi (SAW). Ta fi ko wacce nasaba daraja da girma. Kaga kenan duk wanda zai auri 'yar Annabi dole ya zama ƙasa da wannan abin. Ka ga

ʻyar Annabin ta fi shi daraja kenan. To amma duk da haka kuma dole ta yi aure. Ashe kenan mutum don ya je wani gida da ake ganin yana sama da shi, ba laifi bane ya je ya yi aure a gidan. Kamar yadda sahabbai suka yi aure a gidan Annabi (SAW). Kamar yadda Annabi ya yi aure a gidan sahabbai. Ka ga shi ya yi musu nisa, nesa ba kusa ba. Saboda haka idan Annnabi ya auri mace, to darajar matar ta ƙaru. Ita matar da Annabi ya aura ita ce ta samu daraja. Saboda ta auri mai daraja; sai darajarta ta ƙaru. Hakanan kuma idan mutum ya auri ʻyar Annabi (SAW), shi ma ta wannan ɓangaren ya ƙara daraja saboda ya auri ʻyar mai daraja kuma mai daraja (SAW).

To hakanan Annabi (SAW) ya shige gaba wajen auren Usmatu ɗan Zaidu da shi da Faɗimatu bintu Kais. Wanda Faɗimatu bintu Kaisu baƙuraishiya ce. Kuma shi Usama, da mahaifin sa da mahaifiyarsa bayi ne da aka ʻyanta su. Saboda haka Annabi ya ce ki auri Usama kamar yadda ya zo a hadisin Musulim. Hakanan Hadisin Abu malikin Ashʼari yake cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce abubuwa guda 4 suna daga cikin alʼadu na zamanin jahiliiya, amma har yau mutane basu daina yin su ba.

1- Alfahari da ni ɗan wane ne. Har yanzu ana yin wannan- mutum ya daki ƙirji ya ce nine wane ɗan wane. Mune masu daraja, sauran mutane ba su da daraja. Har yanzu ana wannan. Ita kuma darajar ba wani abun kirki yayi ba don Allah Ya ce ....

“Mafi darajar ku a wurin Allah shine wanda ya fi ku jin tsoron Allah.

2- Suka ce a cikin nasaba. Mutum ya fara rigima da wani yana zagin iyayensa da asalinsa da tushensa.Yana ɓata nasabar wasu, shima wannan alʼadace ta jahiliya. Wanda maroƙa suke yi, su ci mutuncin wani don su ɗaga darajar wani.

3- Sannan neman shan ruwa ta hanyar taurari. A ce idan tauraro kaza ya fito za a yi ruwa, idan tauraro kaza bai fito ba ba za a yi ruwa ba. Wannan alʼada ce ta zamanin jahiliyya, wanda kuma har yau ana aMfani da ita.

4- Daga cikin mugayen alʼadun zamanin jahiliya shine kururuwa da ihu da gunji lokacin da aka samu rasuwa ko aka samu mutuwa. Maimakon a ce

'inna lillahi wa inna ilaihi raji'un', a yi addu'a, a yi hawaye, wani wurin ma sai ka ga abun ya zama kamar biki. In hakan ya faru ana biki.

Wannan sune abubuwan da ya kamata a ce an kiyaye dangane da mutumin da ya fito neman aure. A lura da waɗannan halaye kamar yadda Annabi (SAW) ya faɗa cewa...

Idan mutum ya fito neman aure kuka yarda da addininsa da nasabar sa, ka ga ku ake buƙatar ku yarda cewa mutumin nan yana kula da addini. Sannan ku yarda cewa mutumin nan yana kula da halaye. Da can idan ka fito neman aure ba za a baka aure ba sai an je an yi bincike akan mutum ta ɓangare guda 3.

1- Sai an binciki asalinsa an gano daga ina ya ke. Saboda an sha samun mutane su zo daga wani guri mai nisa ba a san su ba, su zo su sa wasu mutane da ba a sansu ba su yi musu wakilci a ɗaura aure. In matsala ta faru sun gudu, a zo a bar mace da 'ya'ya cikin wahala ba su san dangin babansu ba. Uban ya gudu an neme shi an rasa. Ko ba a san danginsa da 'yan'uwansa ba, to ka ga wannan rigimar ya kamata a riƙa kula.
2- A riƙa bicikar addinin mutum. Lallai a tabbatar mutum mai kula ne da addini. Kuma halinsa yana da kyau.
3- A riƙa bincike akan sana'ar mutum. Wacce irin sana'a yake yi da zai riƙe wannan mata.

Idan ba a bincike akan waɗannan abubuwa guda 3 to za a yi ta samun matsala kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya faɗa.

Cewa "idan ba kwa yin bincike a kan addinin mutum da asalin sa da sana'ar sa, to lallai za a samu ɓarna mai yawa a bayan ƙasa." Ɓarnar da za a riƙa samu itace, za a zo a yi ta yin aure ba bincike. A zo a haifi 'ya'ya ba a samu masu kula wa ba. Kuma 'ya'yan nan dole su fito waje su watsu cikin jama'a. Kowa ya je ya kama wata sana'ar da bata dace ba. Wani ya zama ɗan fashi da makami, wani ɗan ƙwaya, wani ya ɗauki bindiga yana kashe mutane, gashi nan iri-iri dai kullum sai ana ta ƙarowa al'umma bala'i. Sai ya zama haihuwan da a ke yi amfanintaa bashi da yawa. Domin 'ya'yan da ake haifa ba sa samun tarbiya, ba sa samun ilimi, ba sa samun kulawa. Saboda haka kullum sai ka ga ana ƙaro rigingimu ne a cikin al'umma.Kullum ana ta kashe juna. Ka ga an haifi yaro, shi da aka haifa bai amfana da haihuwarsa da akayi ba.Waɗanda suka haife shi ba su amfana da sun

haife shi ba. Alʼummar da aka haifowa ba ta amfana da cewa ɗannan da aka haifa ya zame mata alheri ba.

Don haka waɗannan abubuwa wajibi ne a riƙa laʼakari da su ana bincika su. Rashin sanaʼa matsala ne ga wanda zai yi aure. Domin in baka da sanaʼa ta ƙaƙa za ka iya ciyar da matar? Ta ƙaƙa za ka iya ɗaukar nauyin maganin ta, ƙaƙa za ka iya ɗaukar nauyin tufafin ta da cinta da shanta da suturar a da wurin kwannanta? Saboda ma rigima yanzu sai ka ga an yi auren da mutum ma bashi da halin da zai iya biyan sadaƙin matar. Ko bashi da halin da zai iya kama gidan hayan da zai iya ajiye matar. Ko za ta haihu ya tafi roƙon na ragon suna da zai yiwa matar. Kaga duk wannan matsala ce. Ya kamata mutum ya kama sanaʼa a matakin farko ma tukunna kafin ma ya shiga neman aure. Hakanan wajibi a bincika a san asalin mutum da nasabar sa da danginsa kafin a bashi aure. Hakanan ya kamata a duba riƙo da addinin mutum in ana son aure ya yi nagarta, ana so ya ɗore kuma ana so a ci albarkarsa.

## TAMBAYA KAN AURE 15

Amma idan matar ka irin matar Abdullahi ɗan Masʼud ce, wanda shi an san alaramma ne, matarsa kuma tana da wadata saboda tana yin sanaʼoʼi. Da Annabi (SAW) ya yi waʼazi a kan cewa a dinga yin sadaƙa ana yin kyauta, sai ta je ta samu manzon Allah (SAW), ta ce "ya Rasulallah ka yi umarni yau da a yi sadaƙa, kuma ni ina da gwalagwalai kuma ina son na yi sadaƙa da wasu daga ciki, to amma Abdullahi ɗan Masʼud yana rayawa cewa da shi da ʻyaʼyansa suka fi cancantar na bawa wannan abin." Sai Manzon Allah (SAW) ya ce, "Abdullahi ɗan Masʼud ya yi gaskiya. Miji ki da ʻyaʼyanki sune mafi cancantar waɗanda za ki yiwa sadaƙa. Maʼana idan kina da wadata, kina da hali, wanda ya fi kamata a ce ya ci moriyar halin ki da wadatar ki sune mijin ki da ʻyaʼyan ki. Don haka Annabi (SAW) ya tabbatar mata cewa duk da tana da wadata, idan ta tashi yin alheri ta yiwa mijinta da ʻyaʼyanta. Domin ba wajibi ne ta ci da mijin ta ba, ba wajibi ne ta ci da ʻyaʼyanta ba. Idan ta yi musu abin kirki wannan abin zai fi da a ce an kaishi waje.

Hakanan za muga cewa akwai shi kuma wani mutum wanda shi sana'arsa yin ƙaho ne. Sana'ar yin ƙaho a zamanin jahiliyya ta fi ko wace sana'a ƙasƙanci. Idan mutun ya shiga wannan sana'a, idan bas sa'a ya ci ba, sai mutum ya mutu bai samu aure ba, idan bai riga ya yi auren ba. Saboda haka ne Annabi (SAW) da ya ga wani sahabi sana'arsa kenan kuma mutumin kirki ne, sai Annabi (SAW) ya gayawa mutane cewa su aura daga gare shi kuma su aura masa. Ma'ana idan yana da 'ya a aura, sannan kuma idan yazo neman aure a bashi. Kamar yadda ya zo a cikin wani hadisi na Sunan abi Dauda mai lamba ta 2202, Imam Hakim ya ruwaito shi da imamul Baihaƙi. Wannan hadisi yana nuna kenan sana'arka ba za ta hana a baka aure ba matuƙar kana kula da addini a sana'r. Lokacin da muka taso da muna yara, mun ji ana cewa irin masu sana'ar mahauta; sai a ce ba a auren mahauta ko ba a aurar musu saboda za su tashi ranar Al ƙiyama suna haushin kare. To wannan ba gaskiya bane. Mahauta kamar kowa da kowa suke. Sana'a ce kawai ta a yanka rago a feɗe a daddatsa ƙashin a sayar da naman, ba wani abu bane sabo. A cikin sahabbai ma akwai masu irin wannan sana'ar.

Don haka ba daidai bane a ware wani mai sana'a ana suka wannan sna'a tasa ko kuma ana sukarsa. Haka nan kuma za ka ga a wasu yankunan ba a bawa ladani aure, wai saboda ana ganin cewa ladanai ba masu arziƙi, har ma ana ganin cewa idan kana ladanci to taluci zai same ka. To kuma bah aka bane, camfi ne. Su ladanai masu daraja ne a addinin musulunci. Manzon Allah (SAW) ya faɗi wasu adadin shekaru da idan mutum ya yi yana kiran sallah ranar Al ƙiyama zai tsira kuma za a yi masa kujera, a yi masa dogon wuya da zai riƙa hango abinda ake yi a ranar Al ƙiyama. To ma kiran sallah, menene a cikinsa? Kalmar shahada ce yake ta maimaitawa. Yaya mutumin da yake ta maimaita kalmar shahada a ce kuma ƙarshe wai shine ƙasƙantacce a cikin al'umma? Bayan ya fi kowa ma lada. Za a jio ykiran sallar sa kuma a amsa masa, kuma shima ya samu lada. Saboda haka wannan ba daidai bane.

Haka nan kuma za ka ga an ware wani irin yanayi a ce ba za ayi aure a irin wannan yanayi ba, ko lokaci, wani guri saboda wani dalili. Wannan camfe-camfen shima yana nan. Sai ka ji ana cewa mace mai farar ƙafa ce, ko mai baƙar ƙafa ce. Ko idan an aure ta a wata rana, ko a wani wata, ko lokaci to auren ba zai yi albarka ba. Ko idan iyayenta suna kaza ba zai yi albarka ba, duk wannan camfe-camfen ba a son mutum ya sa su a cikin aure. Kamar yanzu wani ya auri mace, da ba shi da hali, sai

Allah ya bashi hali bayan ya yi auren. Shikenan sai a camfa wannan mata cewa ai tunda ya aureta arziƙinsa ya buɗe. Wato itace arziƙinsa kenan, shi yasa ake kiranta matar arziƙi. Sai ka ga an riƙe ta duk tsiyar da take yi saboda an camfa ta cewa idan mutum ya saketa zai talauce, mai farin ƙashi ce. Wata kuma idan mutum yana cikin wadata, yana cikin hali, bayan ya yi aure, sai Allah Ta'ala ya jarabce shi da rashi, to da danginsa, da 'yan'uwansa, idan ba masu tarbiya da imani bane, sai su riƙa gani wannan mata ita ta jawowa ɗan nasu ko ɗan uwansu musiba. Tunda ya aure ta abubuwansa suke yin ƙasa, don haka wannan ba matar arziƙi bace. Sai ka ga ana ta ƙoƙarin lalata auren. Ko a ware wani wata, musamman watan Safar; wasu kan camfa shi cewa ba a neman aure a ciki kuma ba a yin aure a ciki. Wanda ya yi aure a ciki ba zai ga arziƙi ba. Ko a ware wata rana a ce ba a yin aure a cikinta. Ko wata mace mai wata siffa, ko wani suna, a je a samu masu ilimin hisabi, su ce ai idan sunan ka ya zo iri kaza da sunan ta, an samu kaza da kaza, to wannan abun zai sa ba za ka yi arziƙi ba ko ba za ta yi arziƙi ba. Ko ba za ku samu 'ya'ya masu lafiya ba. Ko ba za ku samu 'ya'ya masu albarka ba. Ko kuma auren ba zai ɗore ba. Ko ba za a samu kyakyawan mafita a cikin auren ba. Duk waɗannan maganganu da kake ji dukkan su shiririta ne. ba su da asali, ba su da tushe a cikin addinin musulunci. Idan mutum ya ga mace ta cika sharuɗɗan da Allah ya faɗa da Manzon sa a cikin Al ƙur'ani da hadisai, kuma siffofinta sun yi an samu soyayya da gamsuwa da juna ta ɓangaren abinda ya shafi halaye da ɗabi'a da duk waɗannan abubuwa da muke ta bayani, to wannan babu laifi su yi aure.

Kamar yadda muka duba a hadisin Barira, soyayya tana da muhimmanci kuma tushe ce a wajen, aure, don haka ne kullum muke shawartar iyaye cewa lallai su daina aurar da 'ya'yansu sai ga waɗanda suke so. Su mazan suna so suma matan suna so, suma iyayen suna so. Domin kaima uba dole ka sa naka sharaɗin. Wasu yaran ba hankali garesu ba, sai su je su zaɓo maka wani yaro da kai ba ka gamsu da halayensa ba. Amma ita da yake ba hankali gare ta ba, sai ta je ta ɗauko wani wanda kuma ba na kirki bane. Wanda idan an biyewa abinda zuciyarta take so, za a zo a yi nadama a ƙarshe. Sai ka yai mata bayani, "idan kin sami mutumin kirki, tunda wannan da na samo miki na kirki ne, amma ba kya son sa, to ba dole in tilasta miki ki so shi ba, amma ki samo min na kirki wanda na yarda da shi. Yadda na ba ki dama ki so shi, nima ki ban dama in so shi. Saboda haka ki zaɓo mai kirki. Idan na kirki ya fito da kika ga kina son sa to nima ina son sa." Amma wasu kuma sai ka ga 'ya'yan ke kawo na kirki iyayen kuma suna la'akari da me aka basu.

Don akwai wata yarinya da take nuna cewa babanta ya kawo mata wani mutum ita kuma ba ta son wannan mutumin. Ashe kuɗi yake ta bawa baban. Ta kawo wani kuma mai addini, wanda babu wani abun suka, ta ce baba idan akwai abinda kake suka game da wannan mutumin a bashi haƙuri ya tafi. Amma nima a gaya mini don zuciyata ta kwanta cewa dalili kaza ne ya sa ba za a aurar da ni gareshi ba. Saboda haka uban bai samu dalili ba face dai ya karɓi kuɗin wani. Kaga wannan ba daidai bane har ʻyar ka ta fi ka hankali da bincike da sanin ya kamata. Don haka a dinga shawartar yara. Ba ma son a dinga yin aure kullum ana samun matsala. Allah shi ke haɗa soyayya a tsakanin zuƙatan mutane. Don haka in ba a samu soyayya ba, aure ba zai yi nagarta ba. Haka shima mijin bai kamata a tilasta shi ya auri macen da ba ya so ba. Kamar itama macen bai kamata a tilastata ta auri mijin da ba ta so ba. Dole a yi haƙuri har sai an samu daidaitawa da fahimtar juna. A samu kowa yana ƙaunar kowa.

Idan muka ɗauki hadisin Barira, zai nuna mana cewa Barira ita baiwa ce; da ita da mijin ta duka suna cikin bauta. To sai ya zama waɗanda suka mallaketa sun ɗora mata fansa ta bayar da uƙiya 9 ta fanshi kanta. Ta samu Nana Aisha, sai ta ce" zan taimaka miki kuma za ta saye ki, amma zan sharɗanta muku cewa wulaya tana hannu na." Sai ta gaya wa Annabi (SAW), sai ya ce "ki ʻyantata domin wulaya tana hannun wanda ya ba da ʻyanci." Wannan ƙissar tana da tsawo. Mun gutsurota ne in da ke da alaƙa da abin da muke Magana. To, bayan ta ʻyantata, shine aka ba ta zaɓi tsakanin zama da mijinta ko rabuwa da shi; sai ta ce ta zaɓi rabuwa da shi. Ta ce da zai bata duniya da abinda ke cikinta ba za ta ci gaba da zama da shi ba. A wani hadisin Abdullahi ɗan Abbas, Manzon Allah (SAW) ya ce "inama za ki koma wajen mijinki? Sai ta ce "Ya rasulallah umarni ne kake bani na dole in je in yi?" Ya ce "aʼa, ina nema masa alfarma ne." Ta ce to bani da buƙata da shi; ba na sonsa. Annabi (SAW) bai takura mata ta koma inda ba ta so ba sabda ya san cewa idan babu soyayya to zama yana da matsala. Tare da cewa shi mijin ya na tsananin sonta. Har yakan zo gaban Annabi yana kuka, yana zubar da hawaye, yana cewa a taimaka masa a je a yiwo masa bikon ta. Amma Annabi bai ce ta koma dole ba. Tare da ga tsananin so ta ɓangaren mijin ga tsananin ƙi ta ɓangaren matar. Ita ba ta so ko ʻmisƙala zarratin. Shi kuma yana so har zai iya mutuwa saboda ita. Ashe ka ga kenan dole ne a samu soyayya ko da na ɓangare ɗaya ya fi yawa, ya zama dai akwai son. Idan namijin baya son mata, ko matar ba ta son na namijin, ko duk su

biyun basa son juna, to abin da ya kamata a yi shine haƙuri. Kada a haɗa wannan auren da ƙarfin tsiya- saboda wai ko zumunta ko a ce za a haɗa 'ya'yan abokai.

Yanzu kawai wani sai ya gayawa abokin sa cewa ya "turo ɗanka ya ga 'yata" kuma ba a sharɗanta in yana so ba; ko ma ya ce ya bashi kawai. Ko kuma cikin dangi, ɗalibi yana karatu, a cikin danginsa, akwai wacce ba ta samu miji ba, kawai sai a zo a ce wai an bashi ita. Shi kuma bai taɓa zama sun tattauna wata magana ta soyayya ba. Saboda haka wannan yana daga cikin matsala. Akwai wani ɗalibi da ya taɓa bugo mini waya da ga wata ƙasa yana karatu a wata ƙasar a turai. Kawai nan kuma sai aka yi mishi waya cewa wai akwai wata a cikin danginsu an bashi ita. Ya ce duk karatun ya ƙi tafiya saboda duk lissafin da ya yi an ruguza masa. Ka ga ba daidai bane. A bar mutum ya zaɓa. Idan shi yake son wata a cikin danginsu, wacce ya halatta ya aura, wannan kuma su suka haɗa kan su. Amma iyaye ku daina cewa sai kun haɗa su ta ƙarfi. Da can an yi irin haka an sha, saboda wayewar ɗan Adam ba ta kai yanzu ba, abubuwan zamanin ba irin na yanzu ba. To amma yanzu dole mutum ya riƙa la'akari kada ya jefa zuriyarsa ko 'ya'yansa cikin wahala da ƙunci da damuwa. A ce mutum ya rayu fa, yana sonsa yana so shine kyakyawar rayuwa. Rayuwa ba wai yawan kuɗi ba ce, ko yawan ilimi ko yawan mulki da sarauta ba, a'a, ya zama zuciyar ka tana cikin nutsuwa. Idan ba a samu nutsuwar zuciya ba, ko me ka tara za ka ji ba ka jin daɗinsa. Don haka wajibi ne a riƙa ba ma'aurata dama suna fahimtar juna kafin a kai ga yin aure.

To idan an samu waɗannan abubuwan da duka muka faɗa, ka ga an samu tushe na cewa siffofin da aka faɗa game da miji sune da ya kamata a lura da su. Siffofin da aka faɗa game da mace ma sune ya kamata a lura da su.

To sai Magana akan zuwa zance. Yaya a ke bayyanawa mace ana son ta, ko yaya mace take bayyanawa namiji tana son sa? Ta wace hanya za a haɗu tsakanin ma'aurata, kuma ya ake zuwa zance? Abinda ake kira zance a larabci shine 'Khiɗba', shine Annabi (SAW) ya ke gaya mana cewa, kada mutum ya nemi aure akan neman auren ɗan uwansa. Neman aure shine ka shirya za ka yi auren. Ka duba ka ga cewa duk sharuɗɗan da ake nema ka cika su don ka aure ta. Kuma kamar yadda nake gayawa masu neman aure, su daina tsanantawa wajen sanya siffofi da sharuɗɗa da yawa. Wani ka ji ya ce hafizar Alƙur'ani, doguwa fara, to ka ga, ƙera maka za a yi? Kuma duk sanda ka samu mace mai irin waɗannan siffofin, itama za ka samu akwai masu son ta da yawa. Kuma ba dole ne kaima ka cika nata

siffofin ba. Yadda kake jin kana da sharaɗi, itama fa tana da sharaɗi. Kuma duk mutumnin da za ka ga yana faɗan irin waɗannan abubuwa, to z aka samu shi bashi da irin su. To ya kai da ba ka da abu kuma za ka ce ba za ka auri mace ba sai mai irin wannan? Duk da ana son surki ɗin amma dai dole mutum ya daina sa irin waɗannan sharuɗɗa masu wahala. Irin haka sai ya je ya yi ta neman aure bai samu ba. Ko kuma ya riƙa nema, sai ya nemi wacce ya san ta fi ƙarfinsa ta kowanne fanni, ta kowane ɓnangare.

To wajen neman aure ko hanyoyin haɗa aure guda 3 ne. Hanya ta farko mutum ya ga matar. Abinda ya kamata, ba ita ya kamata ya fara yiwa magana ba, iyayenta ya kamata a fara sana wa da cewa" na ga 'yar ku ina so. Idan ba a yi mata miji ba, ko idan an bani dama na shigo na nemi aurenta. To a nan idan ya tura wakilanta, su ka gayawa mahifin yarinyar, to shi kuma sai ya ce a ɗan bani dama. A ina yake? Sai a ce a wuri kaza. To shikenan a bamu dama za mu bincika. Idan mun ga ya dace, sai mu bashi dama ya zo su tsaya da ita. Sai uba ya kafa nasa kwamitin na a bincika, inda wannan mai so ya zo wajen 'yar sa zance ya ke. Idan ya gamsu da cewa ana iya bashi, sai ya bashi dama su zo su tattauna. Idan sun samu fahimta da ƙaunar juna, to shikenan sai su yi bayani, sai a shiga gaba a ɗau mataki na gaba. To wannan haka ya kamata a yi. Amma yanzu za ka ga 'yan matan ake fara yiwa magana. Kumama wani lokaci sai ka ga an bar yara suna fita zance da dare. Kowama sai ya zo yai sallama gidanka, 'yar ka ta fito. Ba ka san shi ba, baka taɓa ganinsa ba, baka san me ya kawo shi ba; aure ya kawo shi ko ba aure ne ya kawo shi ba? Ya cancanta ko bai cancanta ba? Da lokacin, da yanayin mutumin, da ita yarinyar, duk ba a yi su a kan dokoki ba. Bai kamata yarinya ta riƙa fita da dare ba, musamman a cikin lunguna da saƙo; wanda za ka ga daga magriba ta yi sawu ya ɗauke. Wani guraren ma ba fitila, a cikin duhu ne. To ka ga duk wannan ba daidai bane. Sannan kumama barin yarinya ta riƙa tsayawa da kowa shima ba daidai bane.

Hakanan kuma ma lokacin yin zancen shima bai kamata ma kabari kowa ya yi sallama a gidanka ba ka san shi ba kawai ya ce 'yar ka ta fito. 'Yar nan taka fa itace darajarka, itace ƙimarka. Duk abinda ta yi na kirki sai ya shafe ka. Duk abinda ta yi na tsiya sai an ce 'yar ka ce. To bai kamata ka barta kawai wani ya zo ya ce wai ana sallammma da wance kawai sai a ce tana zuwa ba. Kawai sai ka fito ka ga wani ya tsefe gashin kansa. Ya yi wata irin shiga, ya saɓule wando. Ya sha gilashi baƙi yana zazzare ido, wai yana cewa a yi sallama da 'yar ka. To ka ga wannan ya

kamata ka tura masa yayanta ko ƙaninta ya fara tattaunawa da shi. "To kai me ya kawo ka ƙofar gidan mu? Daga ina kake? To shikenan za mu yi bincike a kan ka. Idan mun gamsu da kai, sai ka dawo. To ka ga wannan shine abinda ya kamata iyaye su riƙa lura da shi. Idan ba haka ba, za a yi ta samun abubuwan kunya, takaici da kuma abinda bai dace ba.

Iyaye mata ma babban aikin su ne tunda sune suke shiryo yaran su turo su waje. Saboda haka idan mutum ya yi sallama, su ce a'a, mu 'ya'yanmu ba haka ake yi ba. Ku je ku yi masa bayani cewa, ya fara turo iyayensa ne tukuna su nema masa izini na cewa mun yarda ma ya zo ya yi sallama da ita. Amma yanzu wata uwar ma gani take idan ana yawan sallama da 'yarta to farin jini gare ta. Saboda haka sai ka ga samari har layi ake wajen zance. Ace ke wance ga ɗaya saurayin naki a can kan kwana, ta ce dan Allah bashi haƙuri in gama da wannan. Saboda haka idan an gama da wannan, sai a koma a yi azance da wancan, sai wani ma ya yi sallama da ita, sai a ce "kai wannan yarinya da farin jinni take." Ai dama lokacin da ka yi mata suna, malam wane ne ya yi raɗa suna, shi kuma an camfa shi, idan ya yiwa yaro suna to shikenan farin jini ya ke yi.

Saboda haka daganan an buɗewa yarinya ƙofa. Sai ka yi ta ganin ta da abubuwa; wani ya sai mata waya, wani ya sai mata kaza. Shikenan sai wani ya fara gayyatar ta zuwa taro,  ko a ce za su yi tafiya. Musamman ma, ni ina takaici, yarinya  ta cewa babarta "saurayina ya gayyace ni za mu je guri kaza." Ita kuma uwar sai ta ce, "to Allah ya kiyaye hanya, a dawo lafiya." Inafa za a dawo lafiya? Kin tura yarinya ta tafi inda baki sani ba, ko kin haɗata da mutumin da ba a san shi ba. Ko an san shin ma, wa ya ce a bashi 'yar mutane ya tafi da ita wani wuri, kuma har a ce a dawo lafiya? To ka ga ba daidai bane. saboda haka ya kamata, 'ya'yan mu darajarmu ne, mutuncinmu ne, ƙimarmu ne kuma sune gwalagwalanmu. Ya kamata mu san inda ya kamata su je.